[3/26, 9:55 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176 domin karin bayani, maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka fara amfani da maganin zaki ga sauyi, domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari 2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*105&106*

To shima nashi 'bangaran abinda yake faruwa kenan, domin tun bayan ya sauka gida yake kiran wayarta abun ya gagara, da ta fara shiga sai ta katse ya kira ya kai sau goma bai samu biyan bukata ba, sai kawai ya ajiye wayar ranshi gabadaya a 'bace yaso kafin ya kwanta yaji lafiyarta da ta babynsa dake kwance a cikinta, haka kawai yake tausaya mata, ya san duk wani abu da take daurewa take akan ta nuna masa kaunar 'yan uwansa, kuma abunda tayi ya siya mata kima da daraja a idonsa, ya sake jin sonta ya k'aru a zuciyarsa.

Da tunaninta ya kwana ya kuma tashi dashi, wannan dalilin ne yasa yana dawowa daga massalaci ya dauki wayarsa ya kunna, ya fara laluben number ta, cikin ikon Allah sai ta kira shi, a jiyar zuciya ya sauke mai sanyi kafin ya sanya wayar a kunnansa da sallama a bakinsa.

Ta amsa a sanyaye tana dan gyara kwanciyarta, yace." My GIMBIYA fatan kin tashi lafiya ya kwanan bakunta."?

Tace."Lafiya alhamdullihi na kwana da tunaninka da kewarka rashin kwanciya a kirjinka ya janyo min ciwon jiki."

Ya lumshe ido yana jin wani feeling na taso masa yace." Me yasa ki ka takura kanki lallai sai kin kwana umm? saboda na san hakan zai faru ya sa na sauya shawara, yanzu na gamsu da kaunar da kike a kaina da family na.

Sanyayyar ajiyar zuciya ta sauke kafin tace." Nifa ba'a takure nake ba, domin yanayin garin ya burgeni sosai da zamu dawo garin da zama da hakan yayi min dadi." Tafad'i hakane kawai ba har can cikin zuciyarta ba.

Aikuwa yaji dadin maganar yace." Tunda yanayin garin yayi miki dadi zamu dinga zuwa hutu

ko? zan gina miki gida mai kyau."

Tayi 'yar dariya da fadin." Naji dadin hakan mijina."

Yace." Ya babyna ina fatan yana lafiya."?

A shagwabe tace." Jiya tun bayan da kuka gaisa dashi ya dameni da k'iriniya  sai motsi yake min."

Dariya yasa da fadin." Yana bukatar mu sake gaisawa sosai dan jiya baki sakar min jiki mun gaisa yanda ya dace ba, amma ki bashi hakuri kafin mu had'u."

Itama dariyar take kafin tace." Aa ni babu ruwana idan kun had'u sai ka bashi hakuri dan da alama yayi fushi tun wayewar gari beyi motsi ba."

Gabansa ya fad'i!  da sauri yace." Beyi motsi ba fa ki kace."?

Ta dora hannunta a saman cikin tana shafawa kafin tace." Eh mana ya tattara a guri daya kamar bashi da lafiya."

Gabad'aya yaji hankalinsa ya dawo garin yace." Ganin tafe insha Allah."

Da sauri tace." Laa da wasa fa nake maka."?

Ya 'bata rai da fadin." ZINAT an ta'ba wasa da lafiya ashe.'?

Jin yanda yayi maganar babu wasa yasa ta zama serious  tace." Allah tsokanarka nake yanzu haka ma motsi yake yaji muryarka."

Ajiyar zuciya ya sauke da fadin." Saboda kin ga na damu shiyasa zaki mayar dani shashasha ko."?

Kunshe baki tayi tana danne dariyar dake kokarin subce mata, tace." Kayi hakuri Darling."

"Um-um! naki hakurin." Cikin shagawaba yayi maganar.........Tace." Dan Allah fa."

Yace." Nayi amma kada ki sake min wannan wasa hankali na ya tashi wallahi."

Tace." To ba zan sake ba insha Allah."

Yace." Uwale ta tashi."?  tace." Eh tana kicin tana aiki."

Yace." Idan babu damuwa ki kai mata wayar mu gaisa."

Tace." To insha Allah bari na kai mata."

Cikin jin dadi yace." Allah yayi miki albarka."

Ta amsa da "Ameen tana kokarin tashi tsaye.

****

Hamra'u da kanta ta shirya abincin ta zuba cikin kwanuka masu kyau ta jera kan tire kafin ta nufi bandaki a gurguje ta shiga wanka.

A lokacin ne mahaifiyarta Dayyiba ta samu damar aikata mugun nufin ta.

Ko kafin ma Hamra'un ta fito daga bandaki har ta sanya k'aramin   d'anta ya dauki tiran dake dauke da abincin sun fita a tare.

D'aya da rabi na rana Uwale na aiki a kicin  Dayyiba tayi sallama a gidan.

Uwale ta amsa ta fito daga kicin din tana mata barka da zuwa,  kai tsaye daki suka nufa.

Suka fara gaisawa tare da tambayar bayan rabuwa.....Dayyiba tace." Ai da wuri yau na gama abinci nace bari nazo mu gaisa na kuma ga matar Umaru kin san dama ni ban ta'ba ganinta ba."

Uwale tace." Allah sarki sannu da kokari Dayyiba har da wahala haka to mun gode sosai."

Tana murmushi tace." Babu komai Dambu ne na turara mata na san masu ciki da kwad'ayi watakila yayi mata dadi."

Tace." Eh 'kwarai kuwa, bacci takeyi yanzu amma bari na leka na gani ko ta tashi."

Lokacin da ta shiga dakin zaune ta sameta a bakin gado tun bayan shigowar Dayyibar ta tashi duk tana jin maganganunsu.

Tace." Ashe kin tashi  dama mahaifiyar Hamra'u ce tazo ku gaisa   ta kuma kawo miki abinci."

Tace."Allah sarki amma na gode sosai bari na fito mu gaisa."

Ta juya da fadin." To bari na sheda mata."

Shuru tayi tana nazarin al'amarin,  mahaifiyar Hamra'u?  ita sunan yarinyar ma bata kauna ballantana wanda ya danganceta.

Ajiyar zuciya ta sauke kafin ta tashi da k'yar! yunwa sai sasakar cikinta take,  abun goge baki ta dauko cikin kayanta.

Koda ta fito bata zauna ba tukkuna sai da ta wanko bakinta ta dauro alwala sannan ta dawo dakin.

A nutse ta zauna kusa da Uwale ta kalli Dayyibar dake mata wani munafikin kallo tace." Ina wuni fatan mun sameku lafiya."?

A firgice ta amsa da fadin." Lafiya lou muke ya mutan gida da can gurin manyan."

Tace." Duk suna nan lafiya lou."
Daga haka sai ta kawar da kanta tana nazari akan matar kamar mara gaskiya.

Uwale ta bud'e kwanunkan abincin da fadin." Dambu ne ko kina sha'awa."

Kamshi ya bugi hancinta  Dambun ya hadu yaji gyada da zogale ga k'amshin man gyada ziryan yana tashi...........Tunda take sau biyu kacal ta ta'ba cin irin wannan abincin, shima kuma irin na shinkafa bana masara ba ,  wannan dalilin yasa gabadaya ta rikice  yaron dake cikinta ya nuna kwadayinsa akan abincin   .

Ta kalli Dayyibar da fadin" Na gode sosai."

Tana washe baki ta amsa da babu komai dan nayi miki hidima kamar 'yar cikina kike."

Murmushi kawai tayi ta kalli Uwale da fadin." Nayi sha'awarsa.".

Uwale tasa dariya da fadin.'' Ai dole  ni kaina ya bani sha'awa ballanatana ke da kike da lalura."

Dayyiba ta dinga dariyar farin ciki  tace." Ai kin san Hamra'u ta gwane gurin iya abinci gargajiya

dama na turawan kowacce mace tana da baiwa,  amma tabbas duk macan da ta iya girki zata samu soyayyar mijinta.

Ba ita Zinat din ba har   Uwale sai da taji babu dadi da maganar Dayyibar dan kamar maganar tayi kama da habaici.

Babu dai wanda yayi magana a cikinsu,  ta zuba mata a ma daidaicin  plate.  tayi bisimillah ta fara ci a nutse ba ta tunanin komai a ranta.

 Sosai dambun yayi mata dad'i,  tas ta cinye wanda yake gabanta. a cikinta tana jin k'oshi amma a bakinta ba ta gaji ba, haka dai tayi kawaici tasha ruwa.Uwale ke tambayarta, tace." A yanzu dai ta koshi sai zuwa an jima tukkuna."

Dayyiba mahaifiyar Hamra'u zuciyarta fes!  ta fita gidan, babban burinta cikin ya zube ko kuma Gimbiyar ta galabaita.

Aikuwa dai jikinta ne ya mutu kasala ta dame ta, sai kawai taje ta kwanta tana ya mutse fuskarta cikinta ne yake hautsinawa zuciyarta na tashi.

Minti ashirin da kwanciyarta ta tashi a gigice! sakamakon jin wani irin mahaukacin amai da yake taso mata.

Bakin rariya ta gurfana ta dinga sheka aman tana rike kirji!

Uwale hankalinta ya tashi ganin mawuyacin halin da Gimbiyar ke ciki.

Ta rike ta tana mata sannu a lokacin kanta ya dinga juyawa tayi kwance a gurin tana mayar da numfashi.

Uwale tace." Sannu ki daure ki tashi ki koma daki ki kwanta a can kinga nan akwai rana gaki a bakin kwata a kwance."

Shuru tayi ba ta iya cewa komai ba, gabadaya ma bata cikin hayyacinta,  tana jin yanda cikinta yake kartawa! wannan karan ba amai takeji ba zawo!  ne mai karfi yake kokarin kwace mata.

Kokarin tashi take domin shiga bandaki abun ya gagara domin gabadaya jikinta ya shika babu kwari!  duk yanda taso da ta daure ta kasa ba ta ma san lokacin da zawon ya kwace mata ba, kawai sai tsuuuuuu!  ta dinga jin fitarsa kamar an kwance famfo.

Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un!  shine abinda Uwale take nanatawa.

(Cutar a mai da gudawa!)  ya kama 'yar mutane! cutar dake saurin halaka mutum,  hankali a tashe ta nufi gidan Tasallah.

Suka shigo tare  lokacin gudawar sai bin rariya take ita kuma tana kwance a gurin sai matagugu take domin wani masifaffan ciwo cikinta yake mata.

Tasallah tayi salati tana sanar da Ubangiji kafin tayi azamar fita, gidanta ta koma  da yake akwai magungunan gargajiya da take aje dasu,  ta daga karkashin gadon karfenta ta dauko ledar maganar duk tayi kura da dauda!   da yanar gizagizo ajikin ledar ta dauka ta fita.

Aje ledar tayi a gefe ta taimakawa Uwalen suka fara gyarata,  idonta a lumshe yake amma duk tana jin taretaran da suke da ita, ta riga ta mika wuya yanda take jin jiki bata tsammanin zata rayu.

Jikinta  suka wanke mata lokacin anyi sa'a Gudawar ta tsaigata da zuba.

Uwale tayi saurin dauko mata wasu kayan da wando da rigar nono suka sanya mata jikinta mikar da ita sukayi kafafunta suka dinga kyarma!  a daddafe suka shiga da ita daki.

Uwale ce ta shiga gyara gurin,  ita kuma Tasallah sai da ta tsaftace hannuwanta, sannan ta kwance ledar maganin data dauko ta fito dasu a daddaure! daka gani sun jima a ajiye,  wuta ta hura  kafin ta  wanke maganin tas ta zuba  a tukunya tasa jar kanwa  sannan ta d'ora a wuta.

Sai da ya tafasa sosai sannan ta sauke domin yasha iska.

To cikin ikon Allah da hukuncinsa  tana shan wannan magani ta samu sassauci ciwon  cikin da yake damunta yayi sauki  baccin wahala ya d'auketa.

Uwale ta kalli Tasallah da fadin." Sai yanzu hankalina ya kwanta Tasallah al'amarin nan ya tsorata ni mutuka."

Tace." Dole ne, ni kaina ganin yarinyar a galabaice sai da na firgita kasancewar na san cewa wannan cutar na saurin halaka mutum! Allah yasa akwai ajiyayyun magunguna kinga cikin ikon Allah sunyi amfani "

Ta sauke ajiyar zuciya da fadin." Tasallah nifa ina zargin Dayyiba."

Shuru tayi tana kallonta da mamakin maganarta.

Tace." Tun bayan da yarinyar nan taci Dambun da Dayyibar ta kawo mata shikkenan ta rikice shiyasa nake zargin ko da abunda tayi.

Tace." Uwale zato zunubi aka ce koda ya kasance gaskiya ne, ni kuma nafi tunanin ko sauyin cima ne da ruwan sha, kin san hakan na iya janyo faruwar mummunar matsala.

Tace." Idan hakane me yasa jiya da taci abincina ta kwana lafiya? ruwa kuma ba irin wannan muke sha yarinyar take sha ba, kafin mijinta ya tafi sai da ya siya mata ruwan roba gashi can a daki kwali guda. gaskiya ina zargin Dayyiba.

Tasallah tayi murmushi da fadin." Hakan na iya faruwa amma kada kiyi gaggawar yanke hukunci tukkuna.

Shigowar Hamra'u ne ya katse maganar, babu wanda ya nuna mata wani abu a fuska, ta zauna suka gaisa, kafin ta kalli Uwale da fadin." Ummana ta kawo miki Dambu ko."?

Tace." Eh ta kawowa dai Gimbiya."

Ta dan 'bata rai da fadin." Ai naki ne kasancewar na san kina son Dambun masara yasa na tashi da wuri nayi miki, ko kafin na fito daga wanka na samu Ummana bata gidan wai ashe anan tazo."

Tace." To Na gode sosai Allah yayi miki albarka."

Tasallah na 'yar dariya tace." Hamra'u kenan to menene dan kishiyarki taci ai abun burgewa ne "

Zumbura bakinta tayi tana ya mutse fuska.......Dukkaninsu babu wanda yaji dadin abinda tayi, kiri-kiri take nuna kishinta a fili.

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing, idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar

gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:55 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176 domin karin bayani, maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka fara amfani da maganin zaki ga sauyi, domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari 2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*109&110*
Gidan ya rage saura ita kadai, sai ta shiga tunanin abubuwan da suke faruwa, jiya da daddare kafin su kwanta Uwale tayi mata cikakken bayanin abunda yake tsakanin mijinta da yarinyar da tuntuni ta d'ora zargi a kanta, tabbas koda Uwale ba tayi mata bayanin komai ba dama tuntuni ta fahimci wani abu, duk da dai shi bai fad'a mata cewa akwai al'kawarin aure a tsakaninsa da yarinyar ba, to ita yarinyar ta nuna mata alamu tun farkon fara had'uwarsu...Ba zata ha nashi aure ba, domin a yanda Uwalen ke sheda mata yanda yarinyar tayi wahala a kansa hakan ya sanya taji tausayinta, bayan haka kuma ta san duk daran dadewa bai zama lallai ta zauna ita kadai ba, wannan ne dalilin da yasa ta tausayawa yarinar. wai akace son maso wani koshin wagala! amma babu shakka ba zata lamunci munafurci da kumbiya-kumbiya ba. domin tafiso duk abinda za'ayi a fada mata kada a munafurce ta, abu na karshe kuwa dole ya jawa yarinyar kunne ta kiyayi shiga gonarta ko kuma yi mata rashin kunya anan ne za'a samu matsala! domin mutukar yarinyar tace zata raina mata hankali to abu ne mai sauki a gurinta ta cire blet ta zane mata jiki dashi, sai dai duk abunda zai faru ya faru.

To can gidan biki kuwa ya kacame! da hayaniya mata sun fi ashirin akan Uwale dake rabon turaman atamfofi da mayafai da sabulai na wanka da wanki.

Da yawa wasu basu samu zanin ba, saboda yawansu, wasu kuma mayafai suka samu da sabulai, duk wanda ta mik'awa sai tayi masa bayani cewa daga matar Umaru ne.

A cikin wa'inda suka samu kayan har da mutanan Dayyiba......sai suka silale suka nufi gidanta domin kai mata rahoto.

Wasu kuwa gidan Uwalen suka nufa domin mika godiyarsu da kuma jin dadin alkairin da akayi

musu.

Hayaniyar shigowarsu gidan ya katse tunanin da take.

Ta fito tsakar gidan ta gan su da yawa a tsaye....ikon Allah har da masu durkusa mata,  ta jingina jikin bango (garu) tana amsa gaisuwarsu da fadin." Ku daina godiya haka babu komai an zama daya.

D'aya daga cikinsu tace." Dole muyi godiya yarinyar kirki! domin bamu tsammaci haka daga gurinki ba, dalili mun samu labari a bakin wasu daga cikin 'yan uwanmu cewa baki da kirki mutuniyar banza ce ke da dai sauransu, sai gashi kinyi mana bazata mun gode sosai."

Murmushi kawai tayi kafin tace." Ba komai kun san mutum tara yake bai cika cif ba, kowa yana kuskure a rayuwa, wa'inda na 'batawa rai a cikinku su yafe min tunda har Allah yasa na shiga cikinku ai mun zama daya dama rashin sabo da juna ne."

Matar tace." Kwarai kuwa Gimbiya to mu dai  muna bayanki insha Allah domin dai Dayyiba bata da alkibula mai kyau! mu mutanan *KAFUR* muna sonki da kaunarki dan haka ki cire kokwanto a ranki."

Tace." To na gode sosai Allah ya saka da alkairi."

Gabadaya suka amsa da ameen. kafin suyi mata sallama su fita....Itama cike da farin ciki da jin dadi ta koma dakin ta kwanta, cikin zuciyarta take adduar Allah ya bata hakurin zama dasu, tunda tana son mijinta babu abinda ba za tayi ba.

Dayyiba da labari ya iske ta kamar ta kurma ihu saboda bakin ciki, idonta ya ciko da ruwan hawayen bakin ciki ta kalli Taburni da fadin." Amma dai kinji kunya wallahi Ashe amincin da yake tsakaninmu na 'karya ne."?

Taburni tace." Kamar yaya ban gane ba."?

Ta zabga mata harara da fadin.'' Meye amfanin zuwa ki kar'bi turmin atamafa kamar baki ta'ba daura zani ba."

Ta daga mata hannu da fadin." Kinga Dayyiba saurara!  kawai saboda gudun bacin ranki ina kallon alkairi sai na bar shi, kema kin san ba zai yuwu ba, zani da sabulai na samu  ke ko dake ko babu ke dole ina da rabo saboda matar Kawunsa ce to meye abin damuwa."

Dayyiba ta sanya gefan zani ta share guntun hawayen daya fara fitowa  tace." Taburni ban san ya zanyi ba akan wannan al'amari, wallahi idan Hamra'u ta samu shiga gidan Umaru buri na bai wuce ace ta zama mowa ba, amma na san hakan ba zai yuwu ba sai na taka muhimiyyar rawa. gashi bani da kudi a hannuna ballanatana naje a taimaka min."

Tace." Yanzu dai abu na farko da za fara shine janyo hankalinsa kan 'yarki,  ma'ana ya daina ganin kowa a gabansa sai ita, kafin ace ta shiga gidansa, sai kuma ayi musu farraku da Uwargidansa.

Tace." Taburni bani da kudi wallahi, kuma kin san wannan harkar sai an ajiye kudi dole a zubar da jini."

Taja tsaki da fadin." Ashe wasa ki ka dauki al'amarin, ai idan zakiyi yawo tsirara ba abun damuwa bane mutu'kar bukatarki zata biya, ki sayar da gado da katifarki ai ba'a kanki aka fara ba.

Tayi shuru tana nazarin maganar,  tabbas hakan shine mafita domin idan ta tsaya kallon ruwa to kwado ne zai yi mata 'kafa  gwara ta tashi a tsaye.

Uwale ta kawo mata gurasa *(band'asho)😃* Kanawa mune gurasa Allah yasa akwai wa'inda suka san meye ma'anar *(Band'asho)*  Taji  k'uli da man gyada mai kamshi gefe da kabeji da sauran kayan had'i, sosai taji dadi gurasar  taci ta k'oshi  kafin tayi wanka ta shirya jikinta cikin wani milk din les mai taushi da stones a jikinsa, sai ta dora alkyabba mai tafe da hula a jikinta, ta sanya takalmi rufaffan takalmi irin nasarauta, sosai tayi kyau, kamshi turaranta duk ya cika gidan.

Waje ta fito da wayar ta a hannunta.......ido yayi caaa! a kanta,  itama kallonsu takeyi sunyi rukuni-rukuni a gindin bishiya suna ta cin abinci babu kimtsi balle kamun kai.

Can gefe kuma amaryar ce da k'awayenta da ango da abokansa  sun sanya katuwar redio a tsakiyarsu kalangu sai tashi yake amarya da ango suna rawa  ana lika musu 'yan biyar-biyar.

Abin ya burgeta ya bata dariya kai tsaye gurun ta nufa cikin yanayin tafiyarta.

Hamra'u tare da Zabbah dake can nesa suka hangeta tawagar 'yan matan garin sun rufeta a lokacin da take tsakiyar amarya da ango tana manna musu 'yan dari biyar-biyar.......Ihu!!! da kaya-kaya ya cika gurun!

Takaici ya hana Hamr'au karasawa gurin, ta juya a sukwane ta koma gida.....Ita kuwa Zabbah! sai da ta k'arasa gurin, ta kutsa ta samu rabonta dan sai da ta tsira da dubu biyu.

Da wayarta ta dinga yi musu vedio sai hauka suke suna he da he kowa so yake tayi hoto dashi, amarya da ango kuwa kamar su zuba ruwa a kasa su sha a tarihi ba a ta'ba biki irin nasu ba.

Hamra'u ta 'karaso gurin tana wani dauke kai! ita gata wacce ta fita zakkah a cikinsu, da ba a san asalin balbela ba sai ace daga masar tazo .......Ta zuge jakar hannunta ta fito da kudi 'yan dari -dari ta fara watsawa a gurin.........Wani abokin ango yayi saurin sanya wakar *Komai na Babah yafi na yaro!* Zinat kuwa ganin haukan da yarinyar take ya sanya tayi gaggawar fita daga gurin.

Ita kuwa Hamra'u sai wani jin kai take tana wani ya mutse fuska! Zabbah taja ta gefe da fadin." Wannan wa'kar fa da Salmanu yasa dake yake, kinzo kina lika dari-dari ita kishiyar taki dari biyar biyar ta dinga watsawa kuma ta watsa yafi dubu ashirin kinga nima na samu dubu biyu. amma ke kina lika 'yan dari -dari sai wani jin kai kike."

Jikinta yayi sanyi ta kalleta da fadin." Kina nufin dama saboda naji haushi Salmanu yasa wannan wa'kar!

Ta fashe da dariya da fadin." E mana ma'ana kiji haushi kema ki watsa musu kudi."

Ta girgiza kai da fadin.' Lallai Salmanu bashi da mutunci."

Tace." Hamra'u ni dai shawarar da zan baki shine kiyi hakuri ki kwantar da kanki ku zauna lafiya, dan na fahimci matar nan kamar tana da saukin kai kuma ba zaki samu matsala da ita ba, sannan kuma a zahiri ta fiki ta ko'ina kada kice zakiyi gasa da ita."

Tace." Idan na fahimce ki kina so kice na zauna nayi mata bauta ko."?

Ta girgiza kai da fadin " Aa ba haka nake nufi ba, ina nufin ki dai daina kishi a kanta dan naga kin zafafa da yawa, baki da gashin wance dole ki zauna a matsayinki."

Ta girgiza kai da fadin." Ba zai yuwu ba Zabbah shekara sama da goma ina dauki ba dadi akan biyan bu'kata na amma lokaci guda wata ta shiga rayuwata, wallahi ba zan iya daina kishi a kanta ba, domin bana kaunarta na tsaneta! kuma zan iya komai akan ganin bayanta."

Zabbah ta dinga yi mata kallon mara hankali da tunani! itafa gabadaya rayuwar yanzu ta zama

wayo da dubara da kuma siyasa mutukar ka iya wannan zaka zauna lafiya, amma shikkenan tunda tayi iya bakin kokari gurin ganin ta nusar da ita ta kasa fahimta zata kyaleta kawai taje duk abinda za tayi rayuwarta ce.

Shida shaura ya sauka a garin.......Tun kafin ya fito a mota gurin ya hautsine! hayaniya da ifece-iface! tare da haushin karnuka!

Saboda ba ta san ganin bacin rai yasa tayi gaggawar shiga gida, ta san mybe sai ya tsaya yayi abinda ya saba.

Sai dai kuma bata jima da shiga gidan ba ya shigo cikin inform da alama daga gurin aiki yake.

Koda ya shiga gidan hankalinsa gabadaya yana kanta....ya rungumeta yana ta sumbutar fuskarta. A lokacin su Uwale suka shigo gidan.

Uwale Hamra'u da Zabbah dake bayansu......Gabadaya jikin su ne yayi sanyi ganin irin soyayyar da ake zabgawa a gurin, kamar zai cinyeta ya rike fuskarta sai so yake ya kama bakinta tana kaucewa.

Gilmawar Uwale a gurin ita ta hankaltar dashi, ya sakar mata fuska yana sauke wani irin numfashi.....Juyawar da zai yi yayi ido hudu da Hamra'u dake tsaye kamar wacce aka dasa, gwiwarta tayi bala'in sanyi!

Ya d'an ji kunyarta amma da yake namijin duniya ne sai ya basar yace." Kanwata ina fata dai kin shirya kin kuma yi sallama don yau zamu tafi."

Murya na rawa tace." Ni ba zan koma ba."

Ya kalleta da mamakin furucinta a tare dashi yace." Saboda me."?

Ba tace komai ba, kawai ta juya ta fita kawarta ta rufa mata baya.

Ajiyar zuciya ya sauke yana mamakin al'amarin.

Ya dan juya in da take, wayam babu ita a gurin......bai kawo komai a ransa ba, ya cire takalman dake kafarsa ya shiga dakin da sallama a bakinsa.

Gabadaya suna uwar dakin ita da Uwalen.

Kusa da ita ya zauna yana d'an satar kallonta a idonsa ya hango rama a tare da ita kwana uku kacal ta sauya masa tayi haske sannan duk ta rame.

Uwale dake had'a kaya tace." Naji kuna magana da Hamra'u ko."

Yace." Eh wai me yake faruwa ne?

Murmushi takaici tayi kafin tace." Alkairi ne, amma tunda tace ba zata koma ba, sai ka kyaleta a ranar da aka daura  muku aure ai dole ta zauna a dakinta."

Gabansa ya fadi da jin maganar da Uwalen tayi zata tona masa asiri! be shirya sanar mata da maganar yanzu ba,  ya saci kallon fuskarta yaga babu abunda  ya sauya a yanayin ta wayarta ma take dubawa.

Ajiyar zuciya ya sauke cikin zuciyarsa yake addua Allah yasa ba taji maganar ba, duk da ya san da kamar wuya hakan dan kyau Uwale ta fadi maganar.

Ya kalli agogon dake d'aure a hannunsa  shida da rabi har an fara kiran sallar magriba, yace." Zan je nayi sallah mu gaisa da wanda ya dace kafin na dawo sai ku shirya."

Tace." Ai mu a shirye muke Umaru sallah kawai za muyi.

Yace." Uwale anya ba wani abu ne ya faru ba kuwa."?

Tace." Me ka gani kake wannan maganar.''?

Yace." Naga kamar kina Allah-Allah mu bar garin bayan kinyi alkawari cewa sai kinyi sati uku ko hudu."

Shuru  kawai tayi ba tace masa komai ba.  Ya girgiza kai tare da mikewa tsaye. bahaushe yace shuru ma magana ce, lallai akwai abinda ya faru bayan barin sa garin.

Uwale na idar da sallah ta kalleta da fadin.'' Kafin Umaru ya shigo zan dan shiga muyi sallama mutane."

Tace."To shikkean ba komai idan ya shigo zan sheda masa.

Fitar ta keda wuya ya shigo gidan, yana haska dakin da wayar hannnsa, kan dadduma ya sameta, ta idar da sallah amma bata tashi ba.

Ya zauna saman gadon karfen dake dakin yana kallonta.

Babu yabo babu fallasa ta juyo suka had'a ido taga yana mata wani irin kallo kafin yace." Zo nan ki fada min abinda ya faru bayan tafiya ta."

Ta iske in da yake ya rike  hannunta tare da zaunar da ita kusa dashi, gabadaya hankalinsa yana kanta, yana jiran abinda za tace.

Tace." Kai me kake tunanin zai faru."?  Shuru yayi be san me zai ce ba kawai yana ji a jikinsa ne."

Tace." Kamar yanda Uwale ta fada maka alheri ne hakane, Allah ya sanya alkairi a tsakaninku."

Ya rasa gane abinda take nufi......Ganin yana kallonta yasa tace." Ya aiki ina mutuminka Asp ina fatan kuna lafiya."?

Hannunta ya rike da fadin." Asp yana nan lafiya har ya bani sakon gaisuwarki amma da ba kiyi maganarsa ba na manta, sai kuma ni da nake cikin matsala."

Tace." Matsala kuma."?

Kai ya daga mata kamar karamin yaro.

Ta zuba masa ido tana kallonsa.

Hannunta dake cikin nasa ya fara kokarin cusawa k'asan mararshi.......Tsigar jikinta ta tashi da sauri ta fizge hannun tana harararsa.

Ido jawur!  yake kallonta, kafin yace." Kin gane matsalar ko."?

Tace." Kai kam baka da matsala sai wannan."?

Yace." Ina dasu amma wannan itace a kan gaba."

Ta'be bakinta kawai tayi ta d'auke kanta.

Duk ya rasa yanda zai yi baya so tana sha masa k'amshi!  tabbas ya san da akwai wani abu a kasa.

Ganin abinda take yasa ya kama kansa, yayi kokarin danne kwad'ayinsa, saisaita muryarsa yayi kafin yace." Ina Uwale take ne."?

Ba tare da ta kalleshi ba tace."  Ta fita domin yin sallama da mutane."

Ya mike ba tare da yace mata komai ba ya kama hanyar fita,  kallo ta bishi dashi  tana girgiza kanta.

Bata yarda ta zauna kusa dashi ba,  a kusa da Uwale tayi zamanta suna hira, shi kuwa kamar maraya suka mayar dashi direba haushin hakan ya sanya bai sa musu baki a maganarsu ba, sai dai sa'i da lokaci yana amsa waya jefi-jefi!   a haka suka isa gidan kowa da abunda ya dameshi.

A maimakon ya nufi side dinshi kawai sai ya bita nata,  ta riga ta san bin diddigin da yake mata, haka kawai ta tsinci kanta da jin haushinsa.

A nan yayi wanka ya kimtsa ya fita ya siyo musu abinci, sai da ya kaiwa Uwale nata sannan yayi mata bankwana, koda ya fito kai tsaye sashen Gimbiyar ya nufa babu wani kuzarin kirki a tare dashi.

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing,  idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:55 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176  domin karin bayani,  maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu

cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka fara amfani da maganin zaki ga sauyi, domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari 2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*111&112*

A kwance ya sameta bacci na shirin d'aukarta, ya zauna kusa da ita da fadin." Ki tashi ga abinci na san akwai yunwa a tare dake."

Ta d'an muskuta da niyyar gyara kwanciyarta a ta'kaice tace." Bana jin yunwa."

Yayi kasa'ke yana kallonta kafin yace." Ban yarda ba kwayar idonki ta tabbatar min da cewa akwai abinda ke damunki ko bayan haka ma ai ba ke kadai ce kike rayuwa ba, akwai wanda yake bukatar kici abinci shima ya samu rabonsa.

Shuru kawai tayi masa ba ta da niyyar tashi ballanatana taci abincin.

Ya 'bata ransa da fadin." Na lura kina so mu sanya kafar wando guda, me yasa ki ke min haka ne? ko dan kin ga na damu dake."

Uffan ba tace masa ba, asali ma idonta yana rufe sama-sama take jin sa.

Cikin zafin zuciya ya janye bargon dake rufe a jikinta murya a sama ya kira sunanta "Zinatu."

Ta bude ido tana kallonsa fuskarta babu fara'a ko kadan.

Yace." Na gaji da wasa da hankalin da kike min ki fito fili kiyi min bayanin dalilin da yasa kike wannan abun ai ba haka muka rabu ba da juna ba.

Zaune ta mike tana kallonsa duk ya wani firgice! har gumi yake kamar babu Ac a dakin.

Zum'bura baki tayi ba tace komai ba ta fara kokarin komawa ta kwanta, da sauri ya rike kafadarta ya hana ta kwanciyar in ban da rawa babu abunda jikinsa keyi, da alama baya son b'acin ranta.

"Kina so ki jefa ni cikin damuwa ko? shin ko dai wani abu 'yan uwana sukayi miki wanda kike hukuntani dashi."

Ta kalleshi tare da girgiza kanta kafin tace." Ko daya ni 'yan uwanka ba suyi min komai ba sai alkairi saboda haka ba wannan ce matsala ta ba."

Da sauri yace." Menene matsalarki ki fada min zanyi miki magani."

Cikin ranta ta ayyana wani abu, ta kalleshi ba tare da ta auna maganar ba tace." Ka janye maganar auran Hamra'u."

Ya tsira mata idanuwansa da suke a rikice!  alamun rashin gaskiya ya bayyana a tare dashi, yace." Wacece Hamra'u."?

Kallon mamaki take masa "Wacece Hamra'u."? wai tambayarta yake saboda ya raina mata hankali.

Ganin tana masa kallon zargi yasa ya daburce kafin yace." Waye ya fad'a miki zan aure ta da har kike wannan maganar."?

Tsaki taja kafin tace." Ba ka da gaskiya wallahi kuma ban san cewa kai munafiki bane sai yau wato har ni kake tambaya wacece Hamra'u? yarinyar da kowa ya sanka da ita a gari shine zaka raina min hankali.

Maganganunta sun 'bata masa rai mutuka!  ya fusata! tare da nuna ta da hannu "Kin ga saurara kada kiyi min rashin kunya ni kike kira da munafiki."?

Tace."  Kana nad'e tabarmar kunya da hauka meye dan ka fada min dalilin zuwanka garin cewa maganar auranka  zaku tattauna har ka bada sadaki kun tsayar da magana to sai me don  kayi aure ko ka d'auka zan damu kaina a kan hakan namijin da ake so shi ake kishi a kansa."

Yaji wani mugun bakin ciki da jin kausasan kalamanta!  ya dinga fesar da wani irin huci!  yana kallonta idonsa yayi jajawur! magana daya da tayi itace take sa hankakinsa ya tashi,  (Namijin da ake so shi ake kishi a kansa)  wato wannan yana nuna masa cewar duk abinda zai yi yaje yayi bata sonsa.

Ya tashi ya fita ya bar mata dakin domin zamansa zai iya haifar da kowace irin matsala mara kyau.

Ba ta wani damu da yanayin da ya shiga ba, bacci tayi sosai babu wata damuwa a tare da ita, ta riga ta san duk abinda yake raragefe ne da kame-kame.

Washe gari bai saurareta ba ya shirya ya fita da tarin bacin rai a tare dashi. Wanda har sai da abokinsa ya fahimci cewa yana da damuwa domin kallo daya yayi masa ya sheda hakan, abota ce ta gaskiya wannan dalilin yasa dukkaninsu suka fahimci junansu.

Ya kalleshi da fadin." UMARU kana da damuwa domin na ganta a cikin idanuwanka."

Ajiyar zuciya ya sauke ya kalleshi da fadin." Zinatu ce damuwa ta Asp yarinyar nan idan ta burkice na kan rasa gane kanta."

Asp din yace." Wani abu ne ya faru."?

Yace." Ta samu labarin tabbatuwar aurena da Hamra'u shikkenan take fushi jiya da k'yar na rintsa wallahi."

Yace." Sai hakuri, amma dole ka fuskanci wannan matsalar, kai dai kawai kabi hanyoyi masu kyau da zaka rarrasheta mussaman yanzu da take da juna biyu dole sai an bi komai sannu a hankali."

Yace." Kana nufin nayi ta bin kanta ta nayi min yanda takeso, bana tsammanin yin hakan."

Yace." Aa ba haka nake nufi ba abinda nakeso ka fahinta shine kada ta dauki zafi kaima ka dauka, ka kai zuciyarka nesa ka rarrasheta kada ka biye mata idan ka kwantar da kai ina mai tabbatar maka da cewa fushin ba zai yi nisa ba."

Shuru kawai yayi yana nazarin maganar.......Wani sa'in shi kansa mamakin kansa yake idan yana wani abu akan yarinyar ya rasa dalilin da ya sanya yake gudun bacin ranta, amma baya so ya sakankance ta gane lagonshi ta raina shi. shi yasa wasu lokutan yake mata jan ido.

Da tarin yunwa da damuwa ya isa gidan. jiri da ciwon kai sun addaba masa! kai tsaye gurin Uwale ya nufa ya samu abinci yaci ya kwanta yana hutawa.

Uwalen da kanta ta fuskanci bashi da lafiya....Tace." Ai ba kwanciya ya dace kayi ba asibiti za kaje a dubaka shine abinda ya dace."

Idonsa a rufe yace." Kada ki damu ina so na huta tukkuna muna da likitoci na mussaman zan kira daya daga ciki ya dubani."

Tace." To hakan shine dai-dai ai matar taka ma ai ta jima anan muna hira sai bayan la'asar ta shiga gurinta.

Ya sauke ajiyar zuciya da fadin." Uwale me yasa kika shedawa yarinyar nan abunda yake faruwa."?

Tace." Me yasa ba zan sheda mata ba Umaru ko kafiso mu tafi a haka ta samu labari a duniya tayi mana kallon mutanan banza."

Yace." Ba nufina kenan ba, nafiso duk abinda zai faru a bari ta haihu tukkuna kinga tun bayan dawowarmu babu kwanciyar hankali, na san kuma dalilin jin wannan maganar ne."

Tace." Umaru dole ne fa kayi hakuri da duk abunda zai biyo baya domin lusarin namiji baya ta'ba iya zama da mace biyu uku ko hudu, ka zama jarumi jajurtacce! akan duk abinda zai faru, bayan haka kuma ya zama dole ka jawa Hamra'u kunne ta kiyaye ta kuma sauya munanan d'abi'un da take yi kishi ai ba hauka bane."

Ya kalleta da fadin." Me tayi Hamr'un."? Girgiza kanta tayi da fadin." Aa ni ba zan fada maka komai ba, amma lallai ka ja mata kunne akan abubuwan da take aikatawa."

Ransa ya 'baci! idan ya fahimci maganar wato Hamra'u ta samu hanyar cin mutuncin matarsa saboda tana da tabbacin cewa ta kusa zama dai-dai da ita, wannan shine tunanin da yake, Hamra'u taki dawowa saboda akwai wani abu da tasan ta aikata na rashin kyautawa.
sosai yayi mamakin al'amarin beyi tsammanin cewa zai samu matsala da yarinyar ba, saboda yana da tabbacin nutsuwa da hankalinta.

Sai wajejan goma da wani abu ya shiga gurinta, lokacin ma ita har taci abinci tayi shirin kwanciya ba ta dai kwanta ba wayarta take dubawa.

Yayi sallama ya shiga dakin kamar mara laka a jikinsa.

Babu yabo babu fallasa ta amsa tana kallonsa har ya zauna kusa da ita.......Tace." Sannu ka dawo lafiya."?

Wani sanyi ya sauka a zuciyarsa, sam bai tsammaci haka da gurinta ba.

Da kwarin gwiwa yace." Lafiya ya kika wuni ya babyna."?

Tayi shuru ba tace komai ba.

Ya sake matsawa jikinta   yana nanik'arta. ba tace komai ba, amma gabadaya tsigar jikinta ta tashi jinsa a kusa da ita yana nema ya haifar mata da matsala.

Ya sassauta murya da fadin." My love ki kalleni za muyi magana ta fahimta."

Ta jim na minti biyu kafin ta kalleshi.  ya dinga sarrafa kwayoyin idonsa a kanta, gabadaya jikinta ya mutu, dama abinda ya keso kenan.

Ya sauke sanyayyar ajiyar zuciya kafin ya lalubi hannunta ya rike cikin nashi, a hankali yace." Hamra'u bake taci mutunci ba, ni taciwa mutunci kuma dole na nuna mata muhimmancinki kiyi hakuri kinji ko."

Murmushin takaici tayi kafin tace." Waye yace maka Hamra'u taci mutunci na."?

Yace." Uwale ta sheda min abinda ya faru a tsakaninku kuma raina ya 'baci sosai wannan dalilin yasa na yanke shawarar kiran wayarta a gabana ta baki hakuri."

Ta kalleshi tana so ta gazgata maganarsa,  kamar gaske dai gashi nan yana mata dadin baki.

Ya fito da wayarsa ya nemi number Hamra'un.....cikin ikon Allah wayar ta shiga ba'a samu matsalar network ba.

Bai wani saki fuska ba ya amsa gaisuwarta kafin ya dora da fadin."  Hamra'u abinda ki kayi ban ji dadi ba, kuma ba Gimbiya ki ka tozarta ba ni Umaru ki ka wulakanta  sanin kanki ne cewa mutanan garin *Kafur!* muna da karrama bako da mutuntashi me zai sanya ki wulakanta min mata saboda kin ganta a mahaifarki."

Murya na rawa ta fara rantse-rantse da fadin." Ya saurara tayi masa bayani.....'Kin sauraranta yayi yace." Mutukar kina so mu shirya da juna dole ki bata hakuri akan abinda ki kai mata wannan ne kadai zai sanya na saurareki.

Sai kawai ta fashe da kuka da fadin." Wallahi ni  ba zan bata hakuri ba,  kuma duk wanda ya fada maka cewa na tozarta ta Allah ya isa tsakanina dashi, ka tambayi Uwale itama idan zata fad'i gaskiya ai a gabanta komai ya faru!  sau biyu tana gaura min mari! a fuskata  amma saboda son zuciya za'a ce na bata hakuri!  ni kam duk abunda za'ayi sai dai ayi ba zan bata hakuri ba."

Yace." Ashe baki da mutunci dama."? Shuru  gabanta sai bugawa yake!  yace." Okey shikkenan tunda haka ki ka za'ba zan baki mamaki."  sai kawai ya kashe wayarsa yana jan tsaki!

Ta kalleshi da fadin." Nifa idan saboda ka faranta min rai kake wannan abun to ka daina,  domin hakan ba burge ni kayi ba...........koda yarinyar nan tayi min laifi na hukuntata tuntuni ka dai ja mata kunne ta kiyaye! idan kuma taki za fuskanci b'acin rai."

Yace." Akan hakan zan iya janye auranta sai me."?

Tace." Duniya za tayi Alla wadai dakai! wane irin hallaci ne yarinyar ba tayi maka ba, ai samun nutsuwarka ka aureta, ni bani da matsala  domin ban san abinda Allah ya rufe a tsakaninku ba."

Yace." A da can baya ina sha'awar auranta saboda kyawawan halayenta amma yanzu duk ta fice min rai saboda d'abi'un data sauya,  bayan haka kuma mutukar ba zata zauna lafiya dake ba, to kamar yanda na fada a farko zan iya janye auranta."

'Yar dariya tayi tare da girgiza kanta tace." To Allah ya rufa asiri ya tabbatar da alkairi  ni dai duk wanda ya nufe ni da sharri kansa zai koma."
daga wannan maganar ba ta sake cewa uffan ba, ta shige cikin bargo  tana gyara lulluba,   tashi yayi ya fita, minti goma ya dawo dakin,  ya kashe fitila kai tsaye gadon ya nufa ya kwanta kusa da ita, kamar zai daure ya danne abinda ke cinsa, sai ya kasa ya matsa jikinta sosai yana shanshana sassan jikinta, gabadaya ya rikice jikinsa sai  rawa yake ya birkito ta  rungumeta yayi tsam a jikinsa yana kesses din fuskarta da wuyanta.

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing,  idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:55 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176  domin karin bayani,  maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin

yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka fara amfani da maganin zaki ga sauyi, domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari 2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*113&114*

Da asubar fari 'Dayyiba ta fice daga gidanta da mummunan kudiri a zuciyarta. wani k'aramin kauye ta yiwa tsinke anan take sanya ran biyan bukatar ta, to duk da sammakon da ta buga sai da ta samu kusan mutum biyar suna zaune tsumayin fitowar wacce ta shiga zauran malamin. Dayyiba ta kama layi ta zauna a kusa da wata mata hankalinta kaf yana kan hirar da suke da abokiyar tafiyarta.

Magana suke tattaunawa akan abinda ya kawosu gurinsu bokan wacce tayi kamanceceniya da wacce ta kawo ta, ta kalli matar da fadin." Nima abinda yake tafe dani kenan, ni abinda nakeso ma a rabasu gabadaya ko kuma a haukatata ta shiga duniya."

Matar tace." Wannan duk mai sauki ne mutukar kin cika sharud'ai to bukatarki za ta biya."

Tace." A shirye nake bani da matsala duk abinda akace zanyi mutukar bukatata za ta biya."

Wannan shine 'karshen magana.......Fitowar matar dake ciki ya katse maganarsu, wacce take kan layi tayi saurin shiga ita kuma wacce ta fito daga zauran ta tsaya tana musu sallama da wani irin murmushi a fuskarta da alama akwai nasara a kan abunda tazo dashi gurin.

To d'aya bayan daya suke shiga har layi yazo kan Dayyiba ta shiga ta gurfana gabansa kafin ma ta fara yi masa bayanin abinda yake tafe da ita yace." Kina tafe da aikin babban aljani wanda yake da bukatar kafa hud'u ina fatan kin fahimta."

Gabanta yana faduwa tace." Malam har aikin nawa ya kai haka."?

Ya buga mata tsawa da fadin." Tashi ki fita ashe da sauran imani ta tare dake tunda kike jayayya damu."

Tace." Ayi hakuri ranka ya dad'e ina neman alfarma na bada kafa biyu amma samuwar kafa hud'u a gurina zai yi wuya."

Ya shiru yana kallon wani jan koko mai kurji-kurji cike da jini a ciki.

Ya kalleta da fadin." To dai gaki gashi nan yana kallonki sai kiyi masa bayani idan ya amince.

Gabanta na bugawa tace." Ubana idan zai yuwu zan bada rago mai koshin lafiya a taimaka min."

Shuru gurin yayi bayan k'are maganarta, can kuma bokan ya kama wata girgiza farar kumfa na fitowa daga bakinsa, ya kai minti goma haka kafin ya dawo hayyacinsa duk yayi wuri-wuri sai uban gumi yake.

Ya kalleta da fadin." Kin ci sa'a yau yana cikin walwala ya kuma amince da maganarki, sauran aikin kuma ya rage naki idan kika kuskure wani to aikin zai dawo kanki.

Cike da farin ciki tace." Na gode ranka ya dade zan kuma kiyaye da izinin ku."

Yace." Da daddare karfe biyu ki samu bakin kwatami (kazamar kwata) ki yanka ragon da hannun hagu ki nayi kina zagin uwarki da ubanki."

Tace." To an gama ranka ya dade.......Ya siffan ta mata kalar ragon da ake bukata sannan ya bata wata laya yace a gurin da ta zubda jinin zata binne.

Cike da farin ta dawo gida, kuma hankalinta bai kwanta ba sai da ta tabbatar ta samu kalar ragon da aka bukata.

Karfe biyu na dare ta fito babu tsoro babu imani ta fara aiwatar da mummunan kudirinta tana yanka ragon tana zagin uwarta da ubanta.........Ta gama ta haka rami da wukar hannunta ta binne layar....kamar saukar aradu taji wata tsawa! "Tashi ki gusa daga gurin."! a gigice! ta shige gida kafafunta na karkarwa.

Koda ta duba gurin da safe wayam! babu alamun anyi wani abu! hankalin ya kwanta ta koma gida da tunanin abinda zai biyo baya.

A daran kwanan soyayya sukayi sai dai kuma gari yana waye wa suka tashi da bala'i da masifa! kamar karnuka! ya nayi ta nayi a fusace! ta jefa masa kwalbar turare a goshinsa a take gurin ya kumbura! shima ya fusata ya zazzabga mata maruka ya kama hanya yayi ficewarsa zuciyarsa na wani tafasa! gabadaya hankalinsa yayi kan Hamra'u

Koda ya isa ofis din kasa samun nutsuwa yayi ya kasa aikata komai, kawai sai ya nufi ofis din Asp yana sheda masa cewa zai tafi *'Kafur* 'Kauyensu.

Asp din yace." Allah yasa dai lafiya domin naga kamar baka hayyacinka.

Budar bakinsa yace." Daf yake da ya rabu da Zinatu saboda wasu dalilai.

Asp ya tsirawa goshinsa ido da fadin." Kun samu  matsala kenan Umaru wai me yasa kake biye mata kuna abu sai kace kananun yara."

A fusace! ya daga masa hannu da fadin." Kaga saurara Asp na lura da kai dama tuntuni kai baka san laifin yarinyar nan  komai tayi dai-dai ne a gurinka,  okey shikkenan ni zan iya rabuwa da ita bani da damuwa kai ka aureta."

Asp ya dinga jin maganar nayi masa kuwwa! a kunne  hankalinsa yayi masifar tashi!  kokarin magana yake amma ya rasa abinda zai ce, yana kallonsa ya fita daga ofis din ya kasa aiwatar da komai.

Ya dauki wayarsa ya kira Zinatu, lokacin tana zaune bayan taci kuka ta koshi abin duniya isheta jin ta take kamar a cikin kurkuku bata so ta bude ido ta ganta a cikin gidan, domin hotonansa na da suke kafe a dakin duk tabi ta farfasasu.

Fashewa tayi da kuka bayan ta daga wayar.

Yace." Ki daina kuka Zinat na kira ki ne domin kiyi min bayanin abinda yake tsakaninku.

Cikin shashshekar kuka take fadin." Na tsaneshi bana k'aunarsa bashi da adalci.

Yace." Me yayi miki na rashin adalci ko dan zai kara aure ki ka tsaneshi."?

Shuru tayi ta gaza furta komai in banda ciwon kai babu abunda  ke damunta.

Ya dinga magana tayi masa shuru, kawai sai ya kashe wayar,  ya kira Madam tare da bata umarnin shiga gidan domin ta rarrasheta.

 'Bangaransa kuwa hankalinsa bai kwanta ba sai da ya ganshi ya sauka a cikin garin *'Kafur!* tukkuna.

Kai tsaye gidan Kawu Ado ya nufa, lokacin dawowarsa kenan daga kasuwa, ganinsa a birkice ya tayar masa da hankali, sai dai kuma da yaji abinda yake tafe dashi hankalinsa ya kwanta, da farin ciki a tare dashi yace." Ai wannan mai sauki ne Umaru, za'a daura auran a yau babu matsala yanzu zamuje tare da kai domin mu tattauna maganar da mahaifin yarinyar domin yaji abinda kake tafe dashi.

Yace." Ba damuwa Kawu tashi muje domin a yau din nake san na koma gida."

Kusan a tare suka tashi, kai tsaye kuma can gidansu Hamra'un suka nufa.

Abu kamar al'mara  gari ya dau'ka!  jama'a sukayi dafifi!  a kofar gidan malam Shafi'i  Kawu Ado ya bada kudi aka siyo goro da alawa....Shi kuma angon ya ajiye dubu hamsin kudin sadaki....Limami ya daura aure bayan gabatar da sallar magariba.

Cikin gidan kuwa Dayyiba cike da 'yan uwanta da k'awaye da makota kowa da abinda yake fad'a.....Da yawa sunfi gazgata cewa ta shiga ta fita a cikin al'amarin, domin dai kowa ya san wata shida aka sa amma ko wata daya ba a cika ba an daura aure sai kace wasan yara.

Hamra'u kamar ta zuba ruwa a kasa tasha saboda farin ciki, hakika babu abunda za tace da mahaifiyarta domin ta taka muhimmiyar rawa a cikin rayuwarta.

A daran ya dauketa suka kama hanyar gida. gabadaya tunaninsa ya tsaya cak!  saboda duniyar ma gabadaya ta rikice masa ya rasa wane irin tunani zai yi, gani yake kamar duk abinda yake mafarki ne.

Cikin dakinsa ta kwana, kuma babu wani abu da ya shiga tsakaninsu, to ina kwanciyar hankalin da wata mu'amula zata wanzu babu ma sha'awa a tare dashi.

Da sassafe ta fita daga d'akin, lokacin yana toilet yana wanka. fitowar ta akan idon Marakisiyya, al'amarin da ya bata mamaki mutuka! ba tayi kasa a gwiwa ba taje ta sanar da Uwar dakinta abinda idonta ya gane mata.

Tace ta tashi  ta taje....bayan fitar Marakisiyyar  minti goma ta nufi sashen nasa...........Koda ta shiga basu kwashe lafiya ba, dan da abun yayi tsamari ma turo ta yayi ta fadi bakin kofa ya mayar da kofarsa ya rufe, ya cigaba da abinda yake.

Ta zauna taci kukanta ta k'oshi, ido jawur! ta fito daga sashen, sai sukayi kicubus da Hamra'un tayi wanka tayi ado sosai sai kamshin turare take.....kallon banza tayi mata kafin taja tsaki ta shige ta bar ta a gurin.

Girgiza kanta kawai tayi ta nufi gurin Uwale domin jin k:arshen labarin.

Ta sameta a zaune fuskarta akwai alamun damuwa.

Suka gaisa sama-sama  kowa da abinda ya dameshi a zuciya.

Uwalen ce ta fara magana kamar haka......"Zinatu kiyi hakuri kinji ko, na san wannan abun shiryayye ne amma babu komai duk  auran da ba'a gina shi ta hanyar Allah da Annabi ba, baya zuwa ko'ina kiyi hakuri da duk abinda za ki gani."

Tace."Uwale me yake faruwa ne? naga yarinyar nan Hamra'u sai shige da fice take a gidan, shin yaushe ma ta dawo? kuma naji kina maganar aure,  ban san me yasa ba tun jiya muke rigima da mijina na rasa abinda nayi masa."

Murmushi takaici tayi kafin ta shiga warware mata abinda yake da akwai, tace." Ni kaina ban sani ba, sai yanzu da ita Hamra'un take sheda min cewa jiya da magariba aka daura auran shi Umar din da kansa yaje garin akayi komai a ka gama to kinji abinda yake faruwa.

Zazzafar ajiyar zuciya ta sauke kafin tace." To saboda kawai zaiyi aure sai ya zama tamkar mahaukaci! gabadaya fa tsakanin jiya da yau ya fice daga hayyacinsa.

Tace." Ni kaina yau kwana biyu kenan rabon daya shigo mu gaisa da duk rintsi yakan shigo idan zai fita, sannan kuma idan ya dawo ma zai shigo ya dubani. wannan dalilin yasa nake zargin wani abu akan al'amarin.

Tace." Uwale idan da matsala ni zan tattara kayana na tafi gida hankalina sai yafi kwanciya bana san tashin hankali."

Ta kwantar da kai da fadin." Kada ki yanke wannan hukuncin Zinatu ki cigaba da hakuri duk abinda mijinki yake baya hayyacinsa.  Asiri akayi masa."

Ido ta tsira mata tana mamakin maganar ASIRI to waye zai yi musu ASIRI irin wannan.

A tare suka shigo  falon,  duk suka zuba musu ido suna kallo....Ita Hamra'un kicin ta nufa, shi kuma ya zauna kusa da Uwale suna gaisawa.

Babu yabo babu fallasa ta amsa sai kallonsa take tana mamakinsa.........Ya dan duba agogon hannunsa da fadin." Uwale sai ki kaji sabon al'amari ko."?

Tace." Eh abun ya bani mamaki Umaru ya akayi ka sauya shawara."?

Kai tsaye yace." Hakan ne samun kwanciyar hankalina domin bana samun nutsuwa a tare da wacce nake rayuwa da ita.

Tace." Wannan maganar sam bata dace ba Umaru me yasa zaka sanja hali zaka kawo rashi zaman lafiya a gidanka."

Yace." Uwale ki bar wannan maganar don Allah nifa dama can dole akayi min yanzu ne na auri zabin raina."

Ta fusata! zuciyarta na tafasa! tace." Yanzu ma ba'ayi maka dole ba  ka *SAKE NI MANA."!*

Innalillahi wa'inna ilahi raji'un! abinda Uwale take nanatawa kenan,  lallai Dayyiba bata da Imani tana so ta raba sunnar ma'aiki.

Ta sake maimaita maganar kamar sabuwar mahaukaciya.....*"KA SAKE!* ni idan ka cika dan halak ne kai." Jikinta har karkarwa yake ta mike tsaye tana so taje gurin da yake zaune.

Ya mike a zabure! da fadin" Kada ki kuskura kizo nan sai kakkarya miki 'kafafu." yana gwada yanda zaiyi da hannunsa.......Ba ta tsorata ba ta 'karasa da fadin." Gani dama tun jiya kake duka na ka karya ni kaga abinda zai faru."

Ya daga hannu da niyyar zabga mata mari Uwale ta rike hannun tana kuka take fadin." Wannan wane irin tashin hankali ne Umaru anya ba za kayi wa kanka fad'a ba."

Hawaye masu zafi suna gudana a saman fuskarta tace." Uwale ki kyaleshi ya aikata abinda yayi niyya dama ai ba yau bane farko.

Tace." Aa ba za'ayi haka ba Zinatu kiyi hakuri ki koma gurinki insha Allah komai zai daidaita."

Hanci ta shaka kafin ta girgiza kanta ta juya da sassarfa ta fita daga falon.

Ya koma yana zauna yana wani irin nishi, sai gumi yake kamar wanda yayi 'yar tsere......Hamra'u dake tsaye da fulas din shayi a hannunta ranta ya 'baci ganin abinda takeso bai faru ba, jikinta a sanyaye taje ta ajiye fulas din kan daining ta koma kicin domin fito da sauran kayan breakfast din.

Ta shiga sashenta ta sanya Baraka ta hada mata kayanta gida zasu tafi .

Ta zaune gefan gado jikinta sai rawa yake ta nemi number Asp murya a dashe suka gaisa, tace." Zan tafi gidanmu ranka ya dade bahaushe yace." Ta inda aka hau ta nan ake sauka."

Da sauri yace." Zinatu idan na isa dake kada ki kuskura kije ko'ina kinji abinda nace miki ko."?

Kashe wayarta tayi bata tsammanin zata tsaya jiran wani abu.

Wanka tayi a gurguje! ta shirya, ta umarci hadimanta suka shirya.......Direban dake dawainiya da gidan ya daukesu a mota suka dauki hanyar *KANO*

Minti ashirin da tafiyarsu Asp ya shiga gidan, kai tsaye sashenta ya nufa........ya tarar ko'ina a rufe! hankalinsa a tashe ya nemi number wayarta a kashe.

Hannu na rawa ya kira abokin nasa yana ganin kiran yaki d'auka idan akwai wanda ya tsana a duniya yake jin haushinsa Asp din ne.

Yayi ta kiran wayarsa yaki dagawa, sai ya hakura ya shiga har gurin Uwale suka gaisa, anan ne ta san da cewar Zinat din bata gidan.

Tafi Asp din shiga tashin hankali, lallai babu shakka a wannan karan dole ta tauna tsakuwa dan aya taji tsoro.

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing, idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:55 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176 domin karin bayani, maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka fara amfani da maganin zaki ga sauyi, domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari 2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*115&116*
Suna shirin tashi daga aiki mai girma Commissioner ya same shi a ofis, cikin girmamawa ya mika masa hannu suka gaisa kafin." Yace." Tunda naga mai girma da kansa to na san babban al'amari ne."

Murmushi yayi kafin yace." K'warai kuwa Umaru wani aiki ne ya taso sai naga da cewar kaja tawaga ma'ana ka zama jagora a tafiyar."

Yace." Insha Allah zan bayar da gudummawata.

Wata takarda ya fito da ita yana masa bayani cewa za suje *ran gadi* Zamfara saboda rashin kwanciyar hankalin da suke fama dashi.....za su hadu da jami'an tsaron garin domin kawo karshen ta'addancin da yake faruwa. gwamnatin garin tare da jami'an tsaron can suka bukaci wannan taimakon daga gurinsu domin suna sa ran idan ya shiga cikin al'amarin za'a samu maslaha."

Ajiyar zuciya ya sauke kafin yace.'' Ranka ya dade babu matsala yaushe ne tafiyar."?

Yace." Idan Allah ya kaimu gobe amma da Asubah zaku dauki hanya."

Yace." To Allah ya kaimu lafiya, amma me yasa ba'a za'ayi tafiyar da Asp ba."?

Girgiza kansa yayi da fadin." Akwai dalili shi akwai muhimman ayyukan da zamu gabatar tare dashi."

Ya mika masa hannu da fadin." Allah yasa mu dace." Ya amsa da ameen ya rabbi.

Sallama sukayi cikin mutunci da girmama juna. tun lokacin da Commissioner ya fahimci cewa Umar din ba irin mutanan da ake nuna su da yatsa bane ya kiyaye abinda zai kawo musu samun matsala domin ya fahimci cewar Umar din yana da babban matsayi a government house bayan haka kuma manya 'kasa suna ji dashi, domin shi kansa shugaban k'asa yana alfahari dashi saboda yana taka muhimmiyar rawa gurin dakile harkokin ta'addanci a kasa baki daya.

A maimakon ya kira Asp ya sheda masa abinda yake faruwa sai kawai yaja bakinsa yayi shuru haka kawai yake jin wani irin haushinsa da kiyayyarsa a zuciyarsa duk wanda ya danganci yarinyar haushinsa yake ji.

Asp ya samu labari a bakin Commissioner dole sai da sa hannunsa komai zai tafi dai-dai, koda yaga abokin nasa ne zai jagoranci tafiyar sai yayi mamaki mutuka amma bai nuna a fuskarsa ba

saboda baya so wani ya fahimci cewa akwai sa'bani a tsakaninsu.

Ya isa gida cikin tarin gajiya da damuwa da rashin walwala duniyar gabadaya tayi masa zafi ya rasa wane irin tunani zai yi.

Ya samu Uwale ta had'a kayanta tsaf  tana jiran shigowarsa, ganinsa sai kawai ta fashe da kuka! kariris!

Hankalinsa ya tashi ainun!  domin ko kadan baya kaunar damuwarta.

Ya rungumeta a jikinsa yana rarrashinta,  amma fafur! taki tayi shuru!  ya kalli Hamra'u da tayi tsuru-tsuru!  alamun rashin gaskiya ya bayyana a tare da ita,  yace." Me yake faruwa ne shin me kukayi mata."?

Tace." Wallahi nima ban sani ba tun dazu nake tambayarta tayi shuru sai share hawaye take wai *'Kafur!* za ta tafi."

Ya kalleta da fadin." Wane irin *'Kafur* kuma?  ai na dau'ka ko sati  uku baki da zuwa ba, ko wani ne ya mutu a can."?

Tace." Umaru zama a tare da kai bashi da amfani tunda ban isa na saka ba kuma ban isa na ha naka ba, to zanyi tafiya ta k'auye zamana a can yafi alkairi."

Yace." Me nayi miki wanda ya janyo wannan maganar."

Tace." Akan abunda kake Umaru shin ko ka samu ta'bin hankali ne."?

Yace." Lafiyata lau na san dai duk kina wannan maganganun akan Zinatu, gabadaya ni yanzu bana ra'ayin zama da ita.

Tace." Shine dalilin da yasa ka koreta dada gidanka.?

Babu wata damuwa a tare dashi yace." Aa ni ban kore ta ba, ita ta kori kanta."

Tace." To shikkenan  tunda kace haka mutukar kana bukatar zama tare dani kaje kayi bikon matarka."

Yace." Uwale ni yanzu muhimiyyar tafiya ce a gabana gobe insha Allah, sai dai idan na dawo."

Shuru tayi kafin tace." Umaru baka kyauta ba wallahi jiya  abokinka yazo gidan nan hankalinsa a tashe, a bakinsa  na samu labari  cewa yarinyar bata gidan.

Yace." Kina nufin Asp yazo gidan nan bayan na fita."?

Tace." Eh yazo kuma yayi min cikakken bayani akan abunda yake faruwa tsakaninka da matarka, gabadaya kaine baka da gaskiya Umaru me yasa ba zaka tausaya mata ba duba da juna biyun da take tare dashi."

Yayi shuru zuciyarsa nayi masa wani irin  zafi! Asp ya samu damar da har yake shigo masa gida ba tare da izininsa ba, har ya samu damar da zai dinga bibiyar abunda ya shafi iyalinsa, shi ai ba yayi masa wannan katsalandan din, ya kamata a wannan karan ya nuna masa kuskuransa.

Hamra'u ta had'a masa ruwan wanka yayi ya samu sassauci amma kadan domin shi kadai ya san irin bakin cikin dake cin zuciyarsa.

Ya sanya jallabiya da gajeran wando ya fito falo fuskar nan a murtuke!

Ita kuwa Amarya ta rangad'a ado sai kamshin turare take mai dad'i da tayar da sha'awa.

Yana zama gurin cin abinci ta isa gurin cikin kwarkwasa da karairaya ta hada masa abincin ta zauna kujerar dake fuskantarsa tana murmushi take bashi labarai irin na jan hankali.

Shi dai uffan bece ba abincinsa kawai yake ci, abinda ya dame shi  ne a gabansa.

A gabanta ya kira wayar Zinatu. koda ta duba taga shine sai ta ajiye wayar........Lokacin mahaifiyarta ta shiga dakin ta samu kiran ya sake shigowa a karo na biyu.

Ta kalleta cikin tausayi da jin kai  irin na uwa,  tace." Ki daga wayar mana."

Murya a dashe! tace." Shine fa."

Tace." To sai me? ki daga kiji abinda yake tafe dashi."

Kamar ba taso ta daga wayar tasa a kunne can kasan makoshi tayi sallama!

Gyaran murya yayi kafin yace." Na dawo na samu labarin kin tafi gidanku shin me kike nufi da aikata hakan."?

Shuru tayi ta gaza furta komai.

Yace." Ke nake sauraro ko kin gaji kamar yanda nima na gaji."?

Hanci taja kafin tace." Bani da lokacin tsayawa na saurarin wannan mayaudariyar muryartaka duk hukuncin daka yanke dai-dai ne a guri na."
Kawai ta katse wayar ta ajiye. wasu zafafan! hawaye suka kwace mata! ya cuceta ya dirka mata ciki yana mata iskancin da ransa yake so.

Uwar ma kamar ta fashe da kuka saboda da takaici. kaf rayuwar yarinyar kwatankwacin rayuwarta ne! tausayinta duk ya isheta, ta sassauta murya da fadin." Kiyi hakuri ki kwantar da hankalinki insha Allah zamu tattauna maganar da mahaifinki idan auran ba zai yuwu ba a rabu shi yafi alkairi."

Da sauri tace."Mammah ni kaina nafi bukatar rabuwar, babban takaici na wannan cikin da nake dauke dashi."

Tace." Wannan kuma sai ki barwa Allah, domin shi ya barwa kansa sanin abinda yake boye, kawai kiyi fatan rabuwa dashi lafiya."

Kasa magana tayi kawai ta sunkuyar da kanta sai so take ta tsayar da hawayen dake zuba amma ya gagara! zubar hawayen shine samun zaman lafiyarta.

Zazzafar ajiyar zuciya ta sauke kafin ta girgiza kai ta kama hanyar fita zuciyarta cike da tunanin neman mafita.

Kishingide ta sameshi a dakin hutawarsa.
A nutse ta zauna kusa dashi kafin tace." Barka da hutu ranka ya dade."

Ya amsa da "Barka kadai Gimbiyar mata ya gida ina 'yar uwar taki."? ya tambayeta Safara'u saboda ya san abinda ya kawo ta gurinsa bayan ba girkinta bane tabbas itama Safara'un tana tafe.
Tana kokarin magana Safah din tayi sallama, jikinta nannade da lifaya kwantankwancin ta jikin Aysha.

Suka gaisa cikin girma da mutunta juna.

Zamansa ya gyara yana kallonsu daya bayan daya kafin yace." Labarin gizo a tambayi koki tun kafin kuyi min bayanin abinda yake tafe daku na karanci hakan a fuskokinku. to ina jiran shigowar Magajin sarki ne domin shi nakeso ya kira mijin yarinyar muji daga bakinsa."

Gimbiyar tasha kunu da fadin." Ranka ya dad'e wannan al'amarin fa bana wasa bane ya za'ayi a matsayinka na mahaifin yarinyar nan ka wakilta wani ai sai ya kara rainawa mutane hankali saboda haka kai ya cancanta kayi magana dashi."

Yace."Aysha ko bayan raina Abdullahi shine Magaji na, wannan dalilin ya sanya nasa shi a cikin maganar domin yayi wa 'yar uwarsa wakilci, ita tazo da magana to amma yana da kyau shima mijin nata aji daga bakinsa.

Tace." Wannan yaro fa bashi da kirki! ranka ya dade in banda wulakanci da ciki zai kori yarinya me tayi masa haka da zafi."?

Yace." Ashe har kin manta halinta kenan? Aysha idan ke kin manta wacece Zinatu ni ban mance ba, kada ki manta irin d'auki ba dadin da muka dinga yi da ita kafin ta amince da auran, ko shakka ba nayi matsalar daga gurinta take.

Safah ta katse shi ta hanyar fadin." Kada kayi gaggawar yanke hukunci ranka ya dad'e! yanda yarinyar nan ta zabge lokaci guda shine zai nuna mana cewa akwai matsalar da take faruwa a tsakaninsu kuma taura d'aya bata taunuwa, bahaushe yace idan anbi ta b'arawo to abi ta mabi sawu, dole shima nasa laifin saboda haka yana da kyau yazo gabanka ku tattauna domin magana ta waya ba zata gamsar ba."

Yace." Wannan shawarar taki tayi Safara'u  abinda za'ayi kenan. Insha Allah komai zai warware.

Magajin Sarki ne ya shigo da sallama a bakinsa.

Gabad'aya suka amsa. ya samu guri ya zauna kafin ya fara gaishe su......Maimartaba yace." Ka kira Umaru mijin Zinatu kace masa ina san ganinsa idan ya samu dama."

Ya fito da waya domin bin umarni.

Daf da zata katse ya daga wayar............bai ma duba suna ba, sai da yayi masa bayanin kansa sannan yace." Magaji afuwa don Allah ya mutan gida ina fatan kuna lafiya."

Yace." Kowa Lafiya lau  dama Maimartaba ne ya bukaci ganinka idan ka samu dama."

Ajiyar zuciya ya sauke kafin yace." Magaji ayi min afuwa ina da uzuri aiki zai kani Zamfara sai dai idan na dawo."

Ransa ya baci da jin abinda yake fada.......Yace." Okey to idan babu damuwa inaso na san dalilin da ya sanya Zinatu zuwa gida."

Yayi jim yana nazarin maganar kafin yace." Babu wani 'kwakw'kwaran dalili nima kawai na dawo

gida na samu bata nan."

Yace." No! akwai dalili  Goje sai dai idan ba zaka fada ba."

Murmushi yayi kafin yace."Ka tambaye mana ni dai na san lafiya lau muke zaune amma ina tunanin kishi ne dalilin da ya sanya ta yanke wannan hukuncin."

Yace."Kishi kuma."?

Yace." Eh 'kwarai kuwa  na 'kara aure  kwana uku da suka wuce wannan shine abinda nake tunani."

Yayi murmushi da fadin." Ni a ganina wannan kadai ba zai janyo har tazo gida ba ko ka manta da lalurar da take tare da ita."? A dan kausashe! yayi maganar.

Shima ya fusata!  yace." Magaji yarinyar nan fa bani na koreta ba, ita ta kori kanta, kuma saboda ita ba zan fasa abinda nayi niyya ba, nasan kasan mata hudu Allah ya halasta min to akan wata ba zan tauye rayuwata ba."

Ya girgiza kansa da fadin." Okey to babu damuwa Allah ya sanya alkairi ya bada zaman lafiya.

Ya amsa da "Ameen ya Allah."

Cikin rashin dadi sukayi sallama da juna.

Da yake hands free yasa wayar duk suna jin abunda suka tattauna.

Yana kishingide bai ce komai ba.....Gimbiya Aysha kuwa sai fad'a take da fadin." Wannan auran warwareshi shi yafi alkairi dama can ita al'amarin be kwanta mata ba, auran jahili wanda yayi rayuwa a daji! bashi da fa'idah mutumin kauye akwai karancin ilimi ta tare dashi babu abunda ba zai aikata ba."

Duk yana jin sababin da take bai ce komai ba har sai da ta gama tukkuna ya gyara zamanshi kafin ya fara magana kamar haka.

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing,  idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:56 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176  domin karin bayani,  maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka   fara amfani da   maganin zaki ga sauyi,  domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari  2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*97&98*
Wani irin bacci sukayi mara dad'i sakamakon damuwar da suke ciki. da yake namiji ne shi yakan iya danne damuwarsa ita kam ta kasa dannewa domin  gabadaya jin kanta take a takure! ita akan kin kanta tasan yun'kurin da tayi ba mai kyau ba ne, shiyasa take bala'in jin kunyar hada id'o dashi!

Kwance ya sameta saman gado tun bayan sallar asubahi ta kwanta tana k'okarin gayyatar bacci yaki zuwa babu shi ma gabad'aya a idonta tunani yafi yawa a tare da ita.

Ido ta tsira masa har ya k'araso bakin gadon, ya shirya tsaf da niyyar fita gurin aiki.

Babu yabo babu fallasa ya kalleta da fadin."  kin tashi lafiya."?

A hankali ta amsa tana dan lumshe idonta.

Kallonta yake yana ayyana abubuwa da yawa a kanta, yanayin ta ya nuna kamar mara lafiya.

Ya daure zuciyarsa yace." Ko kina da damuwa ne."?

Zuciyarta ta karye hawaye naso ya zubo tana mayar dashi bata bukatar tayi masa kuka tunda yana kiranta da shagwababbiya.

Shuru tayi ba tace masa komai ba. sai da ya sake maimata maganar sannan tace." Lafiya na kalau."

Ya kalli agogon dake daure a hannunsa da fadin" Okey haka nake so ni zan fita amma idan kinji wani guri nai miki ciwo ki kira ni a waya."

Ta kalleshi k'auna da sonsa na kara nunkuwa a zuciyarta, a jiyar zuciya ta sauke a hankali tace " To."

Ya kama hanyar fita jikinsa duk babu dadi, yarinyar ta tsaye masa a rai.

"Haka zaka fita ba kayi breakfast ba."?

Maganarta ta katse masa hanzari. juyowa yayi yana kallonta.

Ta sunkuyar da kanta domin bata jurewa kallon kwayar idonsa.

" Kada ki damu zan samu abunda zan ci buri na ki tashi ki nemi abinci kici ko dan abunda ke cikin ki idan kinyi min haka kin gama min komai."

Ta yun'kura ta tashi tana d'an ya mutse fuskarta.

Saurin kawar da kansa yayi sakamakon ganin zahirinta kayan bacci ne a jikinta wanda suka fitar da wasu sassan na jikinta.

Yay gaggawar bude kofar dakin ya fita yana jin yanda jarumarsa ke motsi har ta fara yun'kuri! al'amarin ya bashi mamaki mutuka! koda yake ba'a abun mamaki bane idan anyi la'akari da kwanakin da ya dauka rabon da ya hada shinfida da ita.

Yana zama a ofis kiran wayar Maimartabar ya same shi.

Suka gaisa cikin mutunci da dattako.

Maimartaban yake sheda masa cewa suna da baki da misali sha biyu jirginsu zai sauka anan filin jirgi na Katsinan.

Farin ciki yayi sosai ya dinga godiya tare da adduar Allah ya saukesu lafiya.

Sukayi sallama cikin girmama juna.

Cike da farin ciki ya kira wayar ta.

Fitowarta daga wanka kenan tayi saurin dauka tare da zama gefan gado.

Ya sheda mata abunda yake faruwa.

Jikinta a sanyaye tace." Me yasa ka sheda musu abunda yake tsakanimu."? murya na rawa take maganar

Yayi shuru yana nazarin maganarta.

Tace." Shikkenan na shiga uku  ka janyo min bacin ran iyaye na."

Ya kwantar da murya da fadin." Ni fa ban fada musu maganar da wata manufa ba, na fada musu ne domin su ta ya ni neman mafita, amma bana fatan ranar da zan shiga tsakaninki da iyayenki."

Ta share hawayen saman fuskarta  kawai ta kashe wayar saboda kukan da yake kokarin kufce mata.

Sake kiran wayar yayi tana kallo tana ringing taki dauka, ita yanzu tashin hankalinta zuwan Mahaifiyarta tasan bacin rai ne zai biyo ba.

Babu kuzari a tare da ita ta kimtsa jikinta, ta nemi kujera ta zauna tana duba agogo  sha biyu ta gota tasan yanzu mybe sun sauka .

Wayarta ta d'auka cike da fargaba ta kira mahaifiyarta.

Murya na rawa tace."Mommy ina wuni."?.

A dakile ta amsa gaisuwar.

Ta daure tace." Kun sauka ne."?

Gimbiyar tace." Eh sun sauka dan yanzu suka kira waya,  babu ni 'Yar uwata ce sai yayyunki."

Ajiyar zuciya ta sauke tana jin sanyi a zuciyarta tasan SAFAH tana da sanyi rai ba kamar mahaifiyarta ba.

Ta katse tunaninta da fadin." Kin kyauta abunda ki kayi ZINA kin janyo min zagi da cin mutunci na gode." Ba ta jira amsarta ba, kawai ta kashe wayarta.

Ita kam shuru tayi da waya a hannunta  gabadaya ta rasa ya za tayi da rayuwarta.

SAFAH  tare da Hassana da Hussaina da Magajin sarki suka sauka a gidan......Farin cikin ganinsu yasa ta fashe da kuka!  ta dinga rungumesu  duk ta rasa yanda za tayi saboda jin dadin ganinsu.

Magajin Sarki yace." Ki samu nutsuwa haka zuwan mu gidanki  baya nufin farin cikin ki. akwai babban dalili ne ya kawo mu gidanki."

Ta nemi kan kujera ta zauna jikinta duk a sa'bule.

Ya fara yi mata fad'a tare da kawo mata ayoyin al'kur'ani da hadisai duk dai akan abunda ta aikata mara kyau!

Shuru tayi ba ta iya cewa komai ba, dukkaninsu kowa ya tofa albarkacin bakinsa mussaman SAFAH da ta dinga yi mata nasiha mai ratsa jiki anan ne ta zubar da hawaye,  tana kukan tace." Mammah dan Allah ku gafarce ni wallahi tsautsayi ne da son zuciya insha Allah ba zan sake maimaita abu mai muni irin wannan ba.

Hassana tace." To Alhamdulillhi haka muke so muna rokon Allah ya sauke ki lafiya ya kuma inganta duk abunda zaki haifa."

Gabadaya suka amsa da "Ameen." Kafin su fara yun'kurin tafiya.

Tace." Mammah har zaku tafi ni wallahi na dauka kwana za kuyi."

Magajin Sarki ya harareta da fadin." Sai kace mahaukata ko."?

Ta 'bata rai da fadin." Aunty Hassana don Allah ku zauna ku kwana mana."

Hussaina tace." Baki da hankali ZINA daga zuwa sai mu kwana ke a ganinki hakan yayi

dai-dai"?

Tace." To meye wallahi babu matsala kuna gani dai kowa da gurinsa to me zai dame ku."

SAFAH ta mike tsaye tana gyara yafan mayafinta  da murmushi a fuskarta tace." Zinatu rigima kin ga tashi kiyi mana Jagora cikin gidan mu gaisa dasu. ke kanki kin san abinda kike bukata ba mai yuwu wa bane.

Cike da rashin dadi ta tashi ta shiga daki domin dauko mayafi, nan Aunty Hussana ta bita dakin ta bata wata leda dake cike da turarukan wuta da humra masu kamshin gaske,  sai kuma kaninfari da yawa cikin wata leda a d'aure, tace mata ta jika cikin wani abu tana shan ruwan.

Godiya sosai tayi mata kafin su fito daga dakin a tare.

 Uwale tsohuwa mai dattako! ta kar'be su hannu biyu tana ina a saka ina a sauke dasu.......Da yake basa rabo da abinci ta sanya Hamra'u ta had'a musu abinci wanda zai gamsar dasu.

Haka nan suka saki jikinsu suka ci abinci wanda Hamra'u ta sarrafa sosai Allah yai mata baiwar iya sarrafa abinci ko wane iri ne a zahiri suma sun yaba sosai kuma ci sun gamsu.

Itama ZINAT din taji dadin yanda aka karramasu ta saki jikinta tamkar akwai sabo a tsakaninsu, har tana jan Hamra'un da hira, wanda hakan ya basu mamaki mutuka, to itama dai Hamra'un saki tayi kamar wani sa'bani bai  ta'ba shiga  tsakaninsu ba.

Tafiyarsu keda wuya ya kira wayarta yana tambayarta.

Tace." Ai har sun tafi."

Cike da mamaki yace." Sun tafi."?

Tace."Eh nima wallahi babu yanda banyi dasu ba su kwana amma sun tafi kamar ana korarsu."

Ya girgiza kai da rashin jin dadin hakan, yace." Me yasa da zasu tafi baki kira ni kin sheda min ba, sai  na bar duk abunda nake nazo mu gaisa."

Tayi shuru domin ba tasan me za tace ba.

Yace." Laifin duk naki ne Zina kwata-kwata banji dadin  tafiyarsu ba naso mun gaisa da juna sosai."

Tace." Kayi hakuri amma ai sun gaisa da Uwale har suka ci abinci a gurinta.

Yace." Hakan ma yayi amma Uwale daban ni daban."

Tace." Hakane kuma." Shuru ya ratsa tsakaninsu kafin tace." Daddare me kake bukatar ci."?

Kai tsaye yace." Towon dawa da miyar kuka."
Iya gaskiyar sa ya fadi maganar.

Amma sai ta kyalkyale da dariya da fadin." Towon dawa!  gaskiya ni ban iya ba."

Yace." Aikuwa ki koya domin shine favorite d'ina mussaman dumame towo ko wane iri ne ina sonsa.

Tace." To shikkenan kada ka damu yau ma da kaina zan maka abincin insha Allah."

Yace."Okey da can bake kike ba kenan."?

Da sauri ta gyara maganarta tace." Ni ce mana ina nufin yau na mussaman zanyi maka towon da kake so.

Yace." Idan da akwai matsala ki zauna ki huta kin san baki da koshin lafiya."

Murmushi tayi da fadin." Naji sauki ai ina bukatar samun ladan aure."

Murmushi jin dadi yayi yana juyi kan kujerarsa yace." Shikkenan yau da daddare za muyi hira kenan."

Tana 'yar dariya tace." Sosai irin wacce ba mu ta'ba yin irinta ba."

Yace." Alhamdulillhi na gode Allah da ya bani ke a matsayin matata."

Tace." Nima haka amma  dai ka yafe min laifi na  ko."?

Ya gyara zamansa da fadin." Na yafe miki kuma da ikon Allah zan d'aga miki ki shiga  aljanna Bakya laifi a guri na GIMBIYATA."

Tace." Na gode *Mazan Fama!* Allah ya barmu tare." ya amsa da "Ameen wani irin farin ciki na ziyartarsa.

Aikuwa kamar yanda tayi masa alkawari, da kanta ta shiga kicin din, ta sanya Marakisiyya ta harhad'a mata komai wanda zata bukata, yau abunda bata ta'ba yi ba zata kwatanta.

Ita kad'ai a kicin din tana gwagwarmaya! duk ta jigata, sai gumi take abunka da wanda bai saba ba.

Akayi rud'e kalau! aka rufe ruf! sannan aka shiga had'a miya, tayi dubarar silala naman da albasa da kayan 'kamshi amma bai wani dahu sosai ba, ta zuba su daddawa da kayan miyan data murza a gireta, ta zuba uban farin mai tamkar me shirin yin jar miya.........Can rud'en dake rufe ya fara za'bal'bala kafin kice me murfin tukunyar yayo sama talgen ya fara kumfa yana zuba saman gas din, da sauri take k'okarin cire murfin aikuwa ta 'kone a hannu!! baya ta matsa tana ihu!! taje ta kwance famfo tana wanke talgen daya kona ta. kuka ne kawai ba tayi ba fatar hannunta tayi jajawur! ido jawur! ta fita daga kicin.

Ta zauna kan kujera tana mayar da numfashi..........A'a abu kamar wasa hannu ya fara tashi! ga wani irin zafi da yake mata......kira ta kwalawa Marakisiyya tace mata maza taje ta k'arasa ita tayi abunda zata iya.

Tashi tayi ta shiga d'aki ta kwanta, tana jinyar hannunta.

Daf da zai shigo gidan ya kira wayarta, ta daga su gaisa yana tambayarta jikinta, tace." Lafiya amma garin yi maka towo na k'ona hannu.

Yace." Subahanallahi garin ya hakan ya faru."?

A shagwabe tace." Talgen ne ya dinga zuba naje bude tukunya ya zubo min a hannu."

Yaji duk wani iri a jikinsa yace." Sannu my love amma ba sosai bane ko."?

Tace."Eh ba sosai ba amma har ya tashi sai ciwo yake min."

Yace." Yi hakuri kinji bari  yanzu zanzo nai miki addua insha zaki ji sauki."

A sanyaye tace." Okey my darling  na gode sai ka shigo."  kashe wayar yayi yana Allah-Allah ya isa gidan.

Wanka tayi ta kimtsa domin bata so ya shigo ya sameta babu ado, tunda tasan yana san haka shiyasa ta mayar da hankali gurin yi masa ado da kwalliya na kece raini.

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing,  idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:56 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176  domin karin bayani,  maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka   fara amfani da   maganin zaki ga sauyi,  domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari  2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*99&100*
Wani sanyi ne ya ziyarceshi yayin da yayi tozali da ita a hakimce tayi ado irin wanda yake bala'in burgeshi, in  ban da kamshi babu abunda take........Gabadaya wata irin kasala ta rufeshi tsananin sha'awarta ya sake kamashi,  shi dai yana bala'in son kamshin jikinta.

Kusa da ita ya zauna ya jifanta da wani irin kallo, ta marairace fuska tana kallonsa kafin tayi masa barka da zuwa.

Ya dubi hannun da ya kone!  tsigar jikinsa ta tashi, a hankali ya rike hannun ya fara tofa mata addua  ya gama ya kalleta cike da kulawa yace." Ke zanyi wa sannu  duba da irin tsautsayin da kika samu ta dalili na,  tunda kika sheda min hankalina ya tashi ina Allah-Allah na iso gida naga

halin da kike ciki, amma abun mamaki sai na sameki cikin koshin lafiya kinyi ado da kwalliya irin wanda nakeso ina mai tabbatar miki da cewar ina alfaharin kasancerki a matsayin matata."

Murmushi tayi tare da jin dadin kalamansa, dama kuma babban burinta bai wuce ace ta siye zuciyarsa kaf ya daina ganin ko wace mace a gabansa ba sai ita, ta lura yana da sau'kin kai! kuma ta fahimci ya kamu da tsananin sonta wannan abin alfahari ne a gurinta.

*****

Da safe kafin ya fita gurin aiki yake sheda mata tafiyar da za suyi, sam ba tayi tunanin cewa har da ita za'ayi tafiyar ba, sai da taji yana fadin." Za ku kwana biyu a k'auyen domin kisan 'yan uwana suma su sheda ki sosa."

Sai ta kasa 'boye bacin ranta! ta dan 'bata fuska tana kallonsa.

Ya fuskanci ba tayi na'am da tafiyar ba, ransa bai masa dadi ba.

Ganin taki yin magana ya sanya ya tashi da niyyar fita.

Ta kalleshi a lokacin da yake gyara f-cap din kansa. da kyar tace." Sai ka dawo."

A dakile ya amsa ya kama hanyar fita zuciyarsa duk babu dadi, sam bai ji dadin abinda tai masa ba, ya lura har yanzu ba ta k'aunar a halinsa, a ganinsa duk soyayyar da take nuna masa a banza take, mutukar ba zata kaunaci yan uwansa ba.

Ya saba kiran wayarta idan ya samu saukin aiki amma a ranar sai ya share ta yana so ya nuna mata kuskuranta

B'angaranta kuwa ba wai zuwa 'kauyen ne ba taso ba,cewar da yayi zata zauna tare dasu har na tsayin wasu kwanaki shine abinda ya 'bata mata rai! gaskiya bata tunanin kwana a kauyen 'kafarta-'kafarsa.

Da taji shuru bai kira ta ba, sai ta kira shi, ya daga yana shan k'amshi.

Murmushi tayi kafin tace." Fushi kake ko darling."

Gyaran murya kafin yace." Fushi akan me? a halinki ai ba sabo bane a gurina."

A shagwabe tace." Au! mugun hali ne dani."?

Yayi shuru bai ce mata komai ba.

Ajiyar zuciya ta sauke a sanyaye tace." Kayi hakuri ba wai bana so naje bane naji kayi maganar kwanaki shine bana so."

Ya fusata!  yace." Kin ga idan ma ba zakije ba kiyi zamanki okey." Kawai ya kashe wayarsa.

Ta dinga bin wayar da kallon mamaki! ita fa yanzu kwata-kwata bata bukatar abunda zai shiga tsakaninsu, amma ta fahimci akan 'yan uwansa zai iya cin mutuncin kowa.

A'a! abu kamar wasa 'karamar magana na nema ta zama babba!  fushi yake da ita sosai! dan koda ya dawo daga gurin aikin bai shiga gurinta ba, ya gama duk abunda yake ya nufi sashensu Uwale, zuciyarsa duk babu dadi.

Koda taji shuru bai shigo ba, sai ta yanke shawarar   zuwa gurinsa, tunda zuwa yanzu ta san ya dawo, ita sam ba taga abun fushi da 'bacin rai ba,  bata gudin 'yan uwansa. halinsu ne kawai abun gudu.

Koda ta shiga gurin nasa,  Babu shi babu dalilinsa.  amma akwai alamun ya dawo yayi wanka sannan ga 'karamar wayarsa nan a saman drowar.

Kai tsaye gurinsu  Uwale ta nufa domin tana da tabbacin  yana can.

Abunda taci karo dashi ya kusa tarwatsa mata zuciya, amma sai ta jajurce! tayi kokarin danne mugun kishin da yake taso mata.. tayi musu sallama.

Su biyu ne a falon, Uwale na daki domin gabatar da sallar magariba, shima  dawowarsa kenan daga massalancin, ya samu Hamra'un ta shirya masa lafiyayyan towon farar shinkafa da miyar kubewa d'anya wacce taji bushashshen kifi da man shanu!

Ya dinga shi mata albarka domin yini cur  bai ci abinci ba, tun breakfast din safe,  b'acin ran da ya fita dashi ya ha nashi cin wani abu.

Tana zaune durshan a gabansa bayan ta zuba masa abincin yana ci tana bashi labarai sai dariya yake  sai kace mata da miji.

A zabure! ta kalli bakin kofar!  suka had'a ido, bahaushe yace (Mara gaskiya ko a ruwa gumi yake)  duk sai ta daburce! tayi gaggawar matsawa daga kusa dashi,   shi kam ko gezau! abincinsa kawai yake ci amma ya amsa sallamar bai dai kalleta ba.

Ta zauna kujarar dake kallonsa da fadin." Ranka ya dade ashe ka dawo."?

Ya dago kansa yana kallonta da mamakin sunansa da ta kira shi, sam bai mayi tunanin za tayi masa magana ba, saboda ya san  azabar kishinta.

Da yake Namijin duniya  ne babu kunya yace." Eh na dawo kina raina yanzu nake maganarki a zuciyata."

Taji kamar ta fada masa bakar magana! amma sai tayi shuru kawai tana masa wani irin kallo na tuhuma!

Saurin sunkuyar da kansa yayi! duk dadin towon a bakinsa yaji ya fice masa daga rai!

Hamra'u kam! simi-simi ta kama hanyar d'akinta! tana ta wani kumbura fuska shigowar Gimbiyar ya 'bata mata rai mutu'ka! domin ta katse mata jin dad'inta.

Ya kalleta da fadin." Ya zaki tafi baku gaisa ba.

Ya'ke  tayi ta juya da fadin." Aunty Gimbiya ina wuni."?

Tace." Lafiya lou ina Uwale."?  Kafin ma ta bata amsa Uwalen ta fito da carbi a hannunta,  ganin Gimbiyar yasa ta washe bakinta, sosai tayi farin cikin ganinta a zaune  babban burin ta ace Gimbiyar ta saki jikinta dasu.

 Hamra'u kasa tsayuwa tayi a gurin da sauri ta shige dakinta, ranta idan yayi dubu ya ba'ci, ita dai tana kishin yanda Uwale ke nuna kauna da kulawa akan Gimbiyar.

Cikin mutuncin da girmamawa suka gaisa da juna.

Ta kalleta da fadin." Ya jikin naki jiya Ai yake fada min kin 'kone a hannu har nake cewa zan shiga na dubaki Allah bai bani iko ba."

Tace." Ai ba sosai na k'one ba, kuma tunda yayi min addua gurin ya bushe ya daina ma zafi."

Tace." Duk da haka dai ai kin tsallake tsautsayi! kin ma yi kokari abunda ba ka saba a kansa ba, ai dole ka sha wahala."

Murmushi tayi amma ba tace komai ba.

Da farin ciki a maganarta tace." Mijinki ya sheda miki gobe za muje 'kauye ko "?

Fuska a sake ta amsa " Eh ya fad'a min Allah ya nuna mana goben lafiya."

Tace." Ameen  ai yana da kyau kema ki saba da dangi shiyasa da yace shi ba zai kwana ba, nace to ya zama dole ke ya barki tare damu domin 'yan uwa su sheda fuskarki ai riga an zama d'aya."

Tace." Hakan yayi insha babu matsala ta b'angare na,  ina tare daku."

Kallonta yayi yana mamakin furuncinta.

D'auke kanta tayi dan tunda suke maganarsu bata kalleshi ba saboda masifar haushinsa da take ji.

Uwale sarkin hira da labarai na ban dariya ta dinga bata labarai irin na da!  ta dinga dariya tana mamakin kokari irin na mutan da!  ace Mace ta haihu amma unguwar zoma ta fita yawan nama! ita abun ma dariya ya dinga bata.

Ganin kamar sun manta dashi a gurin yasa ya tashi domin zuwa ya kwanta a gajiya yake tilis!

Ta kalleshi da fadin." Ya zaka tashi kuma."?

Yace." Eh mana to zaman  me zanyi kun manta dani kuna hira bakwa sani a ciki zanje na kwanta ne."

Dariya tayi irin ta tsaffi! kafin tace." To ai gwara ka kwanta ko ka tashi da wuri nima nafiso muyi sammako."

Yana kokarin fita yace." Uwale ai ke yau bana tsammanin zaki iya bacci ."

Ta fashe da dariya da fadin." Me zai hana zanyi wanda ya sawwa'ka dai ai dole nayi zumudi UMARU wata da watanni ba tare da 'yan uwa ba." Da al'ajabi ta k'arasa maganar.

Girgiza kansa kawai yayi kafin yace.'' Sai da safe kenan ya kalleta bata da niyyar tashi su tafi......."A nan zaki kwana ne."?
Ya jefa mata tambayar hannunsa na rike da handle domin bude kofar.

A nutse ta mik'e ta kalli Uwalen da fadin." Sai Allah ya kaimu." Ta amsa da "To Allah ya tashe mu lafiya Alla ya bamu alkairi."
Kusan a tare suka amsa kafin ya bude kofar ya fita ta bi bayansa.

Kowa sashensa ya nufa, bata tsammanin bin sa domin yanda zuciyarta take a tunzure! bata tsammanin
zasu wanye lafiya. munufiki ne har yanzu akwai abunda yake 'boye mata.

Wanka tayi ta sanya kayan bacci tayi kwanciyarta tana tunanin irin hukuncin da za tayi masa cikin ruwan sanyi, abu d'aya za tai masa ya shiga damuwa! shine ta hana shi kanta wannan shine babban tashin hankalinsa, tabbas zai kawo kansa anan za ta fanshe in yaso yaje gurin yarinyar ta bashi kanta, tunda yana zuwa yaci abincinta a boye.

Washe gari da wuri ta gama shirinta sosai ta had'a musu tsaraba cikin baggo, sai da ta shirya tsaf sannan ta zauna domin karyawa.

Lokacin ya shigao cikin farar shadda kar! wando da riga iya gwiwa da wani irin tsadaddan aiki a wuyan rigar da hannu. yayi kyau sosai rashin sanya hula shine yai masa cikas, da alama bashi da ra'ayi ta sosai.

Ta kalleshi ta 'kara kallo, yana da kyau sosai sai yanzu take tantancewa dole mata su rikice a kansa, itama tana masifar sonsa saboda yana da baiwar da ba kowane namiji ne ke dashi ba.

Abinda take rayawa a kansa shima irinsa ne a zuciyarsa,  duk kwanan duniya  'kara sonta da kaunarta yake a zuciyarsa.

Sanyayyar ajiyar zuciya ta sauke kafin ta gaishe shi a sanyaye.

Babu yabo babu fallasa ya amsa yana gyara agogon sarkar dake hannunsa, yace." Har kin shirya kenan."?

Shuru tai masa bata ce komai ba. ta cigaba da kurbar tea din dake gabanta.

Saboda neman magana sai ya kai hannu yana so ya dauke cup din.

Ta kalleshi  da fadin." Ya haka kuma."?

Yace." So nake na sha."

Murmushi kawai tayi ta sakar masa cup din.....ya dauka ya kai bakinsa dai-dai bakinta ya shanye tas!

Ta yunk'ura ta tashi daga gurin.

Ya bi bayanta da kallo a lokacin da take kokarin shiga dakin, yawu ya had'iye ya lumshe idonsa! bayanta kad'ai ya isa ya gigita duk wani namiji lafiyayya dama mara lafiya.

Bayanta yabi jikinsa duk yayi la'asar!  ya same ta tana kokarin nad'a lifaya a jikinta.

Yaje gurin da fadin." Bakya jin zafi zaki nad'a wannan bayan kayan dake jikinki." Yana maganar yana ha nata abunda take.

Ta kalleshi da fadin." Zafi kuma."?

Kansa ya daga da fadin."Eh ana zafi a gari ko bakya jinsa ne."?

Ta san neman magana yake da ita kawai sai ta cire lifayar ta ajiye,  hijab ta d'auko amma bece komai ba. sai abun ya bata mamaki ganinta kamar a yanzu zai magana tunda a zahiri kamar hijab din zai fi lifayar zafi, amma bece komai ba sai aukin kallonta yake gabadaya kwayar

idonsa ta sauya!  ganin haka yasa da sauri ta kama hanyar fita tare da fadin." Wannan jakar baggo din ka fito da ita kaya ne a ciki."

Da hannu ta nuna masa, yabi gurin da kallo kafin ma yayi magana  ta fita daga dakin.  Zazzafar ajiyar zuciya sauke  kafin yasa hannu ya dauki bakkon ya bi bayan ta   da tunanin wani abu a ransa.

 *Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing,  idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:56 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176  domin karin bayani,  maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka   fara amfani da   maganin zaki ga sauyi,  domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari  2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita  kukan ki ya kare_

*GJSR*
*101&102*
Itace a kusa dashi, Uwale da Hamra'u kuma a baya a tsakaninsu suke hirar da ta shafe su, ita dai tayi shuru tana dai jinsu, gabadaya tunaninta ya ta'allaka ne gurin ganin  yanda za ta koyi mu'amula da 'yan uwansa, a jikinta takejin kamar akwai abunda zai faru sakamakon zuwanta garin.

Shi tunaninsa yasha bam-bam da wanda takeyi, domin shi kadai ya san halin damuwar da yake ciki a halin yanzu sha'awa ce tafi damunsa, gashi yayi wa Uwale alkawari yana ganin da kamar wuya alkawarin nan ya tabbata domin  tare da matarsa zai tafi, saboda samun saukin abinda ke damunsa.

Daga karshe dai shuru yayi musu ya daina sanya musu baki a hirar sai ya kasance su biyu kadai suke magana a motar yanayinsu ya nuna d'okin kasancewa da 'yan uwansu.

Daf da za su shiga garin ya kalleta, yaga duk tayi wani iri sai ya mutse fuska take, da alama akwai abunda ke damunta ta dai yi shuru ne kawai.

Sassauta murya yayi da fadin." Menene."?

Kallonshi tayi da gajiyayyun idanuwanta tace." Zuciyata ce take tashi!.

Yace." Saboda me."? shuru tai masa tana ganin ko ta fada masa dalili bai zama lallai ya yarda ba."

Yace." Ba zaki magana ba."?

Ta sauke ajiyar zuciya mai sanyi kafin tace." mybe tafiyar mota ne." Ta dan ja tsaki mtssw! kafin ta cigaba da cewa ."idan ba yau ba din ba, bana tsammanin na ta'ba dogowar tafiya a mota irin wannan."

Yayi shuru yana nazarin maganarta, kwarai hakan na iya faruwa idan anyi la'akari da irin gidan da ta fito mostly masu kud'in nan ba sa jurar tafiyar mota 'karamar tafiya sai hau mata jirgi.

Yace."Sannu ai mun shigo garin da ikon Allah."

Ba tace masa komai ba kawai ta jingina kanta jikin kujera tana sauke numfashi sannu a hankali.

Uwale ce ta iya tofa albarkacin bakinta a kan maganar amma Hamra'u ta tafas! ba tace ba, sai wani dauke kai take tana kumbura fuska.

Tunda suka shiga garin motar ta fara gargada tana ciccijewa sakamakon kwazazzabai da ramuka! bayan wannan yara da almajirai suka dinga bin motar da gudu suna ihu!!!!!!!

Al'amarin ya daure mata kai mutu'ka! ashe lalacewar 'kauyen har ta kai haka? ko'ina ginin jar kasa da wasu dirka-dirka bishiyon kuka da tsamiya had'e da mangaro gasu nan dai iri-iri! garin cike da dabbobi barkatai yaransu da manyansu cikin 'kazanta abun dai sai godiyar Allah.

Uwale sai wangale Baki take tana d'agawa yaran dake bin motar hannu, a tunaninta suna ganinta motar tintac ce ita take ganinsu amma su basa ganin na ciki, su dai farin cikinsu mota ta shigo garin.

Can wani fili mai yalwa ya nufa domin gyara parking.....Lokacin gungun! yaransa suka durfafo gurin suna bushe-bushe karnukan dake biye dasu na haushi gurin ya kacame! 'kura sai tashi

take!

Hankalinta ya tashi ganin haukan da yaran nasa suke! saboda haka yana gyara parking din ta kalleshi lokacin jikinsa har ya fara tsuma! gumi na karyo masa! tace." Dan Allah kada ka biye musu ina nufin kada kayi wannnan abun da kake bana so."

Zazzafar ajiyar zuciya ya sauke ya ciro hankici daga jikinsa gumin fuskarsa ya goge  kafin ya juya gurinsu Uwale lokacin tana ta kici-kicin bude kofar motar.

Ya mika hannu ya bude musu kofar suka fita........Karnukan suna hangoshi a motar sai suka sake rikicewa! da haushi kokari suke iske in da yake, ta rintse idonta da karfi tace." Kada bari su shigo ka rufe motar.

Gaggawar rufewa yayi yana kallonta jikinta sai karkarwa yake,  'kwalla ta cika kwarmin idonta, yana daya daga cikin dalilan da yasa bata kaunar zuwa k'auyen! ta tsani ta bude ido tayi tozali da k'azaman karnukan da idanuwansu ke cike da kwantsa.

Yace."Wai meye hakane? ki saki jikinki kina tare dani babu abunda za suyi miki."

Ta kalleshi hawayen bakin ciki na zuba tace." Ba zan fita a motar nan ba sai ka sallami wa'innan 'kazaman dasu da karnukansu bana  san ganinsu.

Yaji haushin maganarta amma sai ya basar!  kawai ya bud'e 'kofar ya fita.....aikuwa karnukan ne suka dinga tsalle suna rungumeshi! akwai  sabo mai tsanani a tsakaninsu.  takaici da bakin ciki ya ishe ta, kullum yana kiran kansa musulumi amma yana tu'ammali da karnuka wanda kowa ya san hakan haramun ne a musulunci.

Alba ya kwance masa bakin wani kuttu dake cike da tsumi!!! sai kumfa yake!!  ya kafa kansa ya dinga kwankwad'a!! yana wata irin girgiza!

Gurin cika yayi manya da yara duk sun kewayeshi alamu dai sun nuna jama'ar garin suna alfahari dashi.

Duk bada'kalar da take faruwa tana kallo, duk rokon da tayi masa hakan bai sa ya fasa abinda yayi niyya ba,  kafaffar wu'ka  gayawa jini na wuce!  ya kar'ba a hannun Alba tana walwali  ya fara dadurawa! a wuyansa!  anci sa'a  wannan karan bai cire rigarsa ba.  ya kai minti goma yana gurzawa wu'kar! kafin ya kurma! uban ihun! da ya sanya gurin amsawa!  ya fara kai kawo a gurin  yana dukan kirjinsa!

Takaici yasa kawai ta sunkuyar da kanta 'kasa bata tsammanin zata iya cigaba da kallonsa yana

wannan halin.

Farar shaddar jikinsa ta rine! tayi jajawur!  ta jike da gumiin jikinsa! hatta! da gashin kansa digar da gumi! yake!

Kawu Ado ne yayi namijin tunkarar gurin da yake!  yana kokarin rike hannunsa yana fizgewa! jin karfi kawai yake yana wani tattaune bakinsa, su kuma yaran sai kara kambaba darajarsa suke suna 'kara tayar masa da tsumin da yake jikinsa.

Maigari da jama'arsa suka 'karaso gurin domin suna zaune a fada labari ya samesu cewa *GOJE!* ya shigo garin.

Maigarin ya samu nasarar isa gurin da yake......Kawu Ado ya rufa masa baya. dukkaninsu *mubaya* (goyon baya)  sukayi kafin ya sadadu!  Maigari da Kawu Ado hannu na dukan hannu 💪🏻suke masa kirari! *Cau!! Sa'a dai!! Mai maganin wuka da kaho."!!* ire-iren wannan kirarin suka dinga yi masa kafin su samu kansa!  jagab!  ji'ke da gumi suka rirrik'eshi domin shiga dashi cikin gidan.

 Cikin uwar dakin Uwale Kawu Ado ya zaunar dashi, kafin ya fita ya sallami yaran nasa da har yanzu ba su daina bushe-bushe da buga gangani ba, garin duk ya hautsine! sai kace wani babban basarake ne ya sauka.

Da sauri- sauri yake sauke numfashi makogwaronsa sai suya yake, a maimakon yaji sha'awar ruwan sanyi amma  abun mamaki a lokacin babu abunda yake bukata face hayakin Sigari ko shisha duk dai wanda ya samu.

Sai da ya dan samu nutsuwa tukkuna ya fito, aikuwa ya tarar tsakar gidan cike da mata 'yan uwa da kuma abokanar arziki.

Kaf ya dube gurin babu ita babu dalilinta.

Gabansa ya fad'i!  ya kalli Uwale da fadin." Ina Zinatu."?

Tace." Umaru ai kai zan tambaya ni da na barka tare da ita a mota."

Ba tare da ya sake wata magana ba ya kama hanyar fita......matan dake tsaitsaye a gurin sai gaisheshi suke da kyar yake iya amsawa,  gabadaya hankalinsa na gurinta.

Tunda ta hango fitowarsa daga gidab ta dauke kai tare da jan tsaki! cikin ranta take ayyana

wasu abubuwa a kansa.

Ya bud'e motar idanuwansu  suka had'u!   bai ta'ba jin kunyarta ba irin yau!

Yayi saurin janye idonsa yana dawurwura domin ya ma rasa me zai ce mata.

Ganin haka ya sanya kawai ta girgiza kanta ta fara kokarin fitowa daga motar. ya dauki handbang d'inta ya rike yana gyara mata hijab din dake jikinta.

Cikin gajiya ta fito daga motar tana dudduba gurin.

Ya rufe motar da fadin.'' Muje ko."?  Gaba yayi tabi bayansa kamar bata son taka 'kasa.

Handbag din ya mika mata da fadin." Ki shiga zan shigo yanzu."?

Kallonsa tayi na minti biyu kafin ta girgiza kai da fadin." Ni ba zan shiga ni ka d'ai ba."

Bai ce mata  komai ba ya koma gurin motar ya bude ya dauko Shishar sa dake cikin kwali! ba ta gane komeye ba amma tana ta kallonsa gami daso ta hasaso abunda yake cikin kwalin.

Ido ne yayi caaaaa!  a kanta yayin da suka shiga gidan......Wa'inda basu santa ba tambaya kawai suke "Wannan ce matar UMARU."? Uwale na basu amsa daidai da abunda suka tambaya.

Ita dai kasa tsayuwa tayi kawai tabi bayansa dakin da taga ya shiga.

Hamra'u na dakin sai share-share take.......Yanayin dakin ya nuna nasa ne tun lokacin samartaka  duba da irin tarin kayan farauta da suka rataye a bagon  dakin da kuma tarin buhun-buhun magungunan gargajiya irin wanda yake bayarwa.

'Kura duk ta tashi a dakin sakamakon rashin gyaran da bai samu ba tsayin watannin da suka wuce.

Taja ta tsaya bakin k'ofar tana mata wani irin kallo,  wallahi bata ta'ba ganin mara zuciya irin ta ba, kullum cikin bautar namijin da babu guarantee akansa.

Ganin yaki mata magana yasa ita ta magantu tace." Kin ga ya isa haka don Allah! mutumin da ba zama yazo ba meye zaki damu kanki gurin gyara masa daki, ko kin manta yau zai tafi."

A sanyaye  Hamra'un ta kalleshi wai ko zaiyi magana, Uffan bece ba shima so yake ta fita ya

samu sararin busa hayak'insa.

Jiki babu kwari tazo za ta wuce da tsintsinya a hannunta, hanya ta matsa mata har yanzu kallon shashasha take mata, to idan ba haka ba akan me zata dinga wahalar da rayuwarta.

Ta fita daga d'akin ya fito da shishar ya fara tada hayaki!

Ta kalleshi da fadin." Ni ce marainiyar wayonka ko."?

Ya kalleta tare daso tayi masa karin bayani.

Murmushin takaici tayi kafin tace." Ka b'oye ashararanci da kake a idon duniya saboda gudun abun magana amma da yake ni ka mayar dani towon tushe baka jin kunyar aikata abu mara kyau a gabana."

Ya fesar da hayakin dake bakinsa kafin yace." Kwalbar giya ki ka gani a hannuna."?

Tayi shuru tana kallonsa

Yace." Wannan da yake  hannuna! bashi da lada ko zunubi!  sanya kai ne ga wanda yake da ra'ayi kuma bana sha sai irin haka ta faru, ko kin ta'ba tsintar karan Sigari a aljihun rigata."?

Ba tace komai ba tana dai ta nazari da tunani a kansa.

Yayi murmushi da fadin." Ko kin manta kalmar da take cewa (Mata sirrin miji) kece sirri na kuma ina da ta tabbacin cewa duk rintsi duk wuya zaki rufa min asiri a kowane hali, akwai bambanci sosai a tsakaninki da Hamra'u."

Maganganunsa suka kashe mata jiki, ta dinga kallonsa tana sake jin kaunarsa na ratsa sassan jikinta.

Da hannu ya nuna mata kusa dashi da fadin." Zo ki zauna kusa dani  sanyin idanuwana."

Murmushi tayi kafin ta nufi gurin ta zauna kusa dashi da fadin ." Dubi jikinka yanda ya 'baci! kayi wani dukun-dukun! sam wannan rayuwar ba ta dace da kai ba."

Ya ajiye abunda ke hannunsa gabadaya ya mayar da hankalinsa kanta,  yace." *ZINA* ina so ki fahimci wani abu,  wannan abun fa ya kai matakin da ba za'a iya raba ni dashi ba,  ya riga ya zama jiki da Jinina! duk sanda  tsumin ya tashi bana iya sarrafa kaina,  tun ina yaro nake shan magungunan tauri! a cikin dabbobin da Allah ya hallita masu rai kad'an ne ban ci ba. nayi gwagwarmaya da jinsi mutum da aljanu domin har so sukayi su bude min ido! ni ne ban bada goyon baya amma duk da hakan wani lokacin idan sun so suna ziyartata muyi hira su tafi salin alin ba tare da sun cutar dani ba.... babu tabbas akan aljani kuma ba'a yarda dasu amma ni bana tsammanin cewar zasu cutar dani da duk wanda ya shafe ni, dalili musulmai ne kamar yanda nake musulmi saboda haka ki kwantar da hankali kisa a ranki cewa ni ne abokin rayuwarki."

Gabadaya jikinta ya mutu jin abinda yake fada........Dama ta jima tana zarginsa cewa bashi kadai yake rayuwa ba akwai masu taimaka masa.

Ta rasa wane irin tunani za tayi a kansa.

Yace." Bayan sallar la'asar za mu tafi gida bana tsammanin barin ki a garin nan."

Wani bala'in dadi y rufe ta, amma bata nuna masa ba tace." Saboda me."?

Shu'umin kallo yayi mata kafin yace." Ba zan iya bacci ba yau saboda sha'awar dake damuna kwana biyu kina fushi dani kin daina kwana a dakina."

Sunkuyar da kanta tayi tana wasa da yatsun hannunta.

Hannu yasa ya daga fuskarta,  wanda yayi daidai da shigowar Hamra'u dakin tana sheda masa ruwan wankan data dora masa yayi zafi."

Hankalinsa gabadaya yana kan matarsa ya amsa da" Okey to na gode kanwata."

A sanyaye ta saki labulan d'akin,  zuciyarta kamar ta fashe sakamakon abunda ta gani a tsakaninsu.

Yana fitowa daga wankan Uwake ke sheda masa cewa Kawunan sa suna son ganinsa......Yace." Babu damuwa yanzu zai shirya yaje ya samesu.

Ya shiga dakin ya sameta a kwance saman katifarsa sai juye-juye take cikinta ne yake ciwo  ga yunwa na damunta.

Cikin kulawa yace." Zina akwai abunda ke damunki amma idan na tambayeki sai kice babu komai."

Tana ya mutse fuska tace." Ciki na ne yake ciwo idan ba amai nayi ba to  ba zan ji dadi ba.

Girgiza kansa yayi da fadin." Sannu Allah ya sawwake me kike bukata idan na fita na kawo miki kin san  muna da komai na gargajiya."

Tace." Goba da mangaro amma irin wa'inda basu nuna ba."

Yace." Shikkenan."?  shuru tayi na minti biyu kafin tace." Meye ma sunan abun."?

'Yar dariya yayi kafin yace." Agwalima kuke ce masa ko."?  tace." Yawwa dashi da kuma Magarya."

Yace." An gama ranki ya dad'e! amma gyad'a marau-marau fa."

Dariya ya bata kafin tace." Ina so."  Yace." To insha Allah zan kawo miki, ki kwanta ki huta yanzu ni zanje gurin. Iyayana suna nema na.".

Tace." To babu damuwa a ce ina gaishesu."  Yana kokarin fita ya amsa da zasuji insha Allah."

Yayi wa Uwale sallama lokacin tana kicin tana aikin soye-soye......da yake  tana da irin kaji na hausa wanda take kiwo a can baya, sai ta bar su a hannun Tasallah shine fa  tasa aka yanka mata guda biyar aka gyarasu tsaf ta kawo mata tare da duk abun bukata...

 *Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing,  idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:56 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176  domin karin bayani,  maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga

ranar da ki ka fara amfani da maganin zaki ga sauyi, domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari 2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*103&104*
Su biyu ya same su zaune a cikin rumfar kwanon dake k'ofar gidan Kawu Adon, a nutse ya cire takalmansa kafin ya hau kan tabarmar ya zauna cikin girmamawa suka gaisa da juna tare da tambayar bayan rabuwa.........Kawu Haruna yace." Bayan rabuwa sai alkairi Umaru abubuwa da yawa sun faru masu dadi da marasa dadi sai godiyar Allah dama kuma haka duniyar take yau da gobe duk na Allah ne."

Yace." K'warai hakane Kawu Amma naji dadin ganinku cikin koshin lafiya babu wata matsala wannan ne dalilin da yasa hankalina ya kwanta sosai dan idan ba dole ba, babu yanda za'ayi nayi nesa daku to kana taka Allah na tasa tabbas hukuncin da Allah ya zartar shine dai-dai."

Kawu Ado yace." Umaru mu ai hakan abun alfahari ne a gare mu, domin ka fita zakkah a cikin mu, nasan yanzu da yawa wa'inda suke zagin ka a baya jikinsu yayi sanyi domin bahaushe yace (Dan hakin daka raina shike tsone maka ido) kuma Ubangiji na saukar da ikonsa sai dai kallo, shiyasa idan kaga wani yana aikata kuskure babbah ko yaro ta kafadi alkairi ko kuma kayi shuru, jama'a da yawa sun kasa gane hakan, sai sanda Allah ya saukar da ikonsa tukkuna, saboda haka ka daina damuwa wai dan kayi nesa damu hakan ne alkairi a gare mu bakidaya."

Cike da jin dadin maganar yace." Masha Allah Kawu Na gode kwarai da addua da kuma fatan alkairi Allah ya kara girma."

Suka amsa da "Ameen." kafin gurin ya dauki shuru na 'yan mintina.

Ya dan gyara zamansa da fadin." Uwale ce ke sheda min cewa kuna nema na."

Gyara zama yayi tare da gyaran murya kafin yace." Mak'asudin kiran akan wannan yarinya ne Hamra'u! kwanakin baya mahaifinta ya sameni da maganar muka tattauna kuma ya fahimce ni sosai amma na sheda masa cewa sai kazo tukkuna za'a tsayar da magana."

Yayi shuru yana nazarin maganar...sam! baya san gaggawa acikin al'amarinsa, amma yana ganin dole ya amince musu dalili bashi da kwakwkwaran hujjar da zai bayar.

Ya sauke ajiyar zuciya da fadin." Ni kaina al'amarin yana damuna, kuma na san da yawa daga

cikin mutanan gari sun dauke ni kamar mara amana da cika alkawari!  tabbas Allah ke tsarawa bawa rayuwarsa amma a mafarki banyi tunanin auran wata mace bayan Hamra'u ba, akwai abinda Allah yake nufi da faruwar hakan, saboda haka yau  nake da niyyar komawa bakin aiki amma zan bar komai a hannuku duk abunda ya kamata ayi  na neman aure a tabbatar an gabatar zan turo kudin hidima da sauransu idan yaso sai a tsayar da lokaci."

Gabadayansu farin ciki ya lullubesu dama babban burinsu ace yaron ya dawo gida yayi aure, domin auran da yayi a baya sam bai kwanta musu a rai ba  sai kuma gashi had'uwarsu ta farko da sukayi da yarinyar ta nuna k'yama! a garesu wannan shine dalilin da yasa gabad'aya suka d'ora mata karan tsana basa kaunarta ko kad'an.

Kawu Haruna yace." Allah yayi maka albarka Umaru  yanda kayi mana biyayya Allah ya azurtaka da yaran masu albarka, Allah ya jikan mahaifinka yayi masa gafara."

Ya amsa da "Ameen ya Allah Kawu Allah ya saka da alkairi."

Kawu Ado yace." Yanzu kai ya kamata ka tsayar da lokaci domin mu shedawa mahaifin yarinyar."

Yayi jim!  yana nazari kafin yace." Shekara guda yayi."

Kawu Haruna yace." Haba Umaru wane irin shekara kuma? me ka nema ka rasa da har zaka ja lokaci haka."

Shuru kawai yayi yana kallonsa shi a ganinsa shekarar shine dai-dai lokacin matarsa ta haihu hankalinsa zai fi kwanciya baya so yanzu ta samu labari matsala ta afku.

Kawu Adon yace." Kayi shuru kana tunani Umaru ka duba lamarin nan da kyau."

Yace." Kawu akwai dalilin da yasa nace a sa shekara guda domin iyalina na da juna biyu  kasan mata da kishi bana so wata matsalar ta biyo baya idan ta samu labari."

Kawu Haruna ya 'bata fuska tsanar yarinyar ta sake nunnukuwa a ransa  yace." Umaru na dauka ai tuntuni ka shedawa matarka tsakaninka da yarinyar nan Hamra'u, ai bai kamata kaja bakinka kayi shuru ba tunda tilas ta san ba zata zauna ita kad'ai ba."

Ya tsirawa Kawun nasa ido yana mamakin furucinsa.....Idan ban da kaddara baya tsammanin kara aure domin bai tashi da ra'ayin haka ba, mace daya ta isheshi rayuwa mutukar ta cika

abunda yake bukata,  amma yanda ya tsara rayuwarsa ba haka Allah ya tsara masa ba, wannan shine dalilin da yasa yake mamakin furucin kawun nasa.

Kawu Haruna yace." Wata shida za'a sanya  shine dai-dai."

Yace." To shikkenan Kawu Babu damuwa Allah ya tabbatar mana da alkairi."

Gabad'aya suka amsa da "Ameen ya Allah."

Ya d'an gyara kafin yasa hannu cikin aljihu ya fito da kudi  'yan dubu-dubu saffi kar guda ashirin ya ajiye gabansu da fadin." Ga wannan babu yawa bayan haka akwai kayan abinci a can gidan Uwale  idan na koma yanzu zan sanya yara sukai gida."

Suka dinga godiya suna shi masa albarka gabadaya bakinsu yaki rufuwa sai fatan alkairi suke masa.  sallama yayi musu kafin ya bar gurin cike da tararrabi da damuwar abunda zai biyo baya.

Kawu Ado ya shiga gidansa bakinsa kamar gonar audiga.

Matarsa Taburni tana tsintar shinkafa ta kalleshi tana mamakin annushuwar da ya shigo dashi gidan

Kusa da ita ya zauna da fadin." Kina da labarin zuwan Umaru ko."?

Tace." Eh na samu labari a bakin yara Allah yasa da alkairi yazo mana."

Ya fito da sabbin kudin ya ajiye a gabanta, ta dauka tana lissafawa ta kalleshi da fadin." Dubu goma ne."

Yace." Kwarai kuwa haka ya bani ya kuma bawa Haruna sannan yace yanzu zai turo mana da kayan abincin.

Ta washe baki da fadin."  Kai masha Allah ashe yau za muyi miya da nama! mun gode sosai Allah ya saka masa da alkairi."

Ya amsa da "Ameen yana tattara kan kudinsa yasa a aljihu da fadin."  Bayan haka kuma mun tsayar da magana wata shida masu zuwa za'a daura auransa da Hamra'u  'yar gidan 'kawarki

'Dayyiba.

Taburni ta rangad'a bud'a farin ciki kamar ya kasheta tace." Lallai Allah yayi aure da mara kwabo!  yanzu kuwa zan je na shedawa kawata halin da ake ciki."

Yace." Ai yanda na lura da yaron kamar yana tsoron matarsa ne idan ba haka ba mai zai sanya yace sai ta haihu sannan za'ayi maganar aure a take a gurin  Haruna ya nuna masa fushinsa.

Taburni ranta a bace tace."Au! ciki ne da matar tasa."?

Yace." 'Kwarai kuwa ciki ne da ita har yayi kwari mana."

Taja tsaki da fadin."  Hegiyar   yarinya mara mutunci  ai duk sanda na tuna abunda tayi mana sai raina ya 'baci! bana k'aunarta ko kad'an ."

Yace." Duk cikinmu babu mai k'aunarta! wannan ne dalilin da yasa muke so yayi auren cikin gida domin mu samu wacce zata mutuntamu ta kuma daraja mu."

Tace." Wannan shine gaskiya, naji dadin faruwar wannan al'amarin,  Allah kuma ya tabbatar da alkairi."  Ya amsa da "Ameen." Yana kokarin kishingida a gurin.

Ita kuwa da sauri ta tashi ta fara aikace-aikacen ta tana Allah-Allah ta kammala taje ta shedawa 'Kawarta albishir mai dadi.
Da wata iriyar kasala ya koma gidan, gabadaya kansa ya daure ya rasa wane irin tunani zai yi.

Bacci take sosai  duk gumi ya ji'kata! da sauri ya dage labulan ya dora saman 'kofar dakin,  kai tsaye  dakin Uwale ya nufa ya samo mafici ya fito wanda yayi dai-dai fitowarta daga kicin,  ta kalleshi da fadin." Har ka dawo."?

Yace." Eh yanzu nan na shigo Zinatu taci abinci."?

Tace." A'a ai bayan fitarka  na leka dakin sai na sameta tana bacci, shine dalilin da yasa ban tasheta ba.

Yana kokarin barin gurin yace." Yanzu zamu shirya tafiya insha Allah."

Kallo ta bishi da kallo tana mamakin maganarsa.

Rigar jikinsa ya cire ya zauna kusa da ita tare da kokarin cire mata rigar jikinta.

Ido ta bud'e cikin alamun bacci take kallonsa. sai ta fara kokarin tashi zaune.

Ya taimaka ta tashi  burinsa kawai ya rabata da rigar saboda gumin da take.

Ha nashi tayi domin tsarguwa tayi ganinsa babu riga sai take tunanin wani abu zai yi mata.

Da ya fuskanci haka sai ya girgiza mata kai da fadin." Babu abunda zanyi miki ki cire rigar saboda zafi.

Ajiyar zuciya ta sauke kafin ta fara kokarin tashi........hanyar fita ta nufa ya bita da kallon mamaki!

Bandaki ta shiga ta kama ruwa kafin ta fito ta daura alwala.

Uwale ta fito daga kicin hannuna rike da farantin  silba da kwanukan abinci a jere, ta kalleta da fadin." Kin tashi kenan."

Murmushi kawai tayi ba tare da tace komai ba ta fara kokarin kar'bar kayan abincin.

Ta janye da fadin." A'a ki bar shi na k'arasa lada na mana."

Murmushi tayi tana kallonta, hakika matar nada kima da daraja a idonta.

Ta ajiye Tire din da fadin." Umaru ashe sai da ka tashi yarinyar nan ."

Yace." Uwale tashin shi yafi alkairi  tayi sallah ta kuma ci abinci  domin mu dauki hanya da wuri.

Tace." Tun dazu kake magana a 'boye  me kake nufi ne."?

Yace." Uwale kiyi hakuri tare zan koma da ita."

Ta 'bata rai da fadin." Okey ta saka ka a d'aki  ta nuna maka rashin yarda ta kenan."
Maganar tayi dai-dai da shigowarta dakin.

Itama Uwalen sai da ta fadi maganar sannan kuma tayi dakace.

Yace." Ko d'aya kawai nayi wani tunani ne, shiyasa na sanja shawara."

Ba tace komai ba ta kama hanya ta fita ranta a 'bace!

Tana idar da sallar ta kalleshi da fadin." Ka bari kawai zamu dawo tare dasu kayi tafiyarka."

Yace." Saboda me?  shin kin san damuwa da nake ciki kuwa."?

Tace." Kayi hakuri ka danne damuwarka duka kwana nawa za muyi zamu dawo."

Shuru kawai yayi mata a ransa sam beso hakan ba dan dai sun fi karfinsa ne.

Tare suka ci abincin sai jifanta yake da wani irin kallo na mussaman wanda ya kashe mata jiki babu shakka akan ga'ba yake  tana jin tsoron suyi abun kunya.

Aikuwa dai  abunda yake shirin faruwa kenan,  dan fafur!  yaki tafiya lokacin yayi kwanciyarsa sai bayan da ya biya bukatarsa tukkuna!  kunyar duniya ta isheta, ba ta iya wanka a lokacin ba sai da ta tabbatar cewa duhu yayi sannan ta tsarkake jikinta ta gabatar da magariba da isha'i......Lokacin shi kuma ya gama shirin tafiya.

Zuciyarta ce ta karye ta kasa kallonsa sai kokarin mayar da hawaye take.

Koda ya fuskanci halin da take ciki sai ya rungumeta yana rarrashinta......Yanzu bashi da damuwa tunda ya kawar da abunda ke damunsa.

Sosai ta b'oye damuwarta duk dan kada  Uwalen ta fahimci wani abu ta saki jikinta sosai! suka dinga hira a tsakaninsu. Har take tambayar Hamra'u, nan take sheda mata cewa ta tafi gidansu a can zata kwana.

Allah sarki Uwale mace mai karamci da kanta ta gyara mata shimfida sabon zanin gado ta shimfida akan gadon katifar audigar  dake  shimfide akan gadon karfenta irin na mutan da ,  ta kunna mata turaran wata na tsinke! dakin ya dinga kamshi mai dadi,  bata kwanta ba sai da tayi wanka tukkuna ta sanya wata doguwar riga cotton mai tausa sai tasa hula da yake duk tayi gurizin abinda zata bukata....Sosai taji dadin kasancewarta a d'akin, tayi kwanciyarta kan lallausar katifa iskar hadari na kad'a labulan dakin.

Mijinta kawai take gani a lokacin da idonta yake lumshe, ta kira wayarsa ba adadi taki shiga da alama  gidan bashi da network ko kad'an ! gabadaya ta shiga damuwa, muryarsa kawai take bukatar saurara a kunnanta.

*Ayi hakuri da rashin posting akan lokaci wallahi  kanwata ce za tayi sauka al'kur'ani Gobe🙏🏻*

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing, idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:56 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176 domin karin bayani, maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka fara amfani da maganin zaki ga sauyi, domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari 2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*105&106*

To shima nashi 'bangaran abinda yake faruwa kenan, domin tun bayan ya sauka gida yake kiran wayarta abun ya gagara, da ta fara shiga sai ta katse ya kira ya kai sau goma bai samu biyan bukata ba, sai kawai ya ajiye wayar ranshi gabadaya a 'bace yaso kafin ya kwanta yaji lafiyarta da ta babynsa dake kwance a cikinta, haka kawai yake tausaya mata, ya san duk wani abu da take daurewa take akan ta nuna masa kaunar 'yan uwansa, kuma abunda tayi ya siya mata kima da daraja a idonsa, ya sake jin sonta ya k'aru a zuciyarsa.

Da tunaninta ya kwana ya kuma tashi dashi, wannan dalilin ne yasa yana dawowa daga massalaci ya dauki wayarsa ya kunna, ya fara laluben number ta, cikin ikon Allah sai ta kira shi, a jiyar zuciya ya sauke mai sanyi kafin ya sanya wayar a kunnansa da sallama a bakinsa.

Ta amsa a sanyaye tana dan gyara kwanciyarta, yace." My GIMBIYA fatan kin tashi lafiya ya kwanan bakunta."?

Tace."Lafiya alhamdullihi na kwana da tunaninka da kewarka rashin kwanciya a kirjinka ya janyo min ciwon jiki."

Ya lumshe ido yana jin wani feeling na taso masa yace." Me yasa ki ka takura kanki lallai sai kin kwana umm? saboda na san hakan zai faru ya sa na sauya shawara, yanzu na gamsu da kaunar da kike a kaina da family na.

Sanyayyar ajiyar zuciya ta sauke kafin tace." Nifa ba'a takure nake ba, domin yanayin garin ya burgeni sosai  da zamu dawo garin da zama da hakan yayi min dadi." Tafad'i hakane kawai ba har can cikin zuciyarta ba.

Aikuwa yaji dadin maganar yace." Tunda yanayin garin yayi miki dadi zamu dinga zuwa hutu ko? zan gina miki gida mai kyau."

Tayi 'yar dariya da fadin." Naji dadin hakan mijina."

Yace." Ya babyna ina fatan yana lafiya."?

A shagwabe tace." Jiya tun bayan da kuka gaisa dashi ya dameni da k'iriniya  sai motsi yake min."

Dariya yasa da fadin." Yana bukatar mu sake gaisawa sosai dan jiya baki sakar min jiki mun gaisa yanda ya dace ba, amma ki bashi hakuri kafin mu had'u."

Itama dariyar take kafin tace." Aa ni babu ruwana idan kun had'u sai ka bashi hakuri dan da alama yayi fushi tun wayewar gari beyi motsi ba."

Gabansa ya fad'i!  da sauri yace." Beyi motsi ba fa ki kace."?

Ta dora hannunta a saman cikin tana shafawa kafin tace." Eh mana ya tattara a guri daya kamar bashi da lafiya."

Gabad'aya yaji hankalinsa ya dawo garin yace." Ganin tafe insha Allah."

Da sauri tace." Laa da wasa fa nake maka."?

Ya 'bata rai da fadin." ZINAT an ta'ba wasa da lafiya ashe.'?

Jin yanda yayi maganar babu wasa yasa ta zama serious  tace." Allah tsokanarka nake yanzu haka ma motsi yake yaji muryarka."

Ajiyar zuciya ya sauke da fadin." Saboda kin ga na damu shiyasa zaki mayar dani shashasha ko."?

Kunshe baki tayi tana danne dariyar dake kokarin subce mata, tace." Kayi hakuri Darling."

"Um-um! naki hakurin." Cikin shagawaba yayi maganar.........Tace." Dan Allah fa."

Yace." Nayi amma kada ki sake min wannan wasa hankali na ya tashi wallahi."

Tace." To ba zan sake ba insha Allah."

Yace." Uwale ta tashi."?  tace." Eh tana kicin tana aiki."

Yace." Idan babu damuwa ki kai mata wayar mu gaisa."

Tace." To insha Allah bari na kai mata."

Cikin jin dadi yace." Allah yayi miki albarka."

Ta amsa da "Ameen tana kokarin tashi tsaye.

****

Hamra'u da kanta ta shirya abincin ta zuba cikin kwanuka masu kyau ta jera kan tire kafin ta nufi bandaki a gurguje ta shiga wanka.

A lokacin ne mahaifiyarta Dayyiba ta samu damar aikata mugun nufin ta.

Ko kafin ma Hamra'un ta fito daga bandaki har ta sanya k'aramin   d'anta ya dauki tiran dake dauke da abincin sun fita a tare.

D'aya da rabi na rana Uwale na aiki a kicin  Dayyiba tayi sallama a gidan.

Uwale ta amsa ta fito daga kicin din tana mata barka da zuwa,  kai tsaye daki suka nufa.

Suka fara gaisawa tare da tambayar bayan rabuwa.....Dayyiba tace." Ai da wuri yau na gama abinci nace bari nazo mu gaisa na kuma ga matar Umaru kin san dama ni ban ta'ba ganinta ba."

Uwale tace." Allah sarki sannu da kokari Dayyiba har da wahala haka to mun gode sosai."

Tana murmushi tace." Babu komai Dambu ne na turara mata na san masu ciki da kwad'ayi watakila yayi mata dadi."

Tace." Eh 'kwarai kuwa, bacci takeyi yanzu amma bari na leka na gani ko ta tashi."

Lokacin da ta shiga dakin zaune ta sameta a bakin gado tun bayan shigowar Dayyibar ta tashi duk tana jin maganganunsu.

Tace." Ashe kin tashi dama mahaifiyar Hamra'u ce tazo ku gaisa ta kuma kawo miki abinci."

Tace."Allah sarki amma na gode sosai bari na fito mu gaisa."

Ta juya da fadin." To bari na sheda mata."

Shuru tayi tana nazarin al'amarin, mahaifiyar Hamra'u? ita sunan yarinyar ma bata kauna ballantana wanda ya danganceta.

Ajiyar zuciya ta sauke kafin ta tashi da k'yar! yunwa sai sasakar cikinta take, abun goge baki ta dauko cikin kayanta.

Koda ta fito bata zauna ba tukkuna sai da ta wanko bakinta ta dauro alwala sannan ta dawo dakin.

A nutse ta zauna kusa da Uwale ta kalli Dayyibar dake mata wani munafikin kallo tace." Ina wuni fatan mun sameku lafiya."?

A firgice ta amsa da fadin." Lafiya lou muke ya mutan gida da can gurin manyan."

Tace." Duk suna nan lafiya lou."
Daga haka sai ta kawar da kanta tana nazari akan matar kamar mara gaskiya.

Uwale ta bud'e kwanunkan abincin da fadin." Dambu ne ko kina sha'awa."

Kamshi ya bugi hancinta Dambun ya hadu yaji gyada da zogale ga k'amshin man gyada ziryan yana tashi...........Tunda take sau biyu kacal ta ta'ba cin irin wannan abincin, shima kuma irin na shinkafa bana masara ba , wannan dalilin yasa gabadaya ta rikice yaron dake cikinta ya nuna kwadayinsa akan abincin .

Ta kalli Dayyibar da fadin" Na gode sosai."

Tana washe baki ta amsa da babu komai dan nayi miki hidima kamar 'yar cikina kike."

Murmushi kawai tayi ta kalli Uwale da fadin." Nayi sha'awarsa.".

Uwale tasa dariya da fadin." Ai dole  ni kaina ya bani sha'awa ballanatana ke da kike da lalura."

Dayyiba ta dinga dariyar farin ciki  tace." Ai kin san Hamra'u ta gwane gurin iya abinci gargajiya dama na turawan kowacce mace tana da baiwa,  amma tabbas duk macan da ta iya girki zata samu soyayyar mijinta.

Ba ita Zinat din ba har   Uwale sai da taji babu dadi da maganar Dayyibar dan kamar maganar tayi kama da habaici.

Babu dai wanda yayi magana a cikinsu,  ta zuba mata a ma daidaicin  plate.  tayi bisimillah ta fara ci a nutse ba ta tunanin komai a ranta.

 Sosai dambun yayi mata dad'i,  tas ta cinye wanda yake gabanta. a cikinta tana jin k'oshi amma a bakinta ba ta gaji ba, haka dai tayi kawaici tasha ruwa.Uwale ke tambayarta, tace." A yanzu dai ta koshi sai zuwa an jima tukkuna."

Dayyiba mahaifiyar Hamra'u zuciyarta fes!  ta fita gidan, babban burinta cikin ya zube ko kuma Gimbiyar ta galabaita.

Aikuwa dai jikinta ne ya mutu kasala ta dame ta, sai kawai taje ta kwanta tana ya mutse fuskarta cikinta ne yake hautsinawa zuciyarta na tashi.

Minti ashirin da kwanciyarta ta tashi a gigice! sakamakon jin wani irin mahaukacin amai da yake taso mata.

Bakin rariya ta gurfana ta dinga sheka aman tana rike kirji!

Uwale hankalinta ya tashi ganin mawuyacin halin da Gimbiyar ke ciki.

Ta rike ta tana mata sannu a lokacin kanta ya dinga juyawa tayi kwance a gurin tana mayar da numfashi.

Uwale tace." Sannu ki daure ki tashi ki koma daki ki kwanta a can kinga nan akwai rana gaki a bakin kwata a kwance."

Shuru tayi ba ta iya cewa komai ba, gabadaya ma bata cikin hayyacinta,  tana jin yanda cikinta

yake kartawa! wannan karan ba amai takeji ba zawo!  ne mai karfi yake kokarin kwace mata.

Kokarin tashi take domin shiga bandaki abun ya gagara domin gabadaya jikinta ya shika babu kwari!  duk yanda taso da ta daure ta kasa ba ta ma san lokacin da zawon ya kwace mata ba, kawai sai tsuuuuuu!  ta dinga jin fitarsa kamar an kwance famfo.

Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un!  shine abinda Uwale take nanatawa.

(Cutar a mai da gudawa!)  ya kama 'yar mutane! cutar dake saurin halaka mutum,  hankali a tashe ta nufi gidan Tasallah.

Suka shigo tare  lokacin gudawar sai bin rariya take ita kuma tana kwance a gurin sai matagugu take domin wani masifaffan ciwo cikinta yake mata.

Tasallah tayi salati tana sanar da Ubangiji kafin tayi azamar fita, gidanta ta koma  da yake akwai magungunan gargajiya da take aje dasu,  ta daga karkashin gadon karfenta ta dauko ledar maganar duk tayi kura da dauda!   da yanar gizagizo ajikin ledar ta dauka ta fita.

Aje ledar tayi a gefe ta taimakawa Uwalen suka fara gyarata,  idonta a lumshe yake amma duk tana jin taretaran da suke da ita, ta riga ta mika wuya yanda take jin jiki bata tsammanin zata rayu.

Jikinta  suka wanke mata lokacin anyi sa'a Gudawar ta tsaigata da zuba.

Uwale tayi saurin dauko mata wasu kayan da wando da rigar nono suka sanya mata jikinta mikar da ita sukayi kafafunta suka dinga kyarma!  a daddafe suka shiga da ita daki.

Uwale ce ta shiga gyara gurin,  ita kuma Tasallah sai da ta tsaftace hannuwanta, sannan ta kwance ledar maganin data dauko ta fito dasu a daddaure! daka gani sun jima a ajiye,  wuta ta hura  kafin ta  wanke maganin tas ta zuba  a tukunya tasa jar kanwa  sannan ta d'ora a wuta.

Sai da ya tafasa sosai sannan ta sauke domin yasha iska.

To cikin ikon Allah da hukuncinsa  tana shan wannan magani ta samu sassauci ciwon  cikin da yake damunta yayi sauki  baccin wahala ya d'auketa.

Uwale ta kalli Tasallah da fadin." Sai yanzu hankalina ya kwanta Tasallah al'amarin nan ya

tsorata ni mutuka."

Tace." Dole ne, ni kaina ganin yarinyar a galabaice sai da na firgita kasancewar na san cewa wannan cutar na saurin halaka mutum! Allah yasa akwai ajiyayyun magunguna kinga cikin ikon Allah sunyi amfani "

Ta sauke ajiyar zuciya da fadin." Tasallah nifa ina zargin Dayyiba."

Shuru tayi tana kallonta da mamakin maganarta.

Tace." Tun bayan da yarinyar nan taci Dambun da Dayyibar ta kawo mata shikkenan ta rikice shiyasa nake zargin ko da abunda tayi.

Tace." Uwale zato zunubi aka ce koda ya kasance gaskiya ne, ni kuma nafi tunanin ko sauyin cima ne da ruwan sha, kin san hakan na iya janyo faruwar mummunar matsala.

Tace." Idan hakane me yasa jiya da taci abincina ta kwana lafiya? ruwa kuma ba irin wannan muke sha yarinyar take sha ba, kafin mijinta ya tafi sai da ya siya mata ruwan roba gashi can a daki kwali guda. gaskiya ina zargin Dayyiba.

Tasallah tayi murmushi da fadin." Hakan na iya faruwa amma kada kiyi gaggawar yanke hukunci tukkuna.

Shigowar Hamra'u ne ya katse maganar, babu wanda ya nuna mata wani abu a fuska, ta zauna suka gaisa, kafin ta kalli Uwale da fadin." Ummana ta kawo miki Dambu ko."?

Tace." Eh ta kawowa dai Gimbiya."

Ta dan 'bata rai da fadin." Ai naki ne kasancewar na san kina son Dambun masara yasa na tashi da wuri nayi miki, ko kafin na fito daga wanka na samu Ummana bata gidan wai ashe anan tazo."

Tace." To Na gode sosai Allah yayi miki albarka."

Tasallah na 'yar dariya tace." Hamra'u kenan to menene dan kishiyarki taci ai abun burgewa ne "

Zumbura bakinta tayi tana ya mutse fuska.......Dukkaninsu babu wanda yaji dadin abinda tayi, kiri-kiri take nuna kishinta a fili.

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing, idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:56 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176 domin karin bayani, maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka fara amfani da maganin zaki ga sauyi, domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari 2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*107&108*
Sai gefin magariba ta tashi daga baccin daya d'auketa, jiki babu kuzari ta tashi zaune da sunan Allah a bakinta, shiru tayi tana tunanin irin wuyar da tasha a d'azu, tabbas da kwananta ya 'kare babu wanda ya isa ya hana Allah zartar da Allah ikonsa, sam ba tayi tsammanin cewar zata sake wata rayuwar ba, duba da irin siradin data tsallake, a mai da gudawa ba karamin cuta bane, yanzu ma gabad'aya bata jin dadin jikinta, duk yayi laushi akwai bukatar karin ruwa a tare da ita.

Zazzafar ajiyar zuciya ta sauke ta fara kokarin sauka daga gadon, kira ya shigo wayarta dake saman gadon, ta dauka tana dubawa, a kalla ya kira yafi sau ashirin tana bacci, tausayinsa ya rufe ta, tasan yana can a dame kamar yanda take a takure! ko kuma jikinsa ne yake fada masa cewa akwai matsala.

Ta daga wayar cike da so taji muryarsa, network yayi tsiya dan sai magana take masa amma shi ba yaji.....Ta kashe wayar ta sake kira anan ma ba babu biyan bukata, kamar zata fashe da kuka ta ajiye wayar takaici duk ya isheta.

Uwale ta shigo dakin, ganinta a zaune yasa ta sauke ajiyar zuciya tace." Kin tashi ko ya jikin naki."?

Tayi kokarin danne damuwarta ta amsa da fadin." Naji sauki sosai na gode."

Tace." Haba ai babu godiya a tsakaninmu Gimbiya Allah dai ya kiyaye gaba."

Ta amsa da "Ameen ya Allah."

A sanyaye tace." Amma don Allah ina neman alfarma a gurin ki."

Cike da mamaki take kallon matar wace irin alfarma ce."?

Tace."Don Allah kada ki fad'awa mijinki abunda ya faru kinji ko."?

Murmushi kawai tayi kafin tace." Insha Allah kada ki damu ba zan fad'a masa ba."

Tace." To na gode sosai."

Har ta juya zata fita daga dakin ta dakatar da ita....."Ina bukatar nayi wanka jikina bana jin dadinsa."

Tace." Ai dole!  amma kiyi hakuri ayi sallah tukkuna bari na dora miki ruwan zafi sai ki gasa jikinki."

Tace." To shikkenan hakan yayi." Uwale ta fita daga dakin tana godiya ga Allah ganin yanda ya gajarta musu wahala.

Cikin ikon Allah ta na yin wanka jikinta ya warware   ta zauna taci abinci zuciyarta fes domin ba tayi tunanin cewa wai abincin da taci dazu ne ya janyo mata matsala ba,  itama tafi tunanin cewa ko sauyin yanayin gari da  sauransu.

Ta kalli Uwale da fadin." Ina so nayi waya amma gidan nan bashi da network yana bada matsala."

Tace." To yanzu ya za'ayi kin ga yanayin gidajen namu ginin da ne babu tsayin katanga a daki ga zurfi.

Tace." Zan fita waje ko Allah zai sa a dace."

Tace." To shikkenan  babu damuwa.

Can wani fili ta nufa,  duk da dare ne hakan bai hana gane ta ba, ido yayi caaa! a kanta, yara da manya masu wuce wa.

Ita dai bata damu ba bukatar ta, ta samu wayar masoyinta.

Bugu daya ta shiga ya daga, abun mamaki tar taji muryarsa babu gargada.

Ajiyar zuciya mai sanyi ta sauke kafin tace " Darling  ya kake? ina fatan kana cikin koshin lafiya."

Yace." Kin san hakan ba zata samu ba, ZINAT me yasa baki  d'aga wayata  akan lokaci ba."

Tace." Ba laifi na bane network ne babu a garin, nima na damu da kai sosai wannan dalilin yasa na fito waje wani fili duk dan naji muryarka."

Yace." Yanzu kina nufin ba'a cikin gida kike ba."?

Tace." Eh ai cikin  gidan na fad'a maka babu network mai kyau.

Ya sauke ajiyar zuciya da fadin." Ki koma gida bana san tsayuwar ki a gurin nan."

Tace." Haba babu fa abunda zai faru duk ga jama'a nan suna kai kawo a gurin."

Ajiyar zuciya ya sauke  yana tunanin  wani abu a ransa,  jiya kwana yayi yana munanan mafarkai a kanta, amma yasan babu wani mahalukin da ya isa ya cutar da ita face Allah ya mayar masa da sharrin kansa.

Hamra'u da k'awarta Zabbah  suka hangota a tsaye da waya a kunne.

Hamra'u tace." Zabbah ga mutsiyaciyar can."

Zabbah ta kalli gurin da fadin." To me ya fito da ita a wannan daran ita ba 'yar gari ba."

Tace." Waya ta take na san kuma da masoyina take, yau sai naci  mutuncinta in yaso duk abinda zai faru ya faru."

Zabbah ta rike hannunta da fadin." Hamra'u kada fa ki aikata abunda zai janyo miki matsala ki bi komai a sannu a hankali."

Ta fizge hannunta da fadin." Zabbah ni kad'ai na san irin b'akin cikin da wannan matar ta k'unsa min, ai magana ta 'kare tunda manya sun shiga maganar har an tsayar da ranar daurin aure."

Hannunta ta fizge ta durfafi gurin da Gimbiyar take tsaye....Zabbah ta rufa mata baya.

Tace." Darling zan shiga na kwanta sai da safe." Daga d'aya b'angaran yace." Okey Allah ya tashe mu lafiya amma ki mika min gaisuwa gurin babyna kafin mu had'u."

Tana murmushi tace." Zai ji da kyau! amma shima yayi kewarka sosai.

Yace." Haka nake so ai duk sanda muka had'u zamu gaisa sosai ki bashi hakuri."

Cikin shagwaba tace."  'Daya babyn naka ma yana bukatarka fa."

Ya lumshe ido tsigar jikinsa na tashi! ya gane abinda take nufi shiyasa gabadaya kasala ta rufeshi yana bala'in son yanayin shagwabarta.

Yace." Wannan babyn yayi min laifi ki sheda masa cewa idan muka had'u zan hukuntashi da kyau."!

Ta fashe da dariya da fadin." Ba ruwana  amma na yarda duk sanda kuka  ka had'u kayi  masa hukuncin da ya dace."

Yana sake release a kujera yace." Zan kuwa cire masa kai shine hukuncin da zanyi."

Maganar ta bata kunya sosai  tana 'yar dariya tace." Ni dai sai da safe."

Yace." Dole ki gudu mana kin san halin da ki ka jefa ni ciki kuwa."?

A sanyaye tace." Kayi hakuri gobe ka dauki azimi."

Yace." Azimin dole kada kiyi  tsammanin gani na gobe kuma idan nazo komai rigimarki tare

zamu tafi."

Tace." Ai gobe ne bikin idan kazo sai mu tafi shikkenan."

Yace."Okey Allah ya kaimu amma mybe shigowar dare zanyi.

Tace." To idan hakane kawai ka bari sai jibi da wuri sai ka shig.......maganar ta katse sakamakon zuwansu Hamra'u gurun.

Ta kashe wayar tana kallonsu.

A wulakance tace." Munafukar Allah ta ala to duk asirin da kuke Allah ya karya alkadarinki, ina so ki san cewa baki isa ki hana abinda Allah ya hukunta ba."

Cike da mamakin maganarta tace." Ke wannan wace irin magana ce."?

Da yatsa ta nuna ta kamar zata tsone mata ido tace." Hamra'u ta UMARU ce shekara da shekaru ina nufin ke baki isa ki shiga tsakanin masoya ba."

Sai abun ya bata dariya amma ba tayi ba ta dake ta sha kunu da fadin." Kin san ni nafi karfin kiyi min rashin kunya ko."?

Aikuwa sai ta fusata! ta sake nuna ta da hannu da fadin." Ke asuwa kuma? ko kin dauka kina da mutunci a garin nan, to bari kiji dake da kare! baku da maraba domin bama 'kaunarki, kuma ki kwana da shirin wata shida kacal ya rage a daura min aure da mijinki sai kiyi duk abinda za kiyi."

Ranta ya 'baci sosai da irin fitsarar da yarinyar take mata, kawai sai ta girgiza kai ta kama hanya domin barin gurun.......Tace." Matar cushe bata daraja."!!

A fusace! ta juyo ta wanke fuskarta da mari wanda sanya ta ganin gilmawar taurari! ta dafe gurin cikin kad'uwa da mamaki take kallonta.

Ta nuna ta da hannu tana so tayi magana, amma tsabar b'acin rai ya ha nata furta komai, kawai ta girgiza kai a gaggauce ta bar gurin, zuciyarta kamar ta fashe saboda tsananin bacin rai!

Zabbah ta kalleta da fadin." Ko babu komai kin sha mari! wallahi Hamra'u baki da wayo har yanzu."

Ido jawur! take kallonta kafin tace." Kin san Allah Zabbah!  sai na rama mari na don kutumar ubanta tazo cikin garinmu ta mare ni, wallahi ba zan yarda ba." Fizge hannunta tayi ta nufi cikin gidan.

Zabbah ta bita da kallon takaici tana girgiza kai  kwata-kwata Hamra'u bata da wayo wallahi, kishi hauka take,  ai idan itace ba zata fito da kishinta a fili kowa ya  fahimta ba,  amma ita duk inda ta zauna maganar kenan,  tayi ta zagin Gimbiyar

Kai tsaye da ta shiga gidan kanta ta nufa gadan-gadan!  mari ta kai mata, tayi saurin kaucewa ta mari iska!! ta tsaya tana numfarfashi idonta cike da ruwan hawaye take fadin." Wallahi baki isa ki mare ni na kyale ki ba, sai na rama." Ta sake mika hannu da niyyar marin ta, kafin tayi aune! taji saukar wani  lafiyayyan marin a fuskarta!

Uwale hankali a tashe! ta shiga tsakaninsu tana tambayar ba'asi.

Gimbiyar ranta a 'bace  tayi mata bayanin duk abinda yake faruwa.

Uwale ta kalli Hamra'u da fuskar bacin rai tace." Amma wallahi kinji kunya Hamra'u kin 'bata wayonki ban ta'ba tunanin haka zuciyarki take ba sai yau."

Sai kawai ta fashe da kuka takaici biyu ya dameta, na farko tasha marika masu zafi daga gurin Gimbiyar, gashi bata samu sararin ramawa ba ana fada mata bakar magana, dama ba tun yau ba ta gane cewa Uwalen tafi kaunar Gimbiyar a kanta.

Bakin ciki da takaici ya ha nata magana kawai ta  kada kanta ta kama hanyar fita tana share hawaye.

Zabbah dake tsaye a tsakar gida tabi bayanta tana rarrashinta....."Yanzu idan Umar din yaji abinda ki kayi wa matarsa kina tsammanin zai kalleki da  mutunci? Hamra'u shifa yaki dan zamba ne me yasa zaki 'bata rawar ki da tsalle."

Ta daga mata hannu da fadin." Kin ga Zabbah na gaji da jin wannan maganar taki, domin ta kunan hagu take fita, kin san Allah sai na saubata matar nan! sai ta gwammace kida da karatu."

Zabbah tace." Yawwa to dama tuntuni ta wannan hanyar ki ka biyo yafi sauki idan kin bi ta karkashin kasa babu wanda zai fahimce ki, amma kin zauna kina hauka haba Hamra'u!

Mugun tsaki taja mai tsayi fuuuuuuu! ta shiga gidansu ba tare da tayi  mata sallama ba,  girgiza kanta tayi itama ta kama hanyar gidansu cike da mamakin al'amarin.

Malam Shafi'i yana dawowa Dayyiba ta shirya masa karya da gaskiya cewa yana da kyau yaje

har gidan Uwalen ya tauna tsakuwa dan aya taji tsoro domin ba zai yuwu ace 'yar uwar tasa tana fifita wata a kan jininsa ba.

Aikuwa ya dauki zugar matarsa domin ransa ya baci da jin abinda 'yar uwarshi ciki daya tayi wato tana fifita wata a kan 'yarsa

Har gida yaje ya sameta ta inda yake shiga ba tanan yake fita ba, sai kumfar baki yake yana sakin kausasan maganganu wanda duk wani mai hankali ya auna maganar ya san habaici ne.

Tana daga cikin daki duk ta na jin abinda yake faruwa....Uwalen na share hawaye tace." Shafi'i na gode da cin mutunci matarka ta zuga ka kazo har gida kaci mutuncina cikinmu daya da kai, baka duba furfurata ba, ka tsaya a kaina kana fada min magana babu komai na gode."

Yace." Ai gaskiya na fada miki Uwale ki gyara kuskuranki, kafin ki k'aunaci kowa Hamra'u ya kamata ki nunawa kauna da kulawa, amma a karon banza kin watsar da zumunci saboda kwadayi kin kama wata mara tarbiya kina mata ladabi a gabanki ta fitar da hannu ta tsinkawa yarinya mari ki kasa daukar mataki, karshe ma ki ka mayar da laifin kanta, wannan ba adalci bane."

Ta sanya gefan zani ta goge ragowar hawayen da ya rage tace." Tabbas da na san wannan bacin ran zan samu da nayi zamana banzo ba, Shafi'i ban ta'ba tunanin akwai ranar da za tazo ka tsaya a gabana ka nayi min rashin kunya ba."

Yace." Duk abinda nayi miki ke kika janyo idan kina son zumuncinmu ya cigaba da gudana to kiyi gaggawar sanya albarka a cikin auran Umaru da Hamra'u! domin da kin so da tuni Umaru ya auri yarinyar nan idan da rabo a kusa ma da tuni ta haihu."

Tayi shuru ta kasa magana tsabar bacin rai!

Shi kuwa rigarsa ya buge ya fita daga gidan ransa a bace.

Tana daga cikin dakin take jin sautin kukanta, tausayinta ya rufeta,duk akan ta nuna kulawa da ita ne yasa aka zo har gida aka sanya ta zubar da hawaye......ita kuwa zata bawa mara da kunya. taji wani kwarin gwiwa a tare da ita.

A nutse ta zauna a kusa da ita tare da dafa kafad'arta.

Ta kalleta a sanyaye da fadin." Kiyi hakuri abinda akayi miki kinji ko."

Girgiza kanta tayi da guntun murmushi a fuskarta tace." Uwale ke zan bawa hakuri nasan dalilina dan uwanki yazo har gida yaci miki mutunci iya son ransa, kuma cikin maganganunsa na fahimci abunda yake nufi. Ban hana Umar Auran Hamra'u ba,  nima kaddara ce ta had'a ni dashi ashe shine uban 'ya'yana ban sani ba, Amma wallahi kaf tunanina bai ta'ba kawowa cewa zan aureshi ba ballantana har na fuskanci matsala irin wannan,  wallahi na amince ya auri yarinyar nan mutukar shine kwanciyar hankalinku gabadaya.

Uwalan ta dinga kallonta tana mamakin furucinta, sam ba tayi tsammanin cewa tana da sauki kai irin haka ba,  yarinyar nada nagarta sai mu'amula ta had'aku sannan zaka fahimta.

****

Washe gari da sassafe ta fita wajen gidan domin samun network......Lokacin  jama'a basu fara kai kawo ba,  ta kira shi yana shirin fita.

Cike da farin ciki ya daga wayar  "Farin ciki na kin tashi lafiya."?

Ta amsa babu yabo babu fallasa kafin ta d'ora da fadin." Za kazo yau din."?

Yace." Eh insha Allah, ina fatan lafiya."? ba tace masa komai ba, kawai ta kashe wayarta ta koma gidan.

Ta samu Uwale ta fito da shirin shiga gidan Tasallah........Tace." Na fita ne nayi waya da maigidanki yace yana kan hanya insha Allah."

Tace."Allah ya kawoshi lafiya da dai nayi niyyar mu zauna mu kwana biyu amma saboda abubuwan da suke faruwa na rashin dadi gwara mu tafi shi yafi alkairi."

Murmushi tayi wanda ya tsaya iyakacin fatar bakinta,  tace." Wancan kayan dake cikin baggo na tsaraba ne ya kamata tunda zaki shiga cikin jama'a ki tafi dasu."

Tace." Kina nufin akwai wasu kayan da ki kazo dasu."?

Tace." Eh suna can dakin." tafada tana nuna dakin Umar din da yake dake rufe.

Uwale kasa magana tayi saboda  mamakin  mutunci da  karamcin yarinyar, tana da kyawun zuciya tana kuma da kyauta da alkairi hakan kamar a jinin jikinta yake.....Ta kalleta da fadin." Sannu da kokari, Allah ya saka da alkairi amma yana da kyau muje tare dake sai ki basu da hannunki.

Tayi jim tana nazarin maganar kafin ta girgiza kai da fadin." Babu komai Uwale ni dake duk daya ne kawai ki basu a matsayin kece ki ka kawo musu babu komai."

Tace." Aa ba za'ayi haka ba, idan ma ba za ki je ba babu damuwa amma tabbas da sunanki zan bada kayan."

Tayi murmushi da fadin." To hakan ma yayi ni zan shiga na kwanta Allah ya sanya alkairi."  Ta amsa da ameen tana kokarin bude dakin Umar din domin fito da kayan.

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing,  idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:56 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176  domin karin bayani,  maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka   fara amfani da   maganin zaki ga sauyi,  domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari  2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*109&110*
Gidan ya rage saura ita kadai, sai ta shiga tunanin abubuwan da suke faruwa, jiya da daddare kafin su kwanta Uwale tayi mata cikakken bayanin abunda yake tsakanin mijinta da yarinyar da tuntuni ta d'ora zargi a kanta,  tabbas koda Uwale ba tayi  mata bayanin komai ba   dama tuntuni ta fahimci wani abu, duk da  dai shi bai  fad'a mata cewa akwai al'kawarin aure a tsakaninsa da yarinyar ba, to ita yarinyar ta nuna mata  alamu tun farkon fara had'uwarsu...Ba zata ha nashi aure ba, domin a yanda Uwalen ke sheda mata yanda yarinyar tayi wahala a kansa hakan  ya sanya taji tausayinta, bayan haka kuma ta san  duk daran dadewa bai zama lallai ta zauna ita kadai ba, wannan ne dalilin da yasa ta tausayawa  yarinar. wai akace  son maso wani koshin wagala!   amma babu shakka ba zata lamunci munafurci da kumbiya-kumbiya ba.  domin tafiso duk abinda za'ayi a fada mata kada a munafurce ta, abu na karshe kuwa dole ya jawa yarinyar kunne ta kiyayi shiga gonarta ko kuma yi mata rashin kunya anan ne za'a samu matsala! domin mutukar yarinyar tace zata raina mata hankali to  abu ne mai sauki a gurinta  ta cire blet  ta zane  mata jiki dashi,  sai dai duk abunda zai faru ya faru.

To can gidan biki kuwa ya kacame! da hayaniya mata sun fi ashirin akan Uwale dake rabon turaman atamfofi da mayafai da sabulai na wanka da wanki.

Da yawa wasu basu samu zanin ba, saboda yawansu, wasu kuma mayafai suka samu da sabulai, duk wanda ta mik'awa sai tayi masa bayani cewa daga matar Umaru ne.

A cikin wa'inda suka samu kayan har da  mutanan Dayyiba......sai suka silale suka nufi gidanta domin kai mata rahoto.

Wasu kuwa gidan Uwalen suka nufa domin mika godiyarsu da kuma jin dadin alkairin da akayi musu.

Hayaniyar shigowarsu gidan ya katse tunanin da take.

Ta fito tsakar gidan ta gan su da yawa a tsaye....ikon Allah har da masu durkusa mata,  ta jingina jikin bango (garu) tana amsa gaisuwarsu da fadin." Ku daina godiya haka babu komai an zama daya.

D'aya daga cikinsu tace." Dole muyi godiya yarinyar kirki! domin bamu tsammaci haka daga gurinki ba, dalili mun samu labari a bakin wasu daga cikin 'yan uwanmu cewa baki da kirki mutuniyar banza ce ke da dai sauransu, sai gashi kinyi mana bazata mun gode sosai."

Murmushi kawai tayi kafin tace." Ba komai kun san mutum tara yake bai cika cif ba, kowa yana kuskure a rayuwa, wa'inda na 'batawa rai a cikinku su yafe min tunda har Allah yasa na shiga cikinku ai mun zama daya dama rashin sabo da juna ne."

Matar tace." Kwarai kuwa Gimbiya to mu dai  muna bayanki insha Allah domin dai Dayyiba bata da alkibula mai kyau! mu mutanan *KAFUR* muna sonki da kaunarki dan haka ki cire kokwanto a ranki."

Tace." To na gode sosai Allah ya saka da alkairi."

Gabadaya suka amsa da ameen. kafin suyi mata sallama su fita....Itama cike da farin ciki da jin dadi ta koma dakin ta kwanta, cikin zuciyarta take adduar Allah ya bata hakurin zama dasu, tunda tana son mijinta babu abinda ba za tayi ba.

Dayyiba da labari ya iske ta kamar ta kurma ihu saboda bakin ciki, idonta ya ciko da ruwan hawayen bakin ciki ta kalli Taburni da fadin." Amma dai kinji kunya wallahi Ashe amincin da yake tsakaninmu na 'karya ne."?

Taburni tace." Kamar yaya ban gane ba."?

Ta zabga mata harara da fadin." Meye amfanin zuwa ki kar'bi turmin atamafa kamar baki ta'ba daura zani ba."

Ta daga mata hannu da fadin." Kinga Dayyiba saurara!  kawai saboda gudun bacin ranki ina kallon alkairi sai na bar shi, kema kin san ba zai yuwu ba, zani da sabulai na samu  ke ko dake ko babu ke dole ina da rabo saboda matar Kawunsa ce to meye abin damuwa."

Dayyiba ta sanya gefan zani ta share guntun hawayen daya fara fitowa  tace." Taburni ban san ya zanyi ba akan wannan al'amari, wallahi idan Hamra'u ta samu shiga gidan Umaru buri na bai wuce ace ta zama mowa ba, amma na san hakan ba zai yuwu ba sai na taka muhimiyyar rawa. gashi bani da kudi a hannuna ballanatana naje a taimaka min."

Tace." Yanzu dai abu na farko da za fara shine janyo hankalinsa kan 'yarki,  ma'ana ya daina ganin kowa a gabansa sai ita, kafin ace ta shiga gidansa, sai kuma ayi musu farraku da Uwargidansa.

Tace." Taburni bani da kudi wallahi, kuma kin san wannan harkar sai an ajiye kudi dole a zubar da jini."

Taja tsaki da fadin." Ashe wasa ki ka dauki al'amarin, ai idan zakiyi yawo tsirara ba abun damuwa bane mutu'kar bukatarki zata biya, ki sayar da gado da katifarki ai ba'a kanki aka fara ba.

Tayi shuru tana nazarin maganar,  tabbas hakan shine mafita domin idan ta tsaya kallon ruwa to kwado ne zai yi mata 'kafa  gwara ta tashi a tsaye.

Uwale ta kawo mata gurasa *(band'asho)😃* Kanawa mune gurasa Allah yasa akwai wa'inda suka san meye ma'anar *(Band'asho)*  Taji  k'uli da man gyada mai kamshi gefe da kabeji da sauran kayan had'i, sosai taji dadi gurasar  taci ta k'oshi  kafin tayi wanka ta shirya jikinta cikin wani milk din les mai taushi da stones a jikinsa, sai ta dora alkyabba mai tafe da hula a jikinta, ta sanya takalmi rufaffan takalmi irin nasarauta, sosai tayi kyau, kamshi turaranta duk ya cika gidan.

Waje ta fito da wayar ta a hannunta.......ido yayi caaa! a kanta,  itama kallonsu takeyi sunyi rukuni-rukuni a gindin bishiya suna ta cin abinci babu kimtsi balle kamun kai.

Can gefe kuma amaryar ce da k'awayenta da ango da abokansa  sun sanya katuwar redio a tsakiyarsu kalangu sai tashi yake amarya da ango suna rawa  ana lika musu 'yan biyar-biyar.

Abin ya burgeta ya bata dariya kai tsaye gurun ta nufa cikin yanayin tafiyarta.

Hamra'u tare da Zabbah dake can nesa suka hangeta tawagar 'yan matan garin sun rufeta a lokacin da take tsakiyar amarya da ango tana manna musu 'yan dari biyar-biyar.......Ihu!!! da kaya-kaya ya cika gurun!

Takaici ya hana Hamr'au karasawa gurin,  ta juya a sukwane ta koma gida.....Ita kuwa Zabbah! sai da ta k'arasa  gurin,  ta kutsa ta samu rabonta dan sai da ta tsira da dubu biyu.

Da wayarta ta dinga yi musu vedio sai hauka suke suna he da he kowa so yake tayi hoto dashi, amarya da ango kuwa kamar su zuba ruwa a kasa su sha a tarihi ba a ta'ba biki irin nasu ba.

Hamra'u ta 'karaso gurin tana wani dauke kai! ita gata wacce ta fita zakkah a cikinsu, da ba a san asalin balbela ba sai ace daga masar tazo .......Ta zuge jakar hannunta ta fito da kudi 'yan dari -dari  ta fara watsawa a gurin.........Wani abokin ango yayi  saurin sanya wakar *Komai na Babah yafi na yaro!* Zinat kuwa ganin haukan da yarinyar take ya sanya tayi gaggawar fita daga gurin.

Ita kuwa Hamra'u sai wani jin kai take tana wani ya mutse fuska! Zabbah taja ta gefe da fadin." Wannan wa'kar fa da Salmanu yasa dake yake,  kinzo kina lika dari-dari   ita kishiyar taki dari biyar biyar ta dinga watsawa kuma ta watsa yafi dubu ashirin kinga nima na samu dubu biyu. amma ke kina lika 'yan dari -dari  sai wani jin kai kike."

Jikinta yayi sanyi ta kalleta da fadin." Kina nufin dama saboda naji haushi Salmanu yasa wannan wa'kar!

Ta fashe da dariya da fadin." E mana ma'ana kiji haushi kema ki watsa musu kudi."

Ta girgiza kai da fadin.' Lallai Salmanu bashi da mutunci."

Tace." Hamra'u ni dai shawarar da zan baki shine kiyi hakuri ki kwantar da kanki ku zauna lafiya, dan na fahimci matar nan kamar tana da saukin kai  kuma ba zaki samu matsala da ita ba,  sannan kuma a zahiri ta fiki ta ko'ina kada kice zakiyi gasa da ita."

Tace." Idan na fahimce ki kina so kice na zauna nayi mata bauta ko."?

Ta girgiza kai da fadin " Aa ba haka nake nufi ba, ina nufin ki dai daina kishi a kanta dan naga kin zafafa da yawa, baki da gashin wance dole ki zauna a matsayinki."

Ta girgiza kai da fadin." Ba zai yuwu ba Zabbah shekara sama da goma ina dauki ba dadi akan biyan bu'kata na amma lokaci guda wata ta shiga rayuwata, wallahi ba zan iya daina kishi a kanta ba, domin bana kaunarta na tsaneta! kuma zan iya komai akan ganin bayanta."

Zabbah ta dinga yi mata kallon mara hankali da tunani! itafa gabadaya rayuwar yanzu ta zama wayo da dubara da kuma siyasa mutukar ka iya wannan zaka zauna lafiya, amma shikkenan tunda tayi iya bakin kokari gurin ganin ta nusar da ita ta kasa fahimta zata kyaleta kawai taje duk abinda za tayi rayuwarta ce.

Shida shaura ya sauka a garin.......Tun kafin ya fito a mota gurin ya hautsine! hayaniya da ifece-iface! tare da haushin karnuka!

Saboda ba ta san ganin bacin rai yasa tayi gaggawar shiga gida, ta san mybe sai ya tsaya yayi abinda ya saba.

Sai dai kuma bata jima da shiga gidan ba ya shigo cikin inform da alama daga gurin aiki yake.

Koda ya shiga gidan hankalinsa gabadaya yana kanta....ya rungumeta yana ta sumbutar fuskarta. A lokacin su Uwale suka shigo gidan.

Uwale Hamra'u da Zabbah dake bayansu......Gabadaya jikin su ne yayi sanyi ganin irin soyayyar da ake zabgawa a gurin, kamar zai cinyeta ya rike fuskarta sai so yake ya kama bakinta tana kaucewa.

Gilmawar Uwale a gurin ita ta hankaltar dashi, ya sakar mata fuska yana sauke wani irin numfashi.....Juyawar da zai yi yayi ido hudu da Hamra'u dake tsaye kamar wacce aka dasa, gwiwarta tayi bala'in sanyi!

Ya d'an ji kunyarta amma da yake namijin duniya ne sai ya basar yace." Kanwata ina fata dai kin shirya kin kuma yi sallama don yau zamu tafi."

Murya na rawa tace." Ni ba zan koma ba."

Ya kalleta da mamakin furucinta a tare dashi yace." Saboda me."?

Ba tace komai ba, kawai ta juya ta fita kawarta ta rufa mata baya.

Ajiyar zuciya ya sauke yana mamakin al'amarin.

Ya dan juya in da take, wayam babu ita a gurin......bai kawo komai a ransa ba, ya cire takalman dake kafarsa ya shiga dakin da sallama a bakinsa.

Gabadaya suna uwar dakin ita da Uwalen.

Kusa da ita ya zauna yana d'an satar kallonta a idonsa ya hango rama a tare da ita kwana uku kacal ta sauya masa tayi haske sannan duk ta rame.

Uwale dake had'a kaya tace." Naji kuna magana da Hamra'u ko."

Yace." Eh wai me yake faruwa ne?

Murmushi takaici tayi kafin tace." Alkairi ne, amma tunda tace ba zata koma ba, sai ka kyaleta a ranar da aka daura muku aure ai dole ta zauna a dakinta."

Gabansa ya fadi da jin maganar da Uwalen tayi zata tona masa asiri! be shirya sanar mata da maganar yanzu ba, ya saci kallon fuskarta yaga babu abunda ya sauya a yanayin ta wayarta ma take dubawa.

Ajiyar zuciya ya sauke cikin zuciyarsa yake addua Allah yasa ba taji maganar ba, duk da ya san da kamar wuya hakan dan kyau Uwale ta fadi maganar.

Ya kalli agogon dake d'aure a hannunsa shida da rabi har an fara kiran sallar magriba, yace." Zan je nayi sallah mu gaisa da wanda ya dace kafin na dawo sai ku shirya."

Tace." Ai mu a shirye muke Umaru sallah kawai za muyi.

Yace." Uwale anya ba wani abu ne ya faru ba kuwa."?

Tace." Me ka gani kake wannan maganar."?

Yace." Naga kamar kina Allah-Allah mu bar garin bayan kinyi alkawari cewa sai kinyi sati uku ko

hudu."

Shuru  kawai tayi ba tace masa komai ba.  Ya girgiza kai tare da mikewa tsaye. bahaushe yace shuru ma magana ce, lallai akwai abinda ya faru bayan barin sa garin.

Uwale na idar da sallah ta kalleta da fadin.'' Kafin Umaru ya shigo zan dan shiga muyi sallama mutane."

Tace."To shikkean ba komai idan ya shigo zan sheda masa.

Fitar ta keda wuya ya shigo gidan, yana haska dakin da wayar hannnsa, kan dadduma ya sameta, ta idar da sallah amma bata tashi ba.

Ya zauna saman gadon karfen dake dakin yana kallonta.

Babu yabo babu fallasa ta juyo suka had'a ido taga yana mata wani irin kallo kafin yace." Zo nan ki fada min abinda ya faru bayan tafiya ta."

Ta iske in da yake ya rike  hannunta tare da zaunar da ita kusa dashi, gabadaya hankalinsa yana kanta, yana jiran abinda za tace.

Tace." Kai me kake tunanin zai faru."?  Shuru yayi be san me zai ce ba kawai yana ji a jikinsa ne."

Tace." Kamar yanda Uwale ta fada maka alheri ne hakane, Allah ya sanya alkairi a tsakaninku.''

Ya rasa gane abinda take nufi......Ganin yana kallonta yasa tace." Ya aiki ina mutuminka Asp ina fatan kuna lafiya.''?

Hannunta ya rike da fadin.'' Asp yana nan lafiya har ya bani sakon gaisuwarki amma da ba kiyi maganarsa ba na manta, sai kuma ni da nake cikin matsala."

Tace." Matsala kuma.''?

Kai ya daga mata kamar karamin yaro.

Ta zuba masa ido tana kallonsa.

Hannunta dake cikin nasa ya fara kokarin cusawa k'asan mararshi.......Tsigar jikinta ta tashi da sauri ta fizge hannun tana hararарsa.

Ido jawur!  yake kallonta, kafin yace." Kin gane matsalar ko."?

Tace." Kai kam baka da matsala sai wannan."?

Yace." Ina dasu amma wannan itace a kan gaba."

Ta'be bakinta kawai tayi ta d'auke kanta.

Duk ya rasa yanda zai yi baya so tana sha masa k'amshi!  tabbas ya san da akwai wani abu a kasa.

Ganin abinda take yasa ya kama kansa, yayi kokarin danne kwad'ayinsa, saisaita muryarsa yayi kafin yace." Ina Uwale take ne."?

Ba tare da ta kalleshi ba tace."  Ta fita domin yin sallama da mutane."

Ya mike ba tare da yace mata komai ba ya kama hanyar fita,  kallo ta bishi dashi  tana girgiza kanta.

Bata yarda ta zauna kusa dashi ba,  a kusa da Uwale tayi zamanta suna hira, shi kuwa kamar maraya suka mayar dashi direba haushin hakan ya sanya bai sa musu baki a maganarsu ba, sai dai sa'i da lokaci yana amsa waya jefi-jefi!   a haka suka isa gidan kowa da abunda ya dameshi.

A maimakon ya nufi side dinshi kawai sai ya bita nata,  ta riga ta san bin diddigin da yake mata, haka kawai ta tsinci kanta da jin haushinsa.

A nan yayi wanka ya kimtsa ya fita ya siyo musu abinci, sai da ya kaiwa Uwale nata sannan yayi mata bankwana, koda ya fito kai tsaye sashen Gimbiyar ya nufa babu wani kuzarin kirki a tare dashi.

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing,  idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:56 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176  domin karin bayani,  maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka   fara amfani da   maganin zaki ga sauyi,  domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari  2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*111&112*

A kwance ya sameta  bacci na shirin d'aukarta,  ya zauna kusa da ita da fadin." Ki tashi ga abinci na san akwai yunwa a tare dake."

Ta d'an muskuta da niyyar gyara kwanciyarta a ta'kaice tace." Bana jin yunwa."

Yayi kasa'ke yana kallonta kafin yace." Ban yarda ba kwayar idonki ta tabbatar min da cewa akwai abinda ke damunki  ko bayan haka ma ai ba ke kadai ce kike rayuwa ba, akwai wanda yake bukatar kici abinci shima ya samu rabonsa.

Shuru kawai tayi masa ba ta da niyyar tashi ballanatana taci abincin.

Ya 'bata ransa da fadin." Na lura kina so mu sanya kafar wando guda,  me yasa ki ke min haka ne? ko dan kin ga na damu dake."

Uffan ba tace masa ba, asali ma idonta yana rufe  sama-sama take jin sa.

Cikin zafin zuciya ya janye bargon dake rufe a jikinta murya a sama ya kira sunanta "Zinatu."

Ta bude ido tana kallonsa fuskarta babu fara'a ko kadan.

Yace." Na gaji da wasa da hankalin da kike min ki fito fili kiyi min bayanin dalilin da yasa kike wannan abun ai ba haka muka rabu ba da juna ba.

Zaune ta mike tana kallonsa duk ya wani firgice! har gumi yake kamar babu Ac a dakin.

Zum'bura baki tayi  ba tace komai ba ta fara kokarin komawa ta  kwanta, da sauri ya rike kafadarta ya hana ta kwanciyar in ban da rawa babu abunda jikinsa keyi, da alama baya son b'acin ranta.

"Kina so ki jefa ni cikin damuwa ko? shin ko dai wani abu 'yan uwana sukayi miki wanda kike hukuntani dashi."

Ta kalleshi tare da girgiza kanta kafin tace." Ko daya ni 'yan uwanka ba suyi min komai ba sai alkairi saboda haka ba wannan ce matsala ta ba."

Da sauri yace." Menene matsalarki ki fada min zanyi miki magani."

Cikin ranta ta ayyana wani abu, ta kalleshi ba tare da ta auna maganar ba tace." Ka janye maganar auran Hamra'u."

Ya tsira mata idanuwansa da suke a rikice!  alamun rashin gaskiya ya bayyana a tare dashi, yace." Wacece Hamra'u."?

Kallon mamaki take masa "Wacece Hamra'u."? wai tambayarta yake saboda ya raina mata hankali.

Ganin tana masa kallon zargi yasa ya daburce kafin yace." Waye ya fad'a miki zan aure ta da har kike wannan maganar."?

Tsaki taja kafin tace." Ba ka da gaskiya wallahi kuma ban san cewa kai munafiki bane sai yau wato har ni kake tambaya wacece Hamra'u? yarinyar da kowa ya sanka da ita a gari shine zaka raina min hankali.

Maganganunta sun 'bata masa rai mutuka!  ya fusata! tare da nuna ta da hannu "Kin ga saurara kada kiyi min rashin kunya ni kike kira da munafiki."?

Tace."  Kana nad'e tabarmar kunya da hauka meye dan ka fada min dalilin zuwanka garin cewa maganar auranka  zaku tattauna har ka bada sadaki kun tsayar da magana to sai me don  kayi

aure ko ka d'auka zan damu kaina a kan hakan namijin da ake so shi ake kishi a kansa."

Yaji wani mugun bakin ciki da jin kausasan kalamanta!  ya dinga fesar da wani irin huci!  yana kallonta idonsa yayi jajawur! magana daya da tayi itace take sa hankakinsa ya tashi,  (Namijin da ake so shi ake kishi a kansa)  wato wannan yana nuna masa cewar duk abinda zai yi yaje yayi bata sonsa.

Ya tashi ya fita ya bar mata dakin domin zamansa zai iya haifar da kowace irin matsala mara kyau.

Ba ta wani damu da yanayin da ya shiga ba, bacci tayi sosai babu wata damuwa a tare da ita, ta riga ta san duk abinda yake raragefe ne da kame-kame.

Washe gari bai saurareta ba ya shirya ya fita da tarin bacin rai a tare dashi. Wanda har sai da abokinsa ya fahimci cewa yana da damuwa domin kallo daya yayi masa ya sheda hakan,  abota ce ta gaskiya wannan dalilin yasa dukkaninsu suka fahimci junansu.

Ya kalleshi da fadin." UMARU kana da damuwa domin na ganta a cikin idanuwanka."

Ajiyar zuciya ya sauke ya kalleshi da fadin." Zinatu ce damuwa ta Asp yarinyar nan idan ta burkice na kan rasa gane kanta."

Asp din yace." Wani abu ne ya faru."?

Yace." Ta samu labarin tabbatuwar aurena da Hamra'u shikkenan take fushi jiya da k'yar na rintsa wallahi."

Yace." Sai hakuri, amma dole ka fuskanci wannan matsalar,  kai dai kawai kabi hanyoyi masu kyau da zaka rarrasheta mussaman yanzu da take da juna biyu dole sai an bi komai sannu a hankali."

Yace." Kana nufin nayi ta bin kanta ta nayi min yanda takeso, bana tsammanin yin hakan."

Yace." Aa ba haka nake nufi ba abinda nakeso ka fahinta shine kada ta dauki zafi kaima ka dauka,  ka kai zuciyarka nesa ka rarrasheta kada ka biye mata idan ka kwantar da kai ina mai tabbatar maka da cewa fushin ba zai yi nisa ba."

Shuru kawai yayi yana nazarin maganar.......Wani sa'in shi kansa mamakin kansa yake idan yana wani abu akan yarinyar ya rasa dalilin da ya sanya yake gudun bacin ranta, amma baya so ya sakankance ta gane lagonshi ta raina shi. shi yasa wasu lokutan yake mata jan ido.

Da tarin yunwa da damuwa ya isa gidan. jiri da ciwon kai sun addaba masa! kai tsaye gurin Uwale ya nufa ya samu abinci yaci ya kwanta yana hutawa.

Uwalen da kanta ta fuskanci bashi da lafiya....Tace." Ai ba kwanciya ya dace kayi ba asibiti za kaje a dubaka shine abinda ya dace."

Idonsa a rufe yace." Kada ki damu ina so na huta tukkuna muna da likitoci na mussaman zan kira daya daga ciki ya dubani."

Tace." To hakan shine dai-dai ai matar taka ma ai ta jima anan muna hira sai bayan la'asar ta shiga gurinta.

Ya sauke ajiyar zuciya da fadin." Uwale me yasa kika shedawa yarinyar nan abunda yake faruwa."?

Tace." Me yasa ba zan sheda mata ba Umaru ko kafiso mu tafi a haka ta samu labari a duniya tayi mana kallon mutanan banza."

Yace." Ba nufina kenan ba, nafiso duk abinda zai faru a bari ta haihu tukkuna kinga tun bayan dawowarmu babu kwanciyar hankali, na san kuma dalilin jin wannan maganar ne."

Tace." Umaru dole ne fa kayi hakuri da duk abunda zai biyo baya domin lusarin namiji baya ta'ba iya zama da mace biyu uku ko hudu, ka zama jarumi jajurtacce! akan duk abinda zai faru, bayan haka kuma ya zama dole ka jawa Hamra'u kunne ta kiyaye ta kuma sauya munanan d'abi'un da take yi kishi ai ba hauka bane."

Ya kalleta da fadin." Me tayi Hamr'un."? Girgiza kanta tayi da fadin." Aa ni ba zan fada maka komai ba, amma lallai ka ja mata kunne akan abubuwan da take aikatawa."

Ransa ya 'baci! idan ya fahimci maganar wato Hamra'u ta samu hanyar cin mutuncin matarsa

saboda tana da tabbacin cewa ta kusa zama dai-dai da ita, wannan shine tunanin da yake, Hamra'u taki dawowa saboda akwai wani abu da tasan ta aikata na rashin kyautawa.
sosai yayi mamakin al'amarin beyi tsammanin cewa zai samu matsala da yarinyar ba, saboda yana da tabbacin nutsuwa da hankalinta.

Sai wajejan goma da wani abu ya shiga gurinta, lokacin ma ita har taci abinci tayi shirin kwanciya  ba ta dai kwanta ba wayarta take dubawa.

Yayi sallama ya shiga dakin kamar mara laka a jikinsa.

Babu yabo babu fallasa ta amsa tana kallonsa har ya zauna kusa da ita.......Tace." Sannu ka dawo lafiya."?

Wani sanyi ya sauka a zuciyarsa, sam bai tsammaci haka da gurinta ba.

Da kwarin gwiwa yace." Lafiya ya kika wuni ya babyna."?

Tayi shuru ba tace komai ba.

Ya sake matsawa jikinta   yana nanik'arta. ba tace komai ba, amma gabadaya tsigar jikinta ta tashi jinsa a kusa da ita yana nema ya haifar mata da matsala.

Ya sassauta murya da fadin." My love ki kalleni za muyi magana ta fahimta."

Ta jim na minti biyu kafin ta kalleshi.  ya dinga sarrafa kwayoyin idonsa a kanta, gabadaya jikinta ya mutu, dama abinda ya keso kenan.

Ya sauke sanyayyar ajiyar zuciya kafin ya lalubi hannunta ya rike cikin nashi, a hankali yace." Hamra'u bake taci mutunci ba, ni taciwa mutunci kuma dole na nuna mata muhimmancinki kiyi hakuri kinji ko."

Murmushin takaici tayi kafin tace." Waye yace maka Hamra'u taci mutunci na."?

Yace." Uwale ta sheda min abinda ya faru a tsakaninku kuma raina ya 'baci sosai wannan dalilin yasa na yanke shawarar kiran wayarta a gabana ta baki hakuri."

Ta kalleshi tana so ta gazgata maganarsa,  kamar gaske dai gashi nan yana mata dadin baki.

Ya fito da wayarsa ya nemi number Hamra'un.....cikin ikon Allah wayar ta shiga ba'a samu

matsalar network ba.

Bai wani saki fuska ba ya amsa gaisuwarta kafin ya dora da fadin." Hamra'u abinda ki kayi ban ji dadi ba, kuma ba Gimbiya ki ka tozarta ba ni Umaru ki ka wulakanta sanin kanki ne cewa mutanan garin *Kafur!* muna da karrama bako da mutuntashi me zai sanya ki wulakanta min mata saboda kin ganta a mahaifarki."

Murya na rawa ta fara rantse-rantse da fadin." Ya saurara tayi masa bayani.....'Kin sauraranta yayi yace." Mutukar kina so mu shirya da juna dole ki bata hakuri akan abinda ki kai mata wannan ne kadai zai sanya na saurareki.

Sai kawai ta fashe da kuka da fadin." Wallahi ni ba zan bata hakuri ba, kuma duk wanda ya fada maka cewa na tozarta ta Allah ya isa tsakanina dashi, ka tambayi Uwale itama idan zata fad'i gaskiya ai a gabanta komai ya faru! sau biyu tana gaura min mari! a fuskata amma saboda son zuciya za'a ce na bata hakuri! ni kam duk abunda za'ayi sai dai ayi ba zan bata hakuri ba."

Yace." Ashe baki da mutunci dama."? Shuru gabanta sai bugawa yake! yace." Okey shikkenan tunda haka ki ka za'ba zan baki mamaki." sai kawai ya kashe wayarsa yana jan tsaki!

Ta kalleshi da fadin." Nifa idan saboda ka faranta min rai kake wannan abun to ka daina, domin hakan ba burge ni kayi ba...........koda yarinyar nan tayi min laifi na hukuntata tuntuni ka dai ja mata kunne ta kiyaye! idan kuma taki za fuskanci b'acin rai."

Yace." Akan hakan zan iya janye auranta sai me."?

Tace." Duniya za tayi Alla wadai dakai! wane irin hallaci ne yarinyar ba tayi maka ba, ai samun nutsuwarka ka aureta, ni bani da matsala domin ban san abinda Allah ya rufe a tsakaninku ba."

Yace." A da can baya ina sha'awar auranta saboda kyawawan halayenta amma yanzu duk ta fice min rai saboda d'abi'un data sauya, bayan haka kuma mutukar ba zata zauna lafiya dake ba, to kamar yanda na fada a farko zan iya janye auranta."

'Yar dariya tayi tare da girgiza kanta tace." To Allah ya rufa asiri ya tabbatar da alkairi ni dai duk wanda ya nufe ni da sharri kansa zai koma."
daga wannan maganar ba ta sake cewa uffan ba, ta shige cikin bargo tana gyara lulluba, tashi yayi ya fita, minti goma ya dawo dakin, ya kashe fitila kai tsaye gadon ya nufa ya kwanta kusa da ita, kamar zai daure ya danne abinda ke cinsa, sai ya kasa ya matsa jikinta sosai yana shanshana sassan jikinta, gabadaya ya rikice jikinsa sai rawa yake ya birkito ta rungumeta yayi tsam a jikinsa yana kesses din fuskarta da wuyanta.

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing,  idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:56 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176  domin karin bayani,  maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka   fara amfani da   maganin zaki ga sauyi,  domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari  2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*113&114*

Da asubar fari 'Dayyiba ta fice daga gidanta  da mummunan kudiri a zuciyarta. wani k'aramin kauye ta yiwa tsinke anan take sanya ran biyan bukatar ta,  to duk da sammakon da ta buga sai da ta samu  kusan  mutum biyar suna zaune tsumayin fitowar  wacce ta shiga zauran malamin. Dayyiba ta kama layi ta zauna a kusa da wata mata  hankalinta kaf yana kan hirar da suke da abokiyar tafiyarta.

Magana suke tattaunawa akan abinda ya kawosu gurinsu bokan wacce tayi kamanceceniya da wacce ta kawo ta,  ta kalli matar da fadin." Nima abinda yake tafe dani kenan, ni abinda nakeso ma a rabasu gabadaya ko kuma a haukatata ta shiga duniya."

Matar tace." Wannan duk mai sauki ne mutukar kin cika sharud'ai to bukatarki za ta biya."

Tace." A shirye nake bani da matsala duk abinda akace zanyi mutukar bukatata za ta biya."

Wannan shine 'karshen magana.......Fitowar matar dake ciki ya katse maganarsu, wacce take kan layi tayi saurin shiga ita kuma wacce ta fito daga zauran ta tsaya tana musu sallama da wani irin murmushi a fuskarta da alama akwai nasara a kan abunda tazo dashi gurin.

To d'aya bayan daya suke shiga har layi yazo kan Dayyiba ta shiga ta gurfana gabansa kafin ma ta fara yi masa bayanin abinda yake tafe da ita yace." Kina tafe da aikin babban aljani wanda yake da bukatar kafa hud'u ina fatan kin fahimta."

Gabanta yana faduwa tace." Malam har aikin nawa ya kai haka."?

Ya buga mata tsawa da fadin." Tashi ki fita ashe da sauran imani ta tare dake tunda kike jayayya damu."

Tace." Ayi hakuri ranka ya dad'e ina neman alfarma na bada kafa biyu amma samuwar kafa hud'u a gurina zai yi wuya."

Ya shiru yana kallon wani jan koko mai kurji-kurji cike da jini a ciki.

Ya kalleta da fadin." To dai gaki gashi nan yana kallonki sai kiyi masa bayani idan ya amince.

Gabanta na bugawa tace." Ubana idan zai yuwu zan bada rago mai koshin lafiya a taimaka min."

Shuru gurin yayi bayan k'are maganarta, can kuma bokan ya kama wata girgiza farar kumfa na fitowa daga bakinsa, ya kai minti goma haka kafin ya dawo hayyacinsa duk yayi wuri-wuri sai uban gumi yake.

Ya kalleta da fadin.'' Kin ci sa'a yau yana cikin walwala ya kuma amince da maganarki, sauran aikin kuma ya rage naki idan kika kuskure wani to aikin zai dawo kanki.

Cike da farin ciki tace." Na gode ranka ya dade zan kuma kiyaye da izinin ku."

Yace." Da daddare karfe biyu ki samu bakin kwatami (kazamar kwata) ki yanka ragon da hannun hagu ki nayi kina zagin uwarki da ubanki."

Tace." To an gama ranka ya dade.......Ya siffan ta mata kalar ragon da ake bukata sannan ya bata wata laya yace a gurin da ta zubda jinin zata binne.

Cike da farin ta dawo gida, kuma hankalinta bai kwanta ba sai da ta tabbatar ta samu kalar ragon da aka bukata.

Karfe biyu na dare ta fito babu tsoro babu imani ta fara aiwatar da mummunan kudirinta tana yanka ragon tana zagin uwarta da ubanta.........Ta gama ta haka rami da wukar hannunta ta binne layar....kamar saukar aradu taji wata tsawa! "Tashi ki gusa daga gurin."! a gigice! ta shige gida kafafunta na karkarwa.

Koda ta duba gurin da safe wayam! babu alamun anyi wani abu! hankalin ya kwanta ta koma gida da tunanin abinda zai biyo baya.

A daran kwanan soyayya sukayi sai dai kuma gari yana waye wa suka tashi da bala'i da masifa! kamar karnuka! ya nayi ta nayi  a fusace! ta jefa masa kwalbar turare a goshinsa a take gurin ya kumbura!  shima ya fusata ya zazzabga mata maruka ya kama hanya yayi ficewarsa zuciyarsa na wani tafasa!  gabadaya hankalinsa yayi kan Hamra'u

Koda ya isa ofis din kasa samun nutsuwa yayi ya kasa aikata komai, kawai  sai ya nufi ofis din Asp yana sheda masa cewa zai tafi *'Kafur* 'Kauyensu.

Asp din yace." Allah yasa dai lafiya domin naga kamar baka hayyacinka.

Budar bakinsa yace." Daf yake da ya rabu da Zinatu saboda wasu dalilai.

Asp ya tsirawa goshinsa ido da fadin." Kun samu  matsala kenan Umaru wai me yasa kake biye mata kuna abu sai kace kananun yara."

A fusace! ya daga masa hannu da fadin." Kaga saurara Asp na lura da kai dama tuntuni kai baka san laifin yarinyar nan  komai tayi dai-dai ne a gurinka,  okey shikkenan ni zan iya rabuwa da ita bani da damuwa kai ka aureta."

Asp ya dinga jin maganar nayi masa kuwwa! a kunne  hankalinsa yayi masifar tashi!  kokarin magana yake amma ya rasa abinda zai ce, yana kallonsa ya fita daga ofis din ya kasa aiwatar da komai.

Ya dauki wayarsa ya kira Zinatu, lokacin tana zaune bayan taci kuka ta koshi abin duniya isheta jin ta take kamar a cikin kurkuku bata so ta bude ido ta ganta a cikin gidan, domin hotonansa na da suke kafe a dakin duk tabi ta farfasasu.

Fashewa tayi da kuka bayan ta daga wayar.

Yace." Ki daina kuka Zinat na kira ki ne domin kiyi min bayanin abinda yake tsakaninku.

Cikin shashshekar kuka take fadin." Na tsaneshi bana k'aunarsa bashi da adalci.

Yace." Me yayi miki na rashin adalci ko dan zai kara aure ki ka tsaneshi."?

Shuru tayi ta gaza furta komai in banda ciwon kai babu abunda  ke damunta.

Ya dinga magana tayi masa shuru, kawai sai ya kashe wayar,  ya kira Madam tare da bata umarnin shiga gidan domin ta rarrasheta.

'Bangaransa kuwa hankalinsa bai kwanta ba sai da ya ganshi ya sauka a cikin garin *'Kafur!* tukkuna.

Kai tsaye gidan Kawu Ado ya nufa, lokacin dawowarsa kenan daga kasuwa, ganinsa a birkice ya tayar masa da hankali, sai dai kuma da yaji abinda yake tafe dashi hankalinsa ya kwanta, da farin ciki a tare dashi yace." Ai wannan mai sauki ne Umaru, za'a daura auran a yau babu matsala yanzu zamuje tare da kai domin mu tattauna maganar da mahaifin yarinyar domin yaji abinda kake tafe dashi.

Yace." Ba damuwa Kawu tashi muje domin a yau din nake san na koma gida."

Kusan a tare suka tashi, kai tsaye kuma can gidansu Hamra'un suka nufa.

Abu kamar al'mara  gari ya dau'ka!  jama'a sukayi dafifi!  a kofar gidan malam Shafi'i  Kawu Ado ya bada kudi aka siyo goro da alawa....Shi kuma angon ya ajiye dubu hamsin kudin sadaki....Limami ya daura aure bayan gabatar da sallar magariba.

Cikin gidan kuwa Dayyiba cike da 'yan uwanta da k'awaye da makota kowa da abinda yake fad'a.....Da yawa sunfi gazgata cewa ta shiga ta fita a cikin al'amarin, domin dai kowa ya san wata shida aka sa amma ko wata daya ba a cika ba an daura aure sai kace wasan yara.

Hamra'u kamar ta zuba ruwa a kasa tasha saboda farin ciki, hakika babu abunda za tace da mahaifiyarta domin ta taka muhimmiyar rawa a cikin rayuwarta.

A daran ya dauketa suka kama hanyar gida. gabadaya tunaninsa ya tsaya cak!  saboda duniyar ma gabadaya ta rikice masa ya rasa wane irin tunani zai yi, gani yake kamar duk abinda yake mafarki ne.

Cikin dakinsa ta kwana, kuma babu wani abu da ya shiga tsakaninsu, to ina kwanciyar hankalin da wata mu'amula zata wanzu babu ma sha'awa a tare dashi.

Da sassafe ta fita daga d'akin, lokacin yana toilet yana wanka. fitowar ta akan idon Marakisiyya, al'amarin da ya bata mamaki mutuka! ba tayi kasa a gwiwa ba taje ta sanar da Uwar dakinta abinda idonta ya gane mata.

Tace ta tashi  ta taje....bayan fitar Marakisiyyar  minti goma ta nufi sashen nasa...........Koda ta shiga basu kwashe lafiya ba, dan da abun yayi tsamari ma turo ta yayi ta fadi bakin kofa ya mayar da kofarsa ya rufe, ya cigaba da abinda yake.

Ta zauna taci kukanta ta k'oshi, ido jawur! ta fito daga sashen, sai sukayi kicubus da Hamra'un tayi wanka tayi ado sosai sai kamshin turare take.....kallon banza tayi mata kafin taja tsaki ta shige ta bar ta a gurin.

Girgiza kanta kawai tayi ta nufi gurin Uwale domin jin k:arshen labarin.

Ta sameta a zaune fuskarta akwai alamun damuwa.

Suka gaisa sama-sama  kowa da abinda ya dameshi a zuciya.

Uwalen ce ta fara magana kamar haka......"Zinatu kiyi hakuri kinji ko, na san wannan abun shiryayye ne amma babu komai duk  auran da ba'a gina shi ta hanyar Allah da Annabi ba, baya zuwa ko'ina kiyi hakuri da duk abinda za ki gani."

Tace."Uwale me yake faruwa ne? naga yarinyar nan Hamra'u sai shige da fice take a gidan, shin yaushe ma ta dawo? kuma naji kina maganar aure,  ban san me yasa ba tun jiya muke rigima da mijina na rasa abinda nayi masa."

Murmushi takaici tayi kafin ta shiga warware mata abinda yake da akwai, tace." Ni kaina ban sani ba, sai yanzu da ita Hamra'un take sheda min cewa jiya da magariba aka daura auran shi Umar din da kansa yaje garin akayi komai a ka gama to kinji abinda yake faruwa.

Zazzafar ajiyar zuciya ta sauke kafin tace." To saboda kawai zaiyi aure sai ya zama tamkar mahaukaci! gabadaya fa tsakanin jiya da yau ya fice daga hayyacinsa.

Tace." Ni kaina yau kwana biyu kenan rabon daya shigo mu gaisa da duk rintsi yakan shigo idan zai fita, sannan kuma idan ya dawo ma zai shigo ya dubani. wannan dalilin yasa nake zargin wani abu akan al'amarin.

Tace." Uwale idan da matsala ni zan tattara kayana na tafi gida hankalina sai yafi kwanciya bana san tashin hankali."

Ta kwantar da kai da fadin." Kada ki yanke wannan hukuncin Zinatu ki cigaba da hakuri duk abinda mijinki yake baya hayyacinsa.  Asiri akayi masa."

Ido ta tsira mata tana mamakin maganar ASIRI to waye zai yi musu ASIRI irin wannan.

A tare suka shigo  falon,  duk suka zuba musu ido suna kallo....Ita Hamra'un kicin ta nufa, shi

kuma ya zauna kusa da Uwale suna gaisawa.

Babu yabo babu fallasa ta amsa sai kallonsa take tana mamakinsa.........Ya dan duba agogon hannunsa da fadin." Uwale sai ki kaji sabon al'amari ko."?

Tace." Eh abun ya bani mamaki Umaru ya akayi ka sauya shawara."?

Kai tsaye yace." Hakan ne samun kwanciyar hankalina domin bana samun nutsuwa a tare da wacce nake rayuwa da ita.

Tace." Wannan maganar sam bata dace ba Umaru me yasa zaka sanja hali zaka kawo rashi zaman lafiya a gidanka."

Yace." Uwale ki bar wannan maganar don Allah nifa dama can dole akayi min yanzu ne na auri zabin raina."

Ta fusata! zuciyarta na tafasa! tace." Yanzu ma ba'ayi maka dole ba  ka *SAKE NI MANA."!*

Innalillahi wa'inna ilahi raji'un! abinda Uwale take nanatawa kenan,  lallai Dayyiba bata da Imani tana so ta raba sunnar ma'aiki.

Ta sake maimaita maganar kamar sabuwar mahaukaciya.....*"KA SAKE!* ni idan ka cika dan halak ne kai." Jikinta har karkarwa yake ta mike tsaye tana so taje gurin da yake zaune.

Ya mike a zabure! da fadin" Kada ki kuskura kizo nan sai kakkarya miki 'kafafu." yana gwada yanda zaiyi da hannunsa.......Ba ta tsorata ba ta 'karasa da fadin." Gani dama tun jiya kake duka na ka karya ni kaga abinda zai faru."

Ya daga hannu da niyyar zabga mata mari Uwale ta rike hannun tana kuka take fadin." Wannan wane irin tashin hankali ne Umaru anya ba za kayi wa kanka fad'a ba."

Hawaye masu zafi suna gudana a saman fuskarta tace." Uwale ki kyaleshi ya aikata abinda yayi niyya dama ai ba yau bane farko.

Tace." Aa ba za'ayi haka ba Zinatu kiyi hakuri ki koma gurinki insha Allah komai zai daidaita."

Hanci ta shaka kafin ta girgiza kanta ta juya da sassarfa ta fita daga falon.

Ya koma yana zauna yana wani irin nishi, sai gumi yake kamar wanda yayi 'yar tsere......Hamra'u dake tsaye da fulas din shayi a hannunta ranta ya 'baci ganin abinda takeso bai faru ba, jikinta a sanyaye taje ta ajiye fulas din kan daining ta koma kicin domin fito da sauran kayan breakfast din.

Ta shiga sashenta ta sanya Baraka ta hada mata kayanta gida zasu tafi .

Ta zaune gefan gado jikinta sai rawa yake ta nemi number Asp murya a dashe suka gaisa, tace." Zan tafi gidanmu ranka ya dade bahaushe yace." Ta inda aka hau ta nan ake sauka."

Da sauri yace." Zinatu idan na isa dake kada ki kuskura kije ko'ina kinji abinda nace miki ko."?

Kashe wayarta tayi bata tsammanin zata tsaya jiran wani abu.

Wanka tayi a gurguje!  ta shirya, ta umarci hadimanta suka shirya.......Direban dake dawainiya da gidan ya daukesu a mota suka dauki hanyar *KANO*

Minti ashirin da tafiyarsu Asp ya shiga gidan, kai tsaye sashenta ya nufa........ya tarar ko'ina a rufe!  hankalinsa a tashe ya nemi number wayarta   a kashe.

Hannu na rawa ya kira abokin nasa yana ganin kiran yaki d'auka idan akwai wanda ya tsana a duniya yake jin haushinsa Asp din ne.

Yayi ta kiran wayarsa yaki dagawa, sai ya hakura ya shiga har gurin Uwale suka gaisa, anan ne ta san  da cewar Zinat din bata gidan.

Tafi Asp din shiga tashin hankali,  Iallai babu shakka a wannan karan dole ta tauna tsakuwa dan aya taji tsoro.

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing,  idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:56 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176  domin karin bayani,  maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu

cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka fara amfani da maganin zaki ga sauyi, domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari 2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*115&116*

Suna shirin tashi daga aiki mai girma Commissioner ya same shi a ofis, cikin girmamawa ya mika masa hannu suka gaisa kafin." Yace." Tunda naga mai girma da kansa to na san babban al'amari ne."

Murmushi yayi kafin yace." K'warai kuwa Umaru wani aiki ne ya taso sai naga da cewar kaja tawaga ma'ana ka zama jagora a tafiyar."

Yace." Insha Allah zan bayar da gudummawata.

Wata takarda ya fito da ita yana masa bayani cewa za suje *ran gadi* Zamfara saboda rashin kwanciyar hankalin da suke fama dashi.....za su hadu da jami'an tsaron garin domin kawo karshen ta'addancin da yake faruwa. gwamnatin garin tare da jami'an tsaron can suka bukaci wannan taimakon daga gurinsu domin suna sa ran idan ya shiga cikin al'amarin za'a samu maslaha."

Ajiyar zuciya ya sauke kafin yace.'' Ranka ya dade babu matsala yaushe ne tafiyar."?

Yace." Idan Allah ya kaimu gobe amma da Asubah zaku dauki hanya."

Yace." To Allah ya kaimu lafiya, amma me yasa ba'a za'ayi tafiyar da Asp ba."?

Girgiza kansa yayi da fadin." Akwai dalili shi akwai muhimman ayyukan da zamu gabatar tare dashi."

Ya mika masa hannu da fadin." Allah yasa mu dace." Ya amsa da ameen ya rabbi.

Sallama sukayi cikin mutunci da girmama juna. tun lokacin da Commissioner ya fahimci cewa Umar din ba irin mutanan da ake nuna su da yatsa bane ya kiyaye abinda zai kawo musu samun matsala domin ya fahimci cewar Umar din yana da babban matsayi a government house bayan haka kuma manya 'kasa suna ji dashi, domin shi kansa shugaban k'asa yana

alfahari dashi saboda yana taka muhimmiyar rawa gurin dakile harkokin ta'addanci a kasa baki daya.

A maimakon ya kira Asp ya sheda masa abinda yake faruwa sai kawai yaja bakinsa yayi shuru haka kawai yake jin wani irin haushinsa da kiyayyarsa a zuciyarsa duk wanda ya danganci yarinyar haushinsa yake ji.

Asp ya samu labari a bakin Commissioner dole sai da sa hannunsa komai zai tafi dai-dai, koda yaga abokin nasa ne zai jagoranci tafiyar sai yayi mamaki mutuka amma bai nuna a fuskarsa ba saboda baya so wani ya fahimci cewa akwai sa'bani a tsakaninsu.

Ya isa gida cikin tarin gajiya da damuwa da rashin walwala duniyar gabadaya tayi masa zafi ya rasa wane irin tunani zai yi.

Ya samu Uwale ta had'a kayanta tsaf  tana jiran shigowarsa, ganinsa sai kawai ta fashe da kuka! kariris!

Hankalinsa ya tashi ainun!  domin ko kadan baya kaunar damuwarta.

Ya rungumeta a jikinsa yana rarrashinta,  amma fafur! taki tayi shuru!  ya kalli Hamra'u da tayi tsuru-tsuru!  alamun rashin gaskiya ya bayyana a tare da ita,  yace." Me yake faruwa ne shin me kukayi mata."?

Tace." Wallahi nima ban sani ba tun dazu nake tambayarta tayi shuru sai share hawaye take wai *'Kafur!* za ta tafi."

Ya kalleta da fadin." Wane irin *'Kafur* kuma?  ai na dau'ka ko sati  uku baki da zuwa ba, ko wani ne ya mutu a can."?

Tace." Umaru zama a tare da kai bashi da amfani tunda ban isa na saka ba kuma ban isa na ha naka ba, to zanyi tafiya ta k'auye zamana a can yafi alkairi."

Yace." Me nayi miki wanda ya janyo wannan maganar."

Tace." Akan abunda kake Umaru shin ko ka samu ta'bin hankali ne."?

Yace." Lafiyata lau na san dai duk kina wannan maganganun akan Zinatu, gabadaya ni yanzu

bana ra'ayin zama da ita.

Tace." Shine dalilin da yasa ka koreta dada gidanka.?

Babu wata damuwa a tare dashi yace." Aa ni ban kore ta ba, ita ta kori kanta."

Tace." To shikkenan  tunda kace haka mutukar kana bukatar zama tare dani kaje kayi bikon matarka."

Yace." Uwale ni yanzu muhimiyyar tafiya ce a gabana gobe insha Allah, sai dai idan na dawo."

Shuru tayi kafin tace." Umaru baka kyauta ba wallahi jiya  abokinka yazo gidan nan hankalinsa a tashe, a bakinsa  na samu labari  cewa yarinyar bata gidan.

Yace." Kina nufin Asp yazo gidan nan bayan na fita."?

Tace." Eh yazo kuma yayi min cikakken bayani akan abunda yake faruwa tsakaninka da matarka, gabadaya kaine baka da gaskiya Umaru me yasa ba zaka tausaya mata ba duba da juna biyun da take tare dashi."

Yayi shuru zuciyarsa nayi masa wani irin  zafi! Asp ya samu damar da har yake shigo masa gida ba tare da izininsa ba, har ya samu damar da zai dinga bibiyar abunda ya shafi iyalinsa, shi ai ba yayi masa wannan katsalandan din, ya kamata a wannan karan ya nuna masa kuskuransa.

Hamra'u ta had'a masa ruwan wanka yayi ya samu sassauci amma kadan domin shi kadai ya san irin bakin cikin dake cin zuciyarsa.

Ya sanya jallabiya da gajeran wando ya fito falo fuskar nan a murtuke!

Ita kuwa Amarya ta rangad'a ado sai kamshin turare take mai dad'i da tayar da sha'awa.

Yana zama gurin cin abinci ta isa gurin cikin kwarkwasa da karairaya ta hada masa abincin ta zauna kujerar dake fuskantarsa tana murmushi take bashi labarai irin na jan hankali.

Shi dai uffan bece ba abincinsa kawai yake ci, abinda ya dame shi  ne a gabansa.

A gabanta ya kira wayar Zinatu. koda ta duba taga shine sai ta ajiye wayar........Lokacin mahaifiyarta ta shiga dakin ta samu kiran ya sake shigowa a karo na biyu.

Ta kalleta cikin tausayi da jin kai irin na uwa, tace." Ki daga wayar mana."

Murya a dashe! tace." Shine fa."

Tace." To sai me? ki daga kiji abinda yake tafe dashi."

Kamar ba taso ta daga wayar tasa a kunne can kasan makoshi tayi sallama!

Gyaran murya yayi kafin yace." Na dawo na samu labarin kin tafi gidanku shin me kike nufi da aikata hakan."?

Shuru tayi ta gaza furta komai.

Yace." Ke nake sauraro ko kin gaji kamar yanda nima na gaji."?

Hanci taja kafin tace." Bani da lokacin tsayawa na saurarin wannan mayaudariyar muryartaka duk hukuncin daka yanke dai-dai ne a guri na."
Kawai ta katse wayar ta ajiye. wasu zafafan! hawaye suka kwace mata! ya cuceta ya dirka mata ciki yana mata iskancin da ransa yake so.

Uwar ma kamar ta fashe da kuka saboda da takaici. kaf rayuwar yarinyar kwatankwacin rayuwarta ne! tausayinta duk ya isheta, ta sassauta murya da fadin." Kiyi hakuri ki kwantar da hankalinki insha Allah zamu tattauna maganar da mahaifinki idan auran ba zai yuwu ba a rabu shi yafi alkairi."

Da sauri tace."Mammah ni kaina nafi bukatar rabuwar, babban takaici na wannan cikin da nake dauke dashi."

Tace." Wannan kuma sai ki barwa Allah, domin shi ya barwa kansa sanin abinda yake boye, kawai kiyi fatan rabuwa dashi lafiya."

Kasa magana tayi kawai ta sunkuyar da kanta sai so take ta tsayar da hawayen dake zuba amma ya gagara! zubar hawayen shine samun zaman lafiyarta.

Zazzafar ajiyar zuciya ta sauke kafin ta girgiza kai ta kama hanyar fita zuciyarta cike da tunanin neman mafita.

Kishingide ta sameshi a dakin hutawarsa.
A nutse ta zauna kusa dashi kafin tace." Barka da hutu ranka ya dade."

Ya amsa da "Barka kadai Gimbiyar mata ya gida ina 'yar uwar taki."? ya tambayeta Safara'u

saboda ya san abinda ya kawo ta gurinsa bayan ba girkinta bane tabbas itama Safara'un tana tafe.
Tana kokarin magana Safah din tayi sallama, jikinta nannade da lifaya kwantankwancin ta jikin Aysha.

Suka gaisa cikin girma da mutunta juna.

Zamansa ya gyara yana kallonsu daya bayan daya kafin yace." Labarin gizo a tambayi koki tun kafin kuyi min bayanin abinda yake tafe daku na karanci hakan a fuskokinku. to ina jiran shigowar Magajin sarki ne domin shi nakeso ya kira mijin yarinyar muji daga bakinsa."

Gimbiyar tasha kunu da fadin." Ranka ya dad'e wannan al'amarin fa bana wasa bane ya za'ayi a matsayinka na mahaifin yarinyar nan ka wakilta wani ai sai ya kara rainawa mutane hankali saboda haka kai ya cancanta kayi magana dashi."

Yace."Aysha ko bayan raina Abdullahi shine Magaji na, wannan dalilin ya sanya nasa shi a cikin maganar domin yayi wa 'yar uwarsa wakilci, ita tazo da magana to amma yana da kyau shima mijin nata aji daga bakinsa.

Tace." Wannan yaro fa bashi da kirki! ranka ya dade in banda wulakanci da ciki zai kori yarinya me tayi masa haka da zafi."?

Yace." Ashe har kin manta halinta kenan? Aysha idan ke kin manta wacece Zinatu ni ban mance ba, kada ki manta irin d'auki ba dadin da muka dinga yi da ita kafin ta amince da auran, ko shakka ba nayi matsalar daga gurinta take.

Safah ta katse shi ta hanyar fadin." Kada kayi gaggawar yanke hukunci ranka ya dad'e! yanda yarinyar nan ta zabge lokaci guda shine zai nuna mana cewa akwai matsalar da take faruwa a tsakaninsu kuma taura d'aya bata taunuwa, bahaushe yace idan anbi ta b'arawo to abi ta mabi sawu, dole shima nasa laifin saboda haka yana da kyau yazo gabanka ku tattauna domin magana ta waya ba zata gamsar ba."

Yace." Wannan shawarar taki tayi Safara'u abinda za'ayi kenan. Insha Allah komai zai warware.

Magajin Sarki ne ya shigo da sallama a bakinsa.

Gabad'aya suka amsa. ya samu guri ya zauna kafin ya fara gaishe su......Maimartaba yace." Ka kira Umaru mijin Zinatu kace masa ina san ganinsa idan ya samu dama."

Ya fito da waya domin bin umarni.

Daf da zata katse ya daga wayar............bai ma duba suna ba, sai da yayi masa bayanin kansa sannan yace." Magaji afuwa don Allah ya mutan gida ina fatan kuna lafiya."

Yace." Kowa Lafiya lau  dama Maimartaba ne ya bukaci ganinka idan ka samu dama."

Ajiyar zuciya ya sauke kafin yace." Magaji ayi min afuwa ina da uzuri aiki zai kani Zamfara sai dai idan na dawo."

Ransa ya baci da jin abinda yake fada.......Yace." Okey to idan babu damuwa inaso na san dalilin da ya sanya Zinatu zuwa gida."

Yayi jim yana nazarin maganar kafin yace." Babu wani 'kwakw'kwaran dalili nima kawai na dawo gida na samu bata nan."

Yace." No! akwai dalili  Goje sai dai idan ba zaka fada ba."

Murmushi yayi kafin yace."Ka tambaye mana ni dai na san lafiya lau muke zaune amma ina tunanin kishi ne dalilin da ya sanya ta yanke wannan hukuncin."

Yace."Kishi kuma."?

Yace." Eh 'kwarai kuwa  na 'kara aure  kwana uku da suka wuce wannan shine abinda nake tunani."

Yayi murmushi da fadin." Ni a ganina wannan kadai ba zai janyo har tazo gida ba ko ka manta da lalurar da take tare da ita."? A dan kausashe! yayi maganar.

Shima ya fusata!  yace." Magaji yarinyar nan fa bani na koreta ba, ita ta kori kanta, kuma saboda ita ba zan fasa abinda nayi niyya ba, nasan kasan mata hudu Allah ya halasta min to akan wata ba zan tauye rayuwata ba."

Ya girgiza kansa da fadin." Okey to babu damuwa Allah ya sanya alkairi ya bada zaman lafiya.

Ya amsa da "Ameen ya Allah."

Cikin rashin dadi sukayi sallama da juna.

Da yake hands free yasa wayar duk suna jin abunda suka tattauna.

Yana kishingide bai ce komai ba.....Gimbiya Aysha kuwa sai fad'a take da fadin." Wannan auran warwareshi shi yafi alkairi dama can ita al'amarin be kwanta mata ba, auran jahili wanda yayi

rayuwa a daji! bashi da fa'idah mutumin kauye akwai karancin ilimi ta tare dashi babu abunda ba zai aikata ba."

Duk yana jin sababin da take bai ce komai ba har sai da ta gama tukkuna ya gyara zamanshi kafin ya fara magana kamar haka.

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing, idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:56 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176 domin karin bayani, maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka fara amfani da maganin zaki ga sauyi, domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari 2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*117&118*
"Aysha duk wannan maganganun da kike basu da tushe ballantana makama, wannan dalilin kad'ai ba zai sanya mu kashewa yarinya aure ba, ba hujja bace, dole mu jirayi zuwansa kamar yanda ya fada yana da uzuri to zamu saurare shi zuwa lokacin da zai kawo kansa."

'Bacin rai ya hana ta magana, kawai taja bakinta tayi shuru takaici tare da tausayin 'yar ta kadai ke damun zuciyarta. Ganin yanda hankalinta ya tashi yasa Shafara'u kwantar mata da hankali da tausasan kalamai masu sanyaya zuciya gami da sa tawakkali da dangana.

Yana kallonsu yayin da suke tattauna maganar so kaunar Safah na cigaba da bin kowane 'bargo na jikinsa, har yanzu tana nan da kyawun zuciya da kuma fahimta, a duk sanda Gimbiyar tasa ta rikice ta tafka wani shirman yana alfahari da ita gurin ganin ta shawo kan matsalar da duk ta shafe su baki d'aya.

****

A daran Asp ya kira wayarsa don da shima har yayi zuciya da abubuwan da yake masa na rashin kyautawa, sai kuma yaga da cewar kiran wayarsa domin su tattauna akan maganar yarinyar da aka bashi amanarta.

Dai-dai lokacin da ya fito daga wanka kiran ya shigo wayarsa.

Sai da ya mula tukkuna kafin ya daga wayar yayi salama babu cikakkiyar walwala a tare dashi.

Ya amsa shima babu sakewa kafin yace." I dan babu damuwa ina so mu tattauna muhimiyyar magana."

Ya sauke ajiyar zuciya kafin yace." Ba damuwa ina sauraranka."

Yace."Maganar dai akan Zinatu take duk da baka san na shiga cikin al'amarin amma ya zama dole na shiga tunda amana ce a hannuna."

Ya danne 'bacin ransa kafin yace." Okey ina sauraranka."

Ya cigaba da cewa." Yanzu Umaru dai-dai kenan abinda kayi ka kyauta! har ka rufe idonka kaci mutunci yarinya da juna biyu a tare da ita, 'bacin ran abinda kake har ya kai ta tattara kayanta ta tafi gidansu, Umaru kai a ganinka hakan dacewa ne."?

Yace." Kaga Asp ni da hankali da tunani nake al'amurana, wannan matsalar data shafe ni ce babu ruwanka da ita, maganar Zinatu ta tafi gidansu wannan matsalarta ce, idan tayi ra'ayi ta dawo idan tana ganin zama a can yafi mata bani da damuwa."

Asp din ya fusata! da fadin." Kana da hankali kuwa Umaru shin ko ka manta waye mahaifin yarinyar ne."?

Murmushin takaici yayi kafin yaja karamin tsaki da fadin." Shiyasa ai farkon magana ta da kai nace ni da hankali da tunani nake tafiyar da al'amura na, mahaifin Zinatu shine Sarkin *KANO* to sai me? bari kaji Asp Allah kadai shine abin tsoro ba wani mahaluki ba, kuma idan ka manta bari na tuna maka dama can ban furta ina sonta ba, bani akayi to akan me zan damu kaina, sai magana ta karshe da za muyi da kai dan naga ka damu da yarinyar nan da yawa baka kaunar damuwarta yanzu ma zan sake maimaita maka cewa zan iya rabuwa da ita ka aura sai kuma me."?

Asp jikinsa ya mutu murus! bakinsa ya mutu ya gaza furta kalma daya hakika ya bashi mamakin da bai taba tunani ba. kawai sai ya kashe wayar ya ajiye a gefe ya shiga tunani akan

al'amarin......Tabbas akwai alamun tambaya wannan abun da abokin nasa yake bana masu hankali da tunani bane.

***

Kamar wanda aka daukewa sha'awa haka ya zama surkududu! duk da yana ganin amaryarsa a kusa dashi hakan bai sanya yayi sha'awarta ba,  gashi nan dai zuciyarsa a kusa abu kadan yake fusata shi .

Ta shigo dakin ta sameshi a kwance ya tsirawa rufin dakin ido......A sanyaye ta zauna a kusa dashi da fadin." Yaya na."

Ya kalleta tare da kokarin tashi  zaune.

Tace."Kayi hakuri kayi bikon matarka domin Uwale da gaske take akan kudirin data dauka.  dan naga tana yi min wani irin kallo, yanzu bata sakewa dani.

Yayi jim yana nazarin maganar kafin yace." Babu ruwanki a cikin wannan al'amarin kin gane ko." Shuru tayi tana kallonsa,  ya cigaba da cewa." Aiki zai kai ni Zamfara da yardar Allah gobe da asubah zamu d'auki hanya, ki kula sosai gida kuma duk rintsi kada ki bari Uwale tasa kafa ta fita daga gidan nan."

Ta marairaice fuska da fadin." Yaya na tafiya kuma nifa amarya ce zaka tafi ka barni."

Ya tsira mata ido yana kallo,  sam abunda take bai burge shi  sai ma mugun haushi da ta bashi. tsaki! yaja dogo kafin yace " Tashi kije ki kwanta."
Ganin yanda ya murtuke fuskarsa!  babu shiri ta tashi salo-salo ta fita daga dakin.  ya koma ya kwanta yana cigaba da tunanin rayuwa.

***

A 'bangaran Zinatu kuwa tunda taji yanda akayi da mijin nata, ta 'kara tsanarsa a cikin ranta, cikinsa ma da take dauke dashi ta dora masa karan tsana tun kafin yazo duniya, dan dai yayi kwari ne amma da duk wuya sai ta zubar dashi ta yar da kwallon mangwaro ta huta da 'kuda.

****

Tafiyarsu Umar din da sati biyu, Asp ya shirya zuwa *KANO* domin tattauna maganar da ta shafi auran abokin nasa, ya kud'urce a ransa cewa kafin abokin nasa ya dawo daga bakin aiki yayi masa kokari gurin ganin matarsa ta dawo dakinta.

Bahaushe yace." Kiwon mutum ake ba dabbah ba,  wannan damar Commissioner ya samu ya dinga bibibiyar al'amarin har dai ya fahimci abinda yake da akwai. dama yana bala'in jin haushin kusancin dake tsakaninsu.

A ranar da Asp din ya  tafi shi kuma ya samu damar kiran Umar din su gaisa kana sukayi maganganun da ya shafi aikinsu, kafin ya shigo masa da maganar dake bakinsa Asp baya gari yaje Kano ziyara.

Sai ya shiga tunanin abinda ya kai Asp garin Kano bayan bashi da wasu 'yan uwa a can, wani sashe na zuciyarsa yace masa yaje gurin matarka ne."

Wani irin bakin ciki ya turnukeshi tabbas ko shakka ba yayi abinda ya kai shi garin Kano kanan. wato dai mutumin nan ba zai daina bibibiyar matarsa ba, lallai wannan karon dole ya tauna tsakuwa dan aya taji tsoro!

Saboda haka yana sallama da Commissioner din bai jirayi komai ba ya nemi number Asp din, sai kuma aka samu akasi domin shi Asp din yana ganin kiran  yaki dauka saboda jikinsa ya bashi ba alkairi bane.

Ya kirashi ya kai sau biyar bai daga ba.

Ya fusata!  ya kira number ta, itama tayi shakulatun 'bangaro dashi yayi-yayi ya gaji  tana kallo bata daga ba. takaici yasa ya jefar da wayar ya turmutsa yatsun hannuwansa cikin sumar dake kansa yana hargitsawa, jikinsa in banda karkarwa babu abinda yake.

Sai da yaci abinci tukkuna ya huta sannan Maimartaban ya zauna dashi domin tattauna maganar da ta kawoshi garin.

Da yake dattijo ne mai halin girma bai nuna 'bacin ran akan abinda ya faru ba,  sai ma dinga kokarin dora laifin a kan 'yar tasa halin mutanan da kenan ma'ana (kaso naka duniya ta k'i shi) ka qi naka duniya taso shi) Asp din ya bada hakuri sosai ya bukaci a bashi Zinatu din domin tafiya da ita.

Ya jima yana nazarin maganar kafin ya kalleshi da fadin." Da izinin abokinka kake tafe ko kuma dai kaine kake kokarin gyara al'amarin."?

Ya sauke ajiyar zuciya da fadin." Kwarai kuwa ranka ya dade kafin nazo nan sai da muka tattauna maganar dashi, yace shi bai ce mata tazo gida ba  sa'bani kawai suka samu ya dawo gidan ya samu bata nan.  dalilin da yasa kuma ba muzo tare ba, yaje *Ran gadi!* garin Zamfara

na san kana da labarin irin tashin hankali da yake faruwa a garin."

Yace." Tabbas muna da labarin irin rikicin da yake faruwa a garin, muna kuma rokon Allah ya kawo mana zaman lafiya da kwanciyar hankali a kasa baki daya.

Ya amsa da "Ameen ya Allah insha Allahu komai zai-dai ta za'a samu tsaro da kwanciyar hankali mutukar an hadu da shuwagabbani nagari."

Yace." Wannan haka yake, samun shuwagabbani nagari a wannan zamanin yana wahala dole muma mu dage da addua mu kuma gujewa abinda Allah baya so sai mu zauna lafiya."

Asp ya risina cikin girmamawa yace ." Allah ya taimake ka kayi magana mai ma'ana yawancin zagin shuwagabbanin da muke shine babbar matsala a gare mu, addua ya kamata muyi musu domin Allah ya basu ikon aikata abinda ya dace to kaga dole mu kiyaye harshen mu mutukar muna so mu zauna lafiya a k'asa."

To tsakanin Asp da Sarki Umaru sun tattauna maganganu masu muhimmanci wanda sai mai hankali da tsinkaye ne zai fahimci inda suka dosa.

Da farko bijirewa tayi da taji maganar ita kam duk abinda za'ayi ba zata koma ba ta gama auran har abadah.

Babu wanda bai shiga dakin ya rarrasheta ba amma fafur! taki karshe ma sai kawai ta kwanta tana kuka ita ta gaji da wannan al'amari wane irin aure ne wannan mara 'yanci.

Da yake akwai kauna mai tsanani a tsakaninta da mahaifinta, koda ya shiga dakin rungumeshi tayi tana kuka tace." Ni ba zan koma ba nafi bukatar rabuwa da auran saboda babu kwanciyar hankali a cikinsa, tun farko sai da nayi tunanin hakan zata faru amma babu wanda ya fahimce ni sai yanzu gashi abubuwa marasa dadi suna biyo baya ina ganin ko na koma babu abunda zai sauya.

Jikinsa ne ya mutu a hankali ya zauna tare da zaunar da ita a kusa dashi, cikin laluma ya fara kwantar mata da hankali, shi kansa baya san ta koma a yanzu yafi bukatarta a gabansa saboda yana tausayawa halin da take ciki, hakika yaron ya bashi mamaki mutuka!

Ya rarrasheta sosai tare da sake bata umarni a karo na biyu, ya kuma tabbatar mata da cewa shine na karshe wata matsalar ta sake faruwa a tsakaninta da mijinta to ba zai mata dole ba amma dai a yanzu tayi masa alfarma ta koma dakinta.

Mahaifinta yafi karfin alfarma a gurinta, tabbas idan ta bijirewa bukatarsa ba zata ga da kyau ba, dole ta sanya hakuri da dangana a zuciyarta, amma a can kasan zuciyarta ita kadai tasan abinda damunta.

Albarka da addua da fatan alkari iyayenta sukayi mata insha Allahu kuma adduarsu ba zata fad'i a kasa ba.

****
Koda suka isa gidan Uwale kasa 'boye farin cikinta tayi ita kuwa Hamra'u kamar wacce aka aikowa da mala'ikan mutuwa! tayi kicin-kicin! idonta jawur kamar me shirin fashewa da kuka!

Uwale ta kalli Asp da fadin." Hakika samun irinka a wannan zamanin sai an tsananta binkice! kai ba za'a kira ka da aboki ba domin ka wuce haka! kana tsaye akan Umaru da al'amuransa Allah ya saka maka da alkairi ya biya ka da aljanna madawwamiya.

Ya amsa da "Ameen ya rabbi ai ba wani abu bane Uwale ban dauki Umar a matsayin aboki ba kamar yanda ki ka fada dan uwana ne! wannan dalilin yasa hankalina ya tashi ganin yanda abubuwa marasa kyau suke faruwa dashi. tabbas akwai abinda yake lullu'be kuma muna rokon Allah yayi mana maganin ko menene.

Tace." Insha Allahu kuwa Ai babu abunda yafi karfin Ubangiji kai dai Allah ya saka maka da alkairi."

Ya amsa da "Ameen kafin yayi musu sallama ya tafi muhallinsa.

Hamra'u tayi zaune a daki tana sakawa da kwancewa, zazzafar ajiyar zuciya ta sauke kafin ta dauki wayarta number sa ta kira.

Sai da ta kira sau uku ana hud'un ya daga! kafin ma tayi magana ya buga mata tsawa! dama zuciyar a kusa take ana fagen daga!!

Jikinta ya shiga rawa! sai ta manta ma abinda za ta fad'a

Yace." Wai shin ke ban ha naki kira na bane? da kaina nace ki bari idan na samu isheshshen lokaci zan kira ki me yake damunki ne."?

Hawaye masu zafi suka cika kwarmin idonta! kamar ta kashe wayar sai dai ta daure murya na rawa tace ." Dama zan fada maka cewa Zinatu t.........! jin ta ambaci sunan wacce ya tsana! yasa da gaggawa ya kashe wayarsa ba zai saurari karshen maganar ba ballantana ransa ya 'baci!

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing, idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:56 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176 domin karin bayani, maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka fara amfani da maganin zaki ga sauyi, domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari 2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*119&120*
Kasa daurewa tayi ba'kin cikin abinda yayi mata yasa ta kasa fita falon, nan ta kwanta kan gado kuka mai cin rai ya k'wace mata, ita kam har yanzu ta kasa fahimtar inda ya dosa kullum babu kyakykyawar mu'amula a tsakaninsu, ba dama tayi masa magana sai ya kyareta! ko ya hantareta! gabad'aya ta kasa shawo kansa a lokacin da ba suyi aure ba ma yafi kulawa da ita, yanzu kuwa da ya cancanta ace ya kula da ita hakan bai samu ba, wannan al'amarin yana bala'in damunta.

Haka ta zama mujiya a cikinsu, dan gabad'aya sai ta tsargi kanta ta dinga ja da baya tana wani abu irin abu na marasa gaskiya, Uwale kam tunda ta fahimci cewa ita da uwarta basu da gaskiya sai kawai itama ta shata mata layi, ta daina sakar mata fuska a yanzu babu kyakykyawar mu'amula a tsakaninsu.
Tafi mayar da hankalinta kan Zinatu saboda tana tausayawa halin da take ciki, tunda ta dawo

take fama yau da lafiya gobe babu sai ya kasance kusan kullum Uwalen tana can sashen nata domin debe mata kewa duk da cewa tana tare dasu Baraka amma kasancewar Uwalen a tare da ita ya faranta mata rai mutuka. sha'kuwa mai kyau ta shiga tsakaninsu.

'Bangaran Hamra'u kuwa abin duniya ya isheta, kullum sai ta zubar da hawayen takaici gidan kaf sun hade mata kai sun mayar da ita saniyar ware babu wanda yake yi da ita, sai ta fara rama a tsaitsaye saboda damuwar da ta sanya a ranta dole itama tabi ayari mutukar tana so tayi rayuwar farin ciki a gidan.

Sai ta dingi shiga sashen Gimbiyar, al'amarin da ya basu mamaki mutuka! amma basu nuna mata komai ba, tun bata sakewa dasu har dai ta saba ta daina dari-dari domin ganin ta sauya hali ya sanya Uwalen sassauta mata, wannan ya sanya hankalinta ya kwanta a gidan, ita ta cigaba da yi wa Zinat din d'awainiya har wankin undis wani sa'in ita take wanke mata ta tsafe mata kitson kanta kana ta kitsa mata sabo, idan kafafunta sun dameta da ciwo itake matsa mata.

Abun dai har ya soma damun Zinat din saboda bata so wasu daga waje suga abunda yake faruwa su d'ora ayar tambaya a kanta shiyasa tayi wani tunani akan al'amarin.

Da fara'a ta shiga ta sameta kan doguwar kujera a kwance tace." Aunty Gimbiya jikin ne ko garin ina fata dai babu abunda ke damunki."?

Ta ya mutse fuska da fadin." Kinga wallahi tun safe na tashi da ciwon mara asibiti nake so muje yanzu."

Tace." Eh lallai zuwa asibitin yana da muhimmanci bari na shedawa Uwale."

Tana kokarin tashi tace." Okey bari na shirya kafin ki dawo." Daki ta nufa tana cire kafa da kyar! ciki wata biyar kacal yayi girma sai suddubaru iri-iri!

Uwale tace." To ko na shirya muje tare."? kai ta girgiza da fadin." Ki zauna kawai yanzu zamu dawo." Tace." Shikkenan amma yana da kyau kafin ku tafi ki shedawa mijinku koda ta waya ne."

Tace." Uwale bana so na kira shi yayi min fad'a ki bari kawai mu tafi."

Tace." Aa dole ki fada masa hakkinsa ne."

A sanyaye tace." Shikkenan.

Cikin tararrabi da jin tsoro ta kira shi, akaci sa'a ya dauka bai kuma yi mata fada ba, su gaisa a

mutunce ya tambayeta gida tace." Kowa lafiya lau."

Shuru tayi tana nazarin maganar dake bakinta. tuntuni tasan baya kaunar tayi masa maganar matarsa amma ya zama dole ta sheda masa abinda yake faruwa.

Yace." Hamrau ko da matsala ne."?

Ajiyar zuciya ta sauke kafin tace." Dama za muje asibiti ne da Aunty Gimbiya bata jin dadin jikinta."

Yaja wani dogon tsaki da fadin." Ba da yawu na ba, kada ki kuskura kije ko'ina."

Ta bude baki kenan za tayi magana ya kashe wayarsa! ta tsirawa wayar hannunta ido tana mamakin irin k'iyayyar da yake nunawa matarsa kamar wacce ta kashe masa uwa da uba.

A sanyaye ta fito daga dakin ta shedawa Uwale yanda sukayi......Cikin bacin rai!  tace." Kamo min wayar tasa muyi magana."

Koda ta kira shi yana kallo har ta katse bai dauka ba, ta dinga kira tana katsewa,  kwata-kwata yaki dauka.

Tace." Wallahi yaki daga wayar na kira ya kai sau bakwai.

Murmushin takaici tayi tana girgiza kai!  hakika  Dayyiba bata kyauta ba ta shiga tsakanin ma'aurata ta sanya musu kiyayyar junansu.

Sosai fa take jin jiki dan koda ta shiga dakin da niyyar sauya kaya kasa komai tayi ta sake kwanciya tana kiran sunan Allah, cikinta ne yake mata wani irin  ciwo ga wani uban gumi da take shar'bawa!

Cikin wannan halin ta shiga ta sameta, bahaushe yace  ciwon 'ya mace na 'ya mace ne! Hamra'u hankalinta ya tashi ganin yanda take murkususu!  duk kiyayyar da take mata sai ta nemeta ta rasa  hankalinta ya tashi ta rasa wane irin taimako za tayi mata.

A hankali tace." Na shigo dan na sauya kaya amma na kasa saboda yanda ciwon cikin nan ya dameni."

A sanyaye tace." Sannu yanzu ya za'ayi?  Uwale tace." Lallai sai na kira maigidan na sheda masa  abinda yake faruwa, to koda na kira shin sai yace kada muje ko'ina."

Ta kalleta tana jin wani irin 'bacin a can cikin ranta, rintse idonta tayi tana tunanin yanda za tayi, ta bud'e idon tare da kallonta tace." Kyaleshi kawai miko min wayata gata can saman mirror."

Da sauri ta mika mata wayar. ta lalubi number Asp da kyar ta iya sheda masa halin da take ciki.

Hankali a tashe yace." Insha Allahu zan turo Likita zai zo ya dubaki yanzu ya baki magani ba sai kunje ko'ina ba tunda muna tare da kwararrun likitoci a cikin gidan.

Tace." To shikkenan nagode Allah ya saka da alkairi."

Ya amsa da" Ameen ya Allah." kafin ya kashe wayar ya fara laluben number Likitan da yake da tabbaci a kansa.

To cikin ikon Allah tana shan magungunan da likitan ya d'ora ta akai ta samu sassauci a take wahalallan bacci ya dauketa, duk ta rame na lokaci guda.

Asp yana tashi daga aiki bai nufi ko'ina ba sai gidan abokin nasa hankalinsa gabad'aya yana kan yarinyar, sai da yaje ya dubata sannan hankalinsa ya kwanta mussaman da ya sameta a zaune ta warware tana cin abinci.

Ya dubata sosai ya kuma bata shawarwari masu amfani kafin yayi mata sallama ya nufi muhallinsa.

A daran ranar ya samu labarin duk abunda yake faruwa.

Koda yake ba labari ya samu ba, hotonan Likitan da ya dubata da hoton Asp da shigarsa da fitarsa duk aka tura masa ta WhatsApp bashi da tabbaci akan wanda ya turo masa sa'kon asali ma bashi da number.

Hankalinsa ya tashi ainun! Asp ya zame masa kadangaran bakin tulu, baya gari amma yana shigar masa gida ba tare da izininsa ba, garadan maza suna karakaina a cikin gidansa har cikin dakin matarsa.

Kansa ya dinga yi masa wani irin ciwo! tunaninsa gabadaya ta tafi gurin ganin ya samu hanyar da warware matsalarsa, yanzu zargin cikin da yake jikin yarinyar yake, Asp ya wuce gona da iri babu abunda ba zai aikata ba.

Cikin rashin tunani da gushewar hankali da tsinkaye ya kira Asp din yana wani irin huci! ya fara surfa masa rashin mutunci! Asp din ya fusata! da karfi ya buga tevur din dake gabansa ya mike tsaye da wayar a kunnansa yana fadin." Umaru ni kake kira fasiki! anya kana da hankali

kuwa ko dai ka fara shaye-shaye ne."?

Shima a fusace! yace." Bana shan komai! hankali kuma bani dashi mutuk'ar akan na zuba maka ido kana abunda kaga kake so, nifa ba  bagidaje bane da zaka dinga raina min hankali. kullum kana bibiyar matata a gindi-agindi dole nayi zarginka, kaje ka dawo da ita ba tare da izinina ba, bana gari kana zurga-zurga a cikin gidana, akan me ba zanyi zarginka ba."

"Ya isa haka."!! Da karfi yayi maganar jikinsa na wani irin karkawa.

Ya cigaba da cewa." Wallahi ban ta'ba tunanin da'kiki! bane kai sai yau!  dole kayi wannan tunanin saboda jahilcin da yake damunka,  ka jima kana mummunan furuci a kaina har kana danganta ni da matarka ta sunnah. to bari kaji kwata-kwata kai baka dace da wannan yarinyar ba, wallahi dana san haka halinka yake da ba zan shige maka gaba har ka samu nasarar auranta ba, babu damuwa kayi kuskuran sakinta  ni kuma zan baka mamaki."! Bai jirayi amsarsa ba kawai ya kashe wayarsa.

Wayar ya tsirawa ido yana kallo hankalinsa a tashe! wannan shine a dake ka a kuma hana ka kuka, Asp ya shiga huriminsa amma saboda tsabar rashin tsoron Allah yana nad'e tabarmar kunya da hauka.

A daran kasa rintsawa yayi koda yake dama can ba wani baccin arziki suke ba, kullum suna tsakanin border suna kai kawo amma dai wani lokacin idan baccin yazo yi suke ba tare da saninsu ba, domin shi bacci daban yake a cikin abinda Allah ya hallata mara sa rai.

Yana kallon wasu daga cikin abokan tafiyarsa suna bingirewa bacci na kwasar su, bai hanasu ba kwai ya kyalesu su sarara shima ya samu damar nazari da tunanin hanyar warware matsalarsa......Sai dai a gurin tunanin baccin dai da yake gudu yazo ya sace shi ba tare da yayi tsammani ba.

Cikin baccin yayi mafarki da  wani dattijon mutum da fararan kaya a jikinsa kansa nade da farin rawani farin gemunsa ya kusa ta'ba kasa akwai wani zabgegen carbi a hannunsa. suffar mutumin dai gashinan ba  mutum ba ba kuma aljan ba.

Sunansa ya kira." UMARU."

Ya amsa da "Na'am."

Yace." Ni ne abokinka ina tare da kai tun kana cikin uwarka nima sunana UMARU ni musulmi ne ina kuma taimakon bil'adam mussaman musulmai. ban ta'ba bayyana a gare ka ba sai yau duba da ganin yanda al'amuranka suka lalace! me yasa kake sakaci da addua? a can baya baka da wasa amma yanzu ka bari har ma'kiya sunyi tasiri a kanka."

Shuru kawai yayi  yana kallon Dattijon.

Yace." Rufe idonka.

Kallonsa yayi nan ya hango k'wayoyin idon dattijon sunyi kama dana *ZAKI!*  Ya zabura! da sauri ya rufe idonsa.

Kamar al'amara ya ganshi gurfane bakin kwatami (kwata mara kyau)  yana hake kasar gurin. yana fito da layar! a zabure! ya bude idonsa yana duba hannunsa yaga layar  sai ya fara dube-dube a gurin, babu dattijon babu dalilinsa.

Ya dinga kiran sunan Allah yana tu'ajibun Al'amarin shin waye wannan dattijon daya ziyarceshi.?

Ya sake duba layar dake rintse a hannunsa tunanin a inda ya ciro ta yake.....Kofar gidan Malam Shafi'i." Zuciyarsa take tuna masa.

Tabbas hakane shin me hakan yake nufi? surkulle akayi maka aka shiga tsakaninka da iyalinka. wannan karon ma zuciyarsa ta sake tunasar masa.

Sai kawai abubuwan da suka wuce suka dinga dawo masa daki-daki!   jikinsa ya jike sharkaf da gumi tsabar fargaba da tashin hankali.

Haka ya wayi gari cikin rashin karsashi da kwarin jiki, duk abunda yake daurewa kawai yake ya rasa ma tunanin da zai yi.

Ya kira wayar Asp din sau curin masaki amma yaki dauka domin ya dauki fushi! dashi  mai tsanani.

Ya kira Hamra'u da fadin." Lallai ta kai wa Zinatu wayar yana so yayi magana da ita, dalili ya kira wayarta itama taki dauka.

Rasa abinda yake damunta tayi ba dan ranta yaso ba ta kai wa Zinat din  wayar ta sheda mata abunda yake da akwai.

Tace." Kinga Hamra'u fita dan Allah bana san b'acin rai! kinzo da rawar jikinki watakila ba alkairi bane a kiran nasa, saboda haka kije kawai bana bukata.

Jikinta babu kwari ta fita da wayar a hannunta tana tunanin irin masifar da zai mata.

Aikuwa dai rufeta yayi da bala'i yana nema ya d'ora mata laifi! takaici yasa kawai ta fashe da kuka ta kashe wayar ba tare da ta cigaba da sauraransa ba kwanciya tayi ta dinga kuka tana tunanin ya rayuwarta zata kasance a gidan, dan taga kamar hankalinsa ya dawo kan matarsa

watakila ita za ta zame musu 'yar aiki, gashinan sai walagigi suke da rayuwarta  shi ya kyareta! ya hantare! ta ita kuma ta aike ta shin wannan wane irin aurene mara 'yanci.

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing,  idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:56 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176  domin karin bayani,  maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka   fara amfani da   maganin zaki ga sauyi,  domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari  2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*121*
Ya kira wayar Asp yafi a 'kirga amma bai saurareshi ba, kawai sai ya yanke shawarar rabuwa dashi ya mayar da hankalinsa guri daya amma can kasan zuciyarsa akwai tarin fargaba da tashin hankali a dan'kare! domin duk abubuwan da suka faru a baya yana tunaninsu yana kuma nazarin ya akayi hakan ta kasance. babu shakka yanzu ya fara hangen gaskiya akan mafarkin da yayi cewa da akwai sanya hannun iyayen Hamra'u gurin 'bacewar tunaninsa, idan ba haka ba ya akayi al'amura suka sauya, da hankalinsa da tunaninsa  ba zai manta lokacin da yanke hukuncin wata shida kafin a daura musu aure ba, amma ya akayi al'amura suka sauya, babban abinda yafi damunsa yanda suka samu matsala da amininsa ya rasa dalilin da ya janyo hakan, burinsa ace Asp din ya d'aga wayarsa sun tattauna maganar, amma ga dukkan alamu yayi fushi dashi irin wanda bai ta faruwa a tsakaninsu ba.

Damuwar da yake ciki ta sanya masa rashin karsashi! da 'kwarin jiki duk abinda yake 'kok'ari kawai yake amma gabadaya hankalinsa yana gida gurin iyalinsa mussaman ita Zinat din da take tare da lalura.

Wani irin tashin hankali ne ya faru a daran ranar da suka gama shirye-shiryen tafiya gida.

Abinda ya faru shine, tun bayan zuwansu garin. 'yan ta'addan da suka damu garin ta'addanci suka sauya dubara! domin tuntuni suna da labarinsa da irin jazaba da baiwar da Allah yayi masa, sai duk suka watse suka sauya ma'boya, amma suna da labarin duk abinda yake faruwa a garin.

Iya bakin kokari da binkice sunyi a garin basu kama wani mai laifi ba. wannan dalilin yasa suka shirya tafiya domin hakan ma nasara ce, ace zuwansu garin ya tsorata masu laifin sun gudu saboda rashin yarda da kai.

Ashe lamfo sukayi. a daran ranar suka saka musu bom! gurin da suke ya kama da wuta!.........Mutum shida suka kone kurmus! wasu suka jikkata! tashin hankali kenan! wannan al'amarin ya dunguzuma shi! shima bom din wurgi yayi dashi can wata nahiya.
Cikin mawuyacin hali yake lalube da hannunsa so yake ya tashi zaune amma inaa! jikinsa yayi nauyi wasu guraran duk sun 'kone! ya kira sunanan Allah da k'arfin gaske! kafin yayi kalmar shahada! ya zabura! ya mike tsaye! yana wani irin ihu!!! da gurnani!!

Abinda ya tsorata su kenan dama sunyi lamfo a ma'boyarsu! duk sai suka gigice! suka fara fitowa wasu na gudu wasu kuma na harbinsa da bindiga.

Basu samu nasarar samunsa ba, saboda yafiso da dabaru!!

Shi din dai Allah ya bawa nasara ya harbe kafafun mutum biyar sukayi kwance a gurin suna jan jiki da ihu!!

Sauran suka ranta a na kare! duk da haka bai fasa sakar musu bullet ba, sai da ya sake samun mutum biyu suka zube a gurin.

Hayaki! da zafin wuta ne kawai yake tashi a gurin.

Jini da sassan jikin dan Adam dole ya firgita wanda bai saba gani ba.

Ya dinga bin 'yan uwansa yana dubawa wasu da rai wasu babu wasu sunyi daga-daga! naman jikinsu ya tarwatse!

Kuka ya dinga yi da hawaye yana kiran sunan Allah! a fili. wannan wane irin tashin hankali ne!

Wannan al'amarin da ya faru ya tashi hankali kowa ba mazauna garin ba kawai duk wani mai kishin musulunci da kishin 'kasa dole ya jajantawa kansa zubar jini a Najeria ya zama kamar

zubar ruwan famfo.

A galabaice aka nufi asibiti dashi da sauran wa'inda suke raye.

'Yan jarida mane ma labarai basu samu cikakken bayanin da suke bukata ba, dalili shi wanda zai musu bayanin baya hayyacinsa, sai dai sun d'auki rahoton gurin da abin ya faru, kuma sun samu nasarar daukar hotonsa a lokacin da ake kokarin sanyashi a cikin motar asibiti, sannan suka kutsa suka dauki hotonan masu laifin da aka samu nasara a kansu.

To kafin kice kwabo labari ya cika 'kasa baki d'aya
*GOJE!* wannan mafaraucin mutumin da ya kasance Jami'in tsaron dake garin katsina ya samu nasara akan 'yan ta'addan da suka addabi garin Zamfara! sai dai yana da muhimmanci mutanan Zamfara da 'kasa gabadaya su dage da addua akan Allah ya tashi kad'arsa! saboda yana cikin tsaka mai wuya dashi da abokanan tafiyarsa dalilin tashin bom da 'yan ta'addan sukayi ya k'ona wasu daga cikinsu kuma sun rigamu gidan gaskiya, yanzu haka dai *UMARU wanda kuka fi Sani GOJE!* Yana kwance a babban asibitin garin Zamfara domin ceto rayuwarsa."
wannan rahotanin da ke yawo gidajen television redio tare da wayoyin mutane .

Tashin hankalin da Asp ya shiga yafi gaban a kwantatashi! kaf headquarter 'yan sandan suna cikin tsananin tashin hankali da damuwa sakamakon abinda ya faru da ma'aikatansu mussaman shi Umar din da suke alfahari dashi........mutum daya ne zuciyarsa babu alkairi domin shi bai so al'amarin ya tsaya a haka ba, amma a zahiri ya jajanta kuma shine ya jagorancesu tafiyar zuwa can garin domin duba marasa lafiyan.

Idan kuka ga yanda hankalin iyalinsa ya tashi sai kun tausaya musu. Zinatu tsayuwa ta gagareta! kafafunta sai karkarwa suke! tun lokacin da taga mijin nata a tv an nuna shi kan wani gado irin na asibiti kamar matacce hankalinta ya tashi, kuka ta fashe dashi tana kiran innalillahi wa'ina ilaihi raji'un!! shikkenan mun zama marayu!

Kuka gabadaya gidan aka rasa mai rarrashin wani dan Uwale ma kasa daurewa tayi abunka da mutan k'auye sai sambatu takeyi tana share hawaye.

Zinat kasa zaman gidan tayi tasa hijab ta fice. kai tsaye gidan Asp ta nufa.

Lokacin bai jima da dawowa ba wanka ya shiga domin shiryawa tafiya.

Kukan da yaji a falon ne yasa cikin gaggawa ya fito.

Ya sameta sai rusa kuka take Madam ta rungumeta tana rarrashi itama Nabila dake zaune a

gefe hawaye take sharewa.

Ya sassauta murya da fadin." Kuyi hakuri addua za kuyi musu Allah ya  basu lafiya.

Jage-jage da hawaye a fuskarta take kallonsa da k'yar ta iya cewa." Ranka ya dade kuna 'boye mana wani abu amma a jikina nake ji mijina ya mutu."

Ya girgiza kai da fadin" Zinat da mijinki ya mutu da yanzu gawarsa ta iso gida yana nan a raye amma ba zan boye miki ba yana bukatar adduarki."

Tana shashshekar kuka tace." Don Allah kayi hakuri ka tafi dani gurinsa inaso na ganshi mu yafewa junanmu."

Tausayinta ya rufeshi yace." Insha Allah zai dawo gida da rai da lafiya ku cigaba da rayuwa. kiyi hakuri tafiya dake ba zai yuwu ba tunda bani kadai bane amma insha Allahu idan mun isa zan kira ki a waya ki dubashi.

A sanyaye tace." Rayuwata ta kare idan na rasa mijina ina sonshi bana so ya mutu barni amma mutuwa dole ce."!!

Wasu hawaye masu zafi suka zubo a fuskar Madam dauriyarta ta k'are sakamakon tausayin yarinyar.

Shima zuciyarsa ce ta karye kawai sai yayi gaggawar shigewa daki yana kiran sunan Allah a zuciyarsa, a gurguje ya shirya ya fita ta can kofar waje domin baya so yazo fita tausayin yarinyar ya sashi zubar da hawaye.

Isar su keda  wuya Allah ya kar'bi rayuwar mutum biyu daga cikin wa'inda suke kwance!  Asp dai kasa hakuri yayi ya fara share hawaye ganin tashin hankali da masifa  mutuwa dole ce amma irin wannan akwai tausayi da tayar da hankali.
Gawarwakin aka had'a guri guda kafin asa a motar da zata kaisu gida.

A daran suka juya amma banda Asp domin cewa yayi ba zai tafi ba tukkuna sai yaga abinda hali yayi, gabadaya ya cire tsammani da samuwar abokin nasa.

Commissioner bai ce masa komai ba kawai ya rabu dashi amma akwai abinda ya kud'ire a

ransa!

Da asubah bayan ya idar da sallah yaje ya zauna kusa dashi yana kallonshi cikin zuciyarsa yake masa adduar samun sassauci.

Likita ya shigo dakin,  suka gaisa kafin ya k'arasa bakin gadon yana dubashi.

Ya kalli Asp din da fadin ." Insha Allah yau din za'ayi masa aikin wannan 'kunar dake kafafuwansa za'a cire fatar gabad'aya  a wanke gurin. kana a sanya magani."

Yace." Dr amma bayan wannan babu wata matsala ko ina nufin babu wani abu daya nakasa a tare dashi.

Yace." Bana tsammanin hakan gaskiya tension ne yayi masa yawa da kuma fargaba amma insha Allah zai tashi da tunaninsa wannan shine iyakar binkicen da mukayi a kansa.

Yace." To Alhamdullhi Allah ya bashi lafiya, su kuma wanda suka rasu Allah ya yafe musu ya kuma kar'bi shahadarsu."

Likitan ya amsa da Ameen ya rabbi kafin ya gama duddubashi ya fita daga dakin.

Misalin tara da rabi Governor garin katsina  tare da mu'karrabansa suka sauka a gidan gomnatin garin.

Tare da governor Zamfara suka isa asibitin domin duba marasa lafiyan.

Lokacin ya tashi kuma cikin hayaccinsa kamar yanda Likitan ya fad'a! sai dai ya gaza furta kalma  daya sakamakon nazari da tunanin abunda ya faru.

Shi kansa Asp din gajiya yayi da magana yayi shuru da bakinsa farin cikinsa dai ya tashi cikin nutsuwa babu buge-buge!

Shigar su keda wuya ya bisu da wani irin kallo yana girgiza kansa gabad'aya haushinsu yake ji Malam me za'ayi da mulki bala'i ne ga wanda ya san hakan!

Asp ya mi'ke tsaye yana musu barka da zuwa.

Suka samu kujeru suka zauna hankalinsu gabadaya yana kansa alhini da damuwa ya bayyana

a fuskokinsu da alama dai ko a cikin shuwagabbanin suna da imani.

Kafin ma wani yayi magana a cikinsu shi ya mangantu....Asp yayi mamakin hakan mutu'ka!

"Rashin tsaro da rashin tsoron Allah da son duniya da mulki shine babbar asara! ga duk wani shugaba."

Duk suba zuba masa ido jin maganar da yake.

Ya cigaba da cewa."
Lokacin da kake ya'kin neman za'be! idonka ya rufe ka tara talakawa kayi musu al'kawaririka kan cewa  idan sun mara maka baya zaka tallefesu zaka basu aikinyi za kuma ka taimaki k'asa baki daya."

"Mulki ya zama abun rububi da kokawa! saboda samun jin dadin duniya,  kayi rantsuwa da Allah da al'kur'ani kan cewa zakayi adalci daga bisani  idan bukatarka ta biya sai ka mance da komai ka fara gina rayuwarka ka auri kyawawan mata ka ajiye a gida kaci mai kyau! kasha mai kyau! ka kwanta a mai kyau!  ka sanya suttura mai kyau! kayi facaka da kudi!  ka nemi duk macen da kake bukata  ka tura yaranka kasashen waje suyi karatu, ka tara kudi a banki ka sayi gidaje gonaki ka gina gidajen mai kayi duk wata bukatar rayuwarka  ka manta da talakawa da nauyinsu yake wuyanka wannan shine al'kawarin daka kayi wa Allah."?

D'akin yayi tsit!  babu wanda yace uffan.

Ya sauke ajiyar zuciya kafin ya cigaba da cewa........."Talauci yayi yawa a duniya saboda zalincin shuwagabbani  mai yasa matasa ba zasu shiga wani mummunan hali ba."?

"Sace-sace fyad'e  harkokin Daba gami da sara suka sun zama ruwan dare shin menene ya jawo hakan?  idan akwai son zuciya irin na mutum  to akwai sanya hannun gwamnati.

Akwai matasan da suke da degree takardunsu sunyi kyau amma ba'a daukesu aiki ba, an dauki wanda yake takardar secondary aiki a halin yanzu sai kana da hanya zaka samu, mahukunta da shuwagabbi basa bin doka kowa kansa ya sani yaya rayuwarsa za tayi kyau ya ingata iyalinsa......Idan haka ake mulki Allah yayi mana tsakani dashi."

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing,  idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*
[3/26, 9:56 PM] Matar Malam😊: _Akwai ingantaccan maganin🌴🌴 gyaran nono na hausa, ga wanda yake da bukatar maganin zai iya tuntubar wannan number...... 08089965176  domin karin bayani,  maganin ya samu lambar yabo saboda ingancinsa, yana amfani sosai domin yana ciko da nono yana kuma sanya k'iba dai misali, babu almundahana babu cuta babu cutarwa sahihin magani ne, idan kin shayar sau goma, ina mai tabbatar miki da cewa daga ranar da ki ka   fara amfani da   maganin zaki ga sauyi,  domin yana gyara mace, zawarawa da 'yan mata kuma kada a barku a baya za ku iya mallakar naku maganin domin in ganta kanki, bahaushe yace idan kana da kyau ka kara da wanka!...ga masu bukatar sari ko sayan d'aya muna KANO muna turawa kowane gari  2k kacal zaki mallaki naki kafin ya kare wallahi sai kin ga sauyi.......*SIYAN NAGARI MAI DA KUDI GIDA*! Idan matsalar nono kike fama da ita kukanki ya 'kare da ikon Allah._

*122*
Governor Nuhu Bamalli ya sauke zazzafar ajiyar zuciya bayan kare maganganun Umar din yace." Umaru ba zamu musanta maganarka ba, domin duk abinda ka fada gaskiya ne, mulki a yanzu ya zama Innalillahi wa'ina wa'ina ilaihi raji'un! amma inaso ka sani cewa ba duka aka taru a ka zama daya ba, da yawa akwai masu gaskiya ma'ana masu kwatantawa mulki irin na Annabi Muhammad SAW da sahabansa, amma mafi akasari dai marasa tsoron Allah a ciki sunfi yawa, sannan kuma bahaushe yace." Idan anbi ta barawo to abi ta mabi sawu! ina nufin ba shuwagabbani kadai suke da laifi ba, har da jama'ar gari! rashin yiwa shugaba addua bai dace ba, kana kuma zagin shugaba da cin mutuncinsa bai kyautu ba, Umaru wata masifar da kanmu muke janyota idan Allah ya jarrabemu da masifa sai kuma mu dauki laifi mu dorawa shuwagabbani.  akwai masu aikata manyan laifukan da Allah ya haramta, Zina tayi yawa a duniya uwa uba   lud'u da madigo da suka zama gama gari wannan babban masifa ce zata iya janyo mana fushin ubangiji. duk abinda muke aikatawa na rashin gaskiya Allah ya na kallonmu kuma muna cin albarkacin Annabi Muhammad SAW ne da babu albarkasa da tuni Allah ya kifar damu,  saboda haka kayi hakuri dole ranka ya baci kuma duk sharhin da kayi mana babu wanda ya bata mana rai, maganarka gaskiya ce,  kasan da cewa muna alfahari dakai a Najeria da zamu samu jarumai irinka to babu shakka Najeria zata gyaru za'a  samu sauyin rayuwa fiye da yanda muke tunani,  kayi hakuri ka cigaba da bada gudumawarka  mu bamu isa mu biyaka ba, amma ka ajiye a ranka cewa zakaje lahira  ka tarar da aikin alkairin da kayi, Allah ya Ubangiji ya baka lafiya ya kuma kare ka a duk inda zaka shiga, muna rokon Ubangiji Allah ya bamu zaman lafiya da kwanciyar hankali a kasa baki d'aya."

Gabadaya suka amsa da Ameeen ya Allah."

To a takaice dai yini guda abinda ya kasance kenan.

Manya k'asa 'yan kasuwa da manyan 'yan siyasa masu sarauta suna sauka a garin domin dubashi. Sarki Umaru mahaifin matarsa tare da 'yan uwanshi a washe garin ranar suka sauka a garin. kai tsaye babban asibitin suka nufa domin dubashi.

Lokacin da suka isa asibitin yana bacci bayan an gamai masa aikin k'unar jikinsa Asp na kusa dashi a zaune.

Maimartaba tare da mukarrabansa suka samu guri suka zauna cikin alhini da damuwa.

Ganin Takawaran nasa a kwance magashiyan jiki duk a 'kone ya tayar masa da hankali mutu'ka! ya tausaya masa sosai kana yayi masa addua tare da fatan samun sauki da ramgwame.

Har suka shirya tafiya bai tashi ba, Sarkin yace a kyaleshi kada a tashe shi tunda sun dubashi a haka babu matsala.

Har bakin mota Asp ya rakasu yana godiya cikin girma da mutunta juna suka rabu.

Sarkin da kansa ya sanya Magaji ya kira masa Zinat a waya.

Koda suka gaisa sai ya shiga shaida mata abinda yake da akwai.

Kasa hakuri tayi hawayen da take dannewa suka subce tace." Ranka ya dade ya jikin nasa ina fatan ya tashi kun gaisa da juna."?

Yace." Alhamdullhi yaji sauki ki kwantar da hankali ki kuma kiyi masa addua domin adduarki tana da muhimmanci a tare dashi.

Tasa hannu ta share hawayen dake zuba tace." Bana iya bacci kullum addua nake masa Allah ya tashi kafadarsa nace ina san zuwa domin na dubashi Asp ya hana."

Yace." Zinatu kada ki janyowa kanki wata matsalar, kinga kema ba cikakkiyar lafiya gareki ba. ki barwa Allah al'amarin sannan kuma zuwanki bashi zai bashi lafiya ba, watakila akwai abinda yake nufi da hakan dan haka ki samu nutsuwa ki kuma tsananta da yiwa mijinki addua."

A sanyaye tace." To insha Allahu Na gode a gaishe min dasu Mommy. " Yace." Za suji da kyau."

wayar ya kashe zuciyarsa cike da tausayin yarinyar.

Koda ya tashi daga baccin Asp yake sheda masa zuwa surukin nasa  sai duk yaji rashin dadi.

Yace." Me yasa baka tasheni ba  naso mu gaisa na nemi afuwar abubuwan da suka faru.

Yace." Shi da kansa ya hana a tasheka sosai ya dubaka ya kuma jajanta al'amarin, dattijon yayi adduo'i masu muhimmanci a garemu baki daya."

Ajiyar zuciya ya sauke kafin yace." Ranka ya dade wallahi har kunyar na hada ido nake dakai saboda irin abubuwa marasa kyau da suka faru tsakanina da kai  wallahi duk abunda ya faru bana hayyacina don Allah kayi hakuri ka gafarceni."

Murmushi yayi da fadin." Umaru abubuwan da suka faru tsakanina da kai ban daukesu wata tsiya ba, domin dana k'ullace ka  da ba zanzo inda kake har na kula da kai ba, ni kaina sai da na zargin hakan saboda nafi kowa sanin halinka, wasu abubuwan da aikata akwai alamun tambaya a ciki to amma Alhamdullhi tunda ka gane gaskiya kuma dawo nutsuwarka wannan shine farin cikinmu."

Yace." Na gode abokina Allah ya bar abota domin Allah, amma ina zargin wani abu dangane da al'amarin sai dai na kasa yarda da hakan."

Yace." Me kake tunani."?

Ya sauke ajiyar zuciya kafin yace." Idan ban manta ba kwanakin da suka wuce da kaina na sheda maka cewa wata shida na tsayar domin daurin aurena da Hamra'u."

Yace." Eh kwarai kuwa hakane amma nayi mamakin yanda akayi ka sauya shawara akayi abun cikin gaggawa."

Murmushin takaici yayi kafin yace."Iyayen yarinyar basu da kirki sun jefe ni sun juyar min da hankali domin biyan bukatarsu na rasa abinda suke nufi da hakan, ko da ba suyi surkulle a kaina ba ni na amince cewar zan auri 'yarsu to wane irin rashin Imani ne zasu juyar min da tunanina su mayar dani kamar zautacce."

Yace ." Gaskiya basu kyauta ba wallahi ban san me yasa wasu mutanan suka yarda da asiri ba,

to meye amfanin hakan da sukayi tunda gashi tun ba'aje ko'ina ba aikin da sukayi ya lalace."

Ya girgiza kai da fadin." Cikin mafarki da taimakon wani bawan Allah naje na lalata aikin.

Ya dinga kallonsa yana mamakin maganarsa......Murmushi yayi ya bagarar da maganar ta hanyar fadin ." Tunda na warware sosai sai ka kira min matata mu gaisa ko hankalinta ya kwanta."

Yace." Kasan kuwa ta dameni kullum sai ta kira waya yafi sau biyar har kuka takeyi.

Tsigar jikinsa ta tashi, ido ya lumshe da fadin." Nima kukan zucci nake tsayin wata da wasu kwanakin ban sata a idona ba mun rabu babu jituwa wallahi hankalina gabadaya yana kanta.

Asp din yana laluben number yace." Kamar ita kadai ka ajiye a gidan ko ka manta su biyu ne ga Uwale ma babbar uwar gida."

Murmushi yayi bai iya cewa komai ba, hannu ya mika masa domin ya bashi wayar.

Yasa wayar a kunnanshi yayi dai-dai da maganarta......"Assalamu alaikum."

Idonsa ya lumshe wani irin yanayi na ziyartashi.

Gyaran murya yayi a nutse yace." Wa'alaikissalam Sirrina marufar asiri na."

Jin muryarsa a kunnanta ya sanya ta sauke sanyayyar ajiyar zuciya a hankali tace." Alhamdullihi jin muryarka a yanzu ya tabbatar min da cewa sauki ya samu a gareka ina rokon Allah ya baka lafiya tare da sauran wa'inda suke kwance."

Ya amsa da "Ameen ya rabbi ya kike ya babyna dake tare dake."?

Hannu ta dora saman cikin da yayi wani irin girma tace." Babynka yana kewarka shima kullum sai yayi kukan rashinka a kusa dashi."

Yace." Ki bashi hakuri kinji ko insha Allah ina nan zuwa gare ku baki d'aya sannan ina neman afuwarki akan abubuwan da suka faru a baya.

Tayi dan murmushi da fadin." Na yafe maka nima ka yafe min."

Yace." Baki min komai ba my love ni ne mai laifi a gurinki amma naji dadi da ki kayi min afuwa

zan dawo mu cigaba da rayuwa mai kyau."

Tace." Allah ya yafe mana baki daya.

Ya amsa da Ameen kafin yace." Ina Uwale ki bata wayar mu gaisa."

Tace." Gata a kusa dani tare da Hamra'u."

Shuru yayi bece komai ba .

Ta mikawa Uwale wayar  suka gaisa sosai tana jajanta masa.

Yace." Uwale ku kwantar da hankalinku na samu lafiya insha Allan zan dawo da kafafuna.

Tace." To Alhamdulillhi Allah ne abin godiya mutanan *Kafur!* ma duk sun ce ayi maka sannu da jiki sai ka dawo gida zasu zo dubaka."

Yace." Na gode sosai Allah ya saka da alkairi."

Wayar ta mikawa Zinat din fuskarta yawalce da fara'a da jin dadin samuwar lafiyar jikinta nata.

Ta mikawa Hamra'u wayar dake zaune tayi jugum!

A sanyaye tace." Yaya na sannu ya jikin."?

Babu yabo babu fallasa ya amsa, iyayen yarinyar sun janyo mata tsana a gurinsa.

Daga haka babu wata kalma mai dadi kawai ya kashe wayarsa.

Idonta ya ciko da ruwan hawaye! tana so itama ya dinga gwada mata soyayya koda bata kai irin wacce yake gwadawa Zinat din ba.

A sanyaye ta mika mata wayar jikinta babu kwari ta tashi ta shige daki ta kwanta abin duniya ya isheta.

Zinat da Uwale kuwa yinin walwala da farin ciki sukayi sakamakon amsa adduarsu da Ubangiji yayi babu shakka Allah maji rokon bawansa ne.

To bahaushe yace ." Rana dubu ta 'barawo rana guda ta me kaya.

*UBAN DABA!* ya samu nasarar shiga asibitin cikin shigar Dr Shu'aib likitan dake tsaye a kan Umar din!

Yayi basaja sosai da yake Dr Shu'aib din gajere ne mai 'kiba shiyasa babu wanda yayi tunanin cewa bashi bane, abinka da dare duk da akwai fitilu a asibitin hakan bai sa an ganeshi ba,kai tsaye ya nufi d'akin da Umar din yake kwance!

A hankali ya mayar da kofar ya rufe.....Asp dake kwance a can saman kujera ya bude idonsa sakamon jin motsin a dakin
Dama can bashi da nauyin bacci.

Ganinshi yasa ya koma ya kwanta dan beyi tunanin cewa wani ne daban ba. baccin ya sake fizgarsa.

Da har ya tsorata amma ganin ya koma ya kwanta yasa ya sauke ajiyar zuciya.

Kai tsaye gadon da yake kwance ya nufa.

Isarsa ke da wuya ya b'ude idonsa!!

'Kwayar idonsa kawai ya kalla ya sheda waye a gabansa.

A zabure! yayi nufin tashi.......shi kuma da gaggawa ya rike masa wuya da kyau!!

Wata shegiyar igiya mai wasu k'ananun kososhi masu tsini! ya ciro daga can kasan aljihun wandon dake jikinsa.

Kokarin d'aure masa wuya yake da igiyar abun ya gagara! domin dambe! suke sosai! duk da ya sha'ke masa wuya! amma bai samu nasara a kansa ba.

Naushi! ya kaiwa hancinsa a take ya fashe ya fara zubar da jini. ya sake kawai fuskarka wawan naushi! yayi tagaga! zai fadi! amma saboda taurin zuciya bai sakar masa wuya ba.

Gurnani! ya dinga yi yana buge-buge! da kyar yake janyo numfashi! ya galabaita sosai! saboda dama can jikin babu 'kwari!

Kamar a mafarki ya dinga jin wani irin abu.

Ya bude ido da saurin gaske.

Abinda ya gani ya tayar masa da hankali shin mai yake faruwa a tsakaninsu.

Da sauri ya nufi gurin  da fadin." Dr me yake faruwa ne."n

Juyowar da zai yi suka had'a ido! nan ya sheda ko waye! jikinsa ya shiga tsuma!  ya zabura! zai fita. kawai ya d'aga igiyar dake hannunsa ya kai masa duka da ita a fuska! aikam duk ta yanke masa fuskarsa har kan idonsa ya rufe! idon jini ya 'bata fuska........Da kyau! yayi ihu!! da fadin." Babu lafiya a daki mai lamba 21."

Kafin kice me hankalin kowa ya tashi duk likitocin dake aikin kwana suka fito tare da masu gadi.

Kai tsaye d'akin suka nufa.....Lokacin ana buga damben Maza!  tsakanin mutum biyu. Asp na kasa a kwance yana matagugu! rai a hannun Allah.

Sosai suke dambe!! irin na k'wanji  da 'kwanji *UBAN DABA!*  hannu guda gareshi amma ya san makwantan mugunta!

Shi  kuma da yake da rauni a jikinsa hakan bai sanya yayi rauni ba, ganin Asp a kwance! ya tayar masa da hankali  babu shakka yau sai yaga karshen mutumin nan mutu'kar yayi sanadin abokinsa.

Ganin abinda yake faruwa ya tayar musu da hankali.

Duk yawansu aka rasa wanda ya iya zuwa gurin domin bada taimakonsa.

Su kansu sucurity din abun yafi 'karfinsu!

Gabadaya ya manta da wanda yake gogayya! shine fa mutumin nan da wu'ka! bata aiki a kansa!  amma ya dage yana wahalar da kansa sai  kai masa sara da kaifaffar wukar dake hannunsa burinsa kawai ya illatashi.

Ganin haka yasa yayi kwankwance ya murd'e! masa hannu ya kwace wu'kar!

Bai kuma jirayi komai ba ya soka masa ita wuyansa!!

A take ya fadi a gurin yana wani irin gurnani! jini ya dinga tsartuwa!

Zubewa a kusa dashi da  wu'kar a hannunsa da karfi yace  *." Ashahadu  Allah ila ha'illalahu -wa ashshahadu Anna Muhammadur-rasulullah.* fad'ar hakan keda wuya ya mi'ke cikin zafin nama yaje ya fizgo k'aramar bindigar dake jikin rigar Asp dake rataye bai jira komai ba ya sai ta a wuyansa.

*Kada ki karanta min littafi ba tare da kin biya ba, kada ki saya ki fitar dashi, 'yar uwa kada kiyi sharing,  idan kina bukatar biyan kudin littafin #500 ne......0542382124....Binta umar gtbabk....Idan kati zaki turo sai kiyi min mgn ta WhatsApp da wannan number*
*07084653262*
*BINTA UMAR ABBALE*